# HASKE
# MAGANIN DUHU



HAUWA'U ABUBAKAR LAWAL
(Mai Turare)

# HASKE MAGANIN DUHU

NA

HAUWA GANDHI LAWAN
MAITURAREN KAMSHI
(Mrs. Yusuf Garba Mustapha)
08090664904 0r 07029324870

Hakkin Mallaka: Hauwa Gandli Lawan Mai Turaren Kamshi.

Copy right(C): Hauwa Gandli Lawan Mai Turaren Kamshi.

## GODIYA

Ga Allahu Rabus Samawati, wal ardihi, Rabbi Musa wa Haruna, Allah ba zan butulce maka ba. Ina godiya da tarin ni'imomin da kai mini. Allah ka sanya ni daga cikin masu ibada da godiya, amin. Alhamdulillah. Salati ga Muftahu Rahma, Nurizzatiyyi, Sayyadil Wujudi, Katimun Nabiyina wallmursali Sayyadina Habibuna, Muhd Rasulillah (S.A.W.) shi da iyalansa da duk masu sonsa suke bin tafarkinsa amin Madallah da Ubangijin haske da duhu.

## TUKUICI

Ga malaman da suka fara karantar da ni, har zuwa yau, Allah ya kai haske ƙaburburansu. Amin.

## INA GODIYA

Ga duk wani mai sona, a duniya tun daga samuwa ta har zuwa yau, ta dalilin hasken karatu, ko kuma wani dalilin na daban. Yaushe zan butulce? Kai *I love you so much* eh? Musamman Fatima Aliyu Isa (Zahra).

## SADAUKARWA

Wannan littafi na sadaukar da duk ladan da Allah zai ba ni ta hanyarshi ga Ruhin SANI LAWAN MAITURARE (Young Doctor) yaron da danginsa suka sa buri da shi, ba ga mu ba, gwamnati ma ta yi jajen rashinsa, domin ta yi alfahari da shi kwarai, tun da sau biyu yana wakiltarta a ƙasar India, da Rasha, kan harkar lafiya. Ya mutu ne a daidai lokacin da yake ƙaƙutukar neman ilimi. Ashe ƙaunar shi, ajalinsa a cikinsa ne. Ina mana ta'aziyyar mutuwar Malam, tare da ɗimbin abokanka, domin duk ran da suka tunaka sai sun yi jimami, irin mutanen da a cikin miliyan ake fidda ɗaya. Duk cikin dangi an shaida ba kamar Malam, sani yana da shekara goma sha biyu ya sauke alkur'ani,

sha biyar ya haddace ya kuma rubuta shi da hannunsa. Mutum ne mai matukar nutsuwa da tawali'u. Karami, amma babba ne a cikin yara, tun yana raye ake cewa wannan tamkar waliyi yake, ashe hoto ne kawai aka ba mu na shi, ya yi mana wata irin rayuwa mai cike da alfanu da izna mai yawa. Allah ya jikan Sani Lawan Maiturare (Malam), don Allah ina rokon kulhuwallahu ko kafa daya ce ga wanda ya karanta shahin nan zuwa ga ruhin Malam Sani. Ya rasu yana da shekara ashirinn da uku, ban taba ganin mai basira irin shi ba. Malaman shi ma shakkar sa suke yi, ashe an bude komai ne na dan lokaci. Allah mun gode maka da ka ba mu shi ka karbi abin ka. Mota ce ta yi ajalinsa, tun daga inda a kai hadari a kai nisan tafiya zuwa asibiti, don ceton ranshi, cikin nutsuwar shi yana karanta Al'kurani dab da za a kai shi asibitin rayuwar ta kare. Ya bar Ummanshi da jimami, Allah ya jikanka da Rahamarsa. Amin.

## INA SON KU

Rahma Idrisu
Aminar Dambatta (Yarinya, Maman Sani)
Mariyata Sada ('Yar Mutan Katsina)
Halimata B.H. (Sharri Kayan Kwalba)
Fauziyyar *Q for Q* (Auren Kudi)

Allah ya barni da ku, da kune nake ganin nasarar rubutuna, Na gode.

## ALBARKARMU TARE

**Ga kawata Kubran Namarwa, tare da iyalanta. Ina godiya fa, yaushe zan butulce?**

## ALLAH YA AMFANA

**Auren Shatu na Aishatu Garba ~~Mustapha~~ (Giwargo Aisha) tare da Angonta Ibrahim. Allah ya bada zuriya dayyiba. WEL COME TO THE WORLD Mustapha Aminu Garba Mustapha. Allah ya raya mana kai da albarka, ya bawa babanka nauyin daukar hidimarku. Ya bawa Mamanka lafiya: Anti Fauziyya Yahya Kura Muhd.**

# HASKE MAGANIN DUHU

Gudu ne take yi, irin gudun da ya yi kama da gudun ceton rai. Gudun daga ka ga mai yinsa, muhimmin lamari ne ya koru shi, domin babu ruwanta da duban inda take ajewa da ɗauke ƙafa. Neman h aske kawai take, don fita daga duhun da ta baro.

Lokaci ɗaya, wani irin duhu ya ziyarci ƙwaƙwalwarta, cikin daƙiƙu da su kai kama da na ƙiftawar ido sassan jikinta ya amsa, ba tare da bin shawarar zuciyarta ba. dole jikin ya bi umarnin ƙwaƙwalwarta. Lokaci ɗaya haske ya ɗauke mata, ta yi warwasa a doran ƙasa, komai na jikinta ya yi laushi luɓus. Mutuwa ce suma ne?

Barista Muttaƙa, da ya fito daga kwanar makarantar Musa Iliyasu, akan idonshi yana ƙoƙarin fitowa ya ga gilamwarta a guje, har sanda ya ƙarasa fitowa titin sosai. yana hangen ta a gujen gudu take yi kamar walƙiya. Har abin ya ɗan taɓa zuciyarsa. Ta *mirrow* ɗinshi sai da ya waiwaya baya don ya yi tsegumin shin wannan yarinyar ita da wa? Bai hango kowa ba, bai ga kowa ba, wanda yake da alaƙa da gudun nata, baya ga ɗaiɗaikun jama'ar da ke yawa a titin sabuwar Jami'ar suna sabgoginsu. Ya hau titin sosai. amma yana tagaba da ganinta, lokaci guda ya ga ta yi faɗuwar bazata a gefen hanya warwas.

Lokacin ne zuciyarshi ta ba shi shawarar yin wani abu. Cikin *low speed* ya gangara gefen hanyar inda take kwance a mace, ya fito da hanzarinshi ya isa kanta Gabanshi ya yi wata irin faɗuwa lokacin da ya haɗa ido da jemammiyar fuskarta. da sassan jikinta kwance sun bi ƙasa.

"Ya Allahu." Shi ya ambata ya kawo masa ɗauki. Ya

duba gabas da yamma, kudu da arewa ko zai ga mai kawo agaji. Kowa ta kanshi yake, motacin da ke titin wuccewarsu su ɗin kawai suke. Ya yi A'uziyya don kariya. Sannan ya koma ya buɗe motar ya ciccibeta ya sakata a ciki. Cikin hanzari ya tashi motar. A asibitin Saudat da ke nan Rijiyar Zakin ya mika ta gun taimakon gaggawa (Emergency), likito da nos-nos suke masu kyakkyawar maraba ta hanyar ba su duk wata kulawa da ta dace. An bata gado, an sa mata *drip*, amma har lokacin ba ta dawo ba. Sai ranta da ke kaiwa yana kawowa.

Barista Habib ya ƙura mata ido, don nazarta wasu yanayi da ya ganta a ciki. Na farko ya karanci akwai alamar matuƙar galabaita da jemewa a jikinta wanda ya assasa fitowar idanunta waje ƙuru-ƙuru. Sannan kalar fatarta da gani ta ɗara wacce take a yanzun hasawa, a gefen fuskarta akwai tambari na mari da yakushi. Sannan gashin kanta aske yake ƙwal-ƙwal. Lallai nan gurin akwai bayani.

Yarinya ce da a tsinkaye da ƙyar ta haura sha tara. Sannan mai matsakaicin tsayi. "Yar jika-jika mai kyan sura. Duk daga inda ta fito ba daga daula ba ne, daga wahala ne. Wai me ya koro kwaɗo daga ruwa zai faɗa wuta?

Dogon likita kakkaura baƙi, ya ɗan doki bayan Barista ya ce, "*Take easy man,* insha Allah za ta farko *normal.* Wuya ce dai ta sha matsanancia, insha Allah nan da goman dare za ta dawo hayyacinta, mun ba ta magunguna masu ƙarfi da za su taimake ta samun haka." Suka kalli agogon a tare, su kai ɗan murmushi. Ya ce, "Na gode likita. To zan iya barinta kenan in je kawo mata kayan buƙatu? Na san zan iya dawowa kafin ƙarfe goman."

"*Yes man you can go,* ba wani abu za mu ba ta duk kulawar da ta dace." Likitan ya faɗa.

"Na gode kwarai, Allah ya biya." L. .n ya yi murmushi, ya juya ya fita ya turo *nurse* biyu don su kula da ita, kafi mai ita ya dawo.

Ya fito daga asibitin cikin godiyar Allah, da raunin jiki. Zuciyarshi cike take fam da wasiwasi iri-iri, to yanzu ya zai yi? Gidansu kawai zai wuce ya gayawa Hajiya ab.. da ke faru..a, kuma shiru kawai zai yi shi din ya ci gaba .a kujiba-kujibarsa har yannyar dai ta dawo hayyacinta .. sada ta da iyayenta? Abin da ya sani Hajiyarsa macce .. ba ta son kwashe-kwashe, yanzun yana gaya mata bal.. .le shi da fadanta za ta yi, ta ringa shiga tana fita kullum ita abin da take cewa, "Shegen karambani ne da dan adam haka kawai Allah ya bar bawanshi a rana kai kuma da rawar kai sai ka kinkimo shi ka ..aido shi inuwa. To yayin da ya tsane kai ne lamba wan da zai jawo ya danna ka wuta, don haka jama'a su yi hattara, jama'ar yau wuyar sha'ani gare su."

To ko kuma gidan Yaya Zainab zai je ya fayyace mata komai? Itama din dai bari ya ja akwai sauran lokacin shaida mata. A cikin motarshi duk yake wannan tunane-tunane, har zuwa inda ya yi *parking* a kofar gidan iyayenshi cikin kofar Nassarawa, inda yake tare da mahaifiyarshi a cikin *apartment* din mahaifinshi da ya mutu ba bari shi ya gyara yake za.. .. a cikinsa. Ya shiga ciki, ya yi wanka, hadi da alwalai sallar Magriba. Sannan ya fada cikin gidansu gurin Hajiyarsa. Ya taradda ita tana addu'a kai tsaye ya wuce cikin kicin yana bude-bude. Cikinsa sai guda yake yi don azab.. yunwa.

Ya yi masifa'far. ..aki da ya yi karo da ame da cot ya dahu ya yi dindim a cikin flask. Ya yi saurin rufewa lokacin da turirinsa ya yi masa oyoyo. Ya bude womar

miyar lafiyayyar miyar kuɓewa busassa ya sa cokali ya tuno zuƙa-zuƙan nama ne na saniya, sai a kansu ya wuce ya ɗau tsokoki uku masu lafiya ya danna a baki. Yanda su kai masa daɗi a rai, ya so a ce dai abin da zai gamsarshi ne ya samu. Amma yanda ya kwaso yar taballan nan haka sakin ya lafci baƙin tuwon nan, ai sai ya yi masa illa a hanji. (Ku ji ni da Barista yana kushe gargajiyar Bahaushe, ai ko ba za a raina ta ba).

Ya koma falon gun hajiyarsa tana shafa addu'a ta ce, "Muttaƙa an dawo?" Ya durƙusa a gabanta ya ce, 'Wallahi Hajiya Allah ya nufa. Ya wunin yau?"

"Komai lafiya."

"Ya wurin aikin naka, yau kam dai ka ɗan yi nutso da yawa, ina jin tun wayewar garin sai yanzun na ganka." Ya yi gajeran murmushi.

"Hajiya neman ne ya jawo tsayin lokacin, kuma Hajiya tun ɗan shayin da na kurɓa da safe ba komai a cikina yunwa nake ji sosai." Tana murmushi.

"Ai akwai lafiyayyens tuwan dawa, miyar busassar kuɓewa, hadda man shanu a ɗakin girki." Tana ta dariya, don dai ta san ba a take yi ita ma, ta san dai Muttaƙa ba ma'abocin tuwo ba ne, tun yana yaronsa. Ya miƙe tsaye ya ce, "Na tafi neman abinci Hajiya."

'Allah ya kiyaye hanya, ai dai ga irinta nan, ni ko saboda kai-kai ɗaya ba zan fasa girkin tuwona ba, ko kuma bayan na yi girkin, ka sani girka ma wani ba, da dai su Maryam na kusa ne. To wannan daiin da ni ce kai, wannan wulaƙancin duk da ake mini da yanzun na nemawa kaina mafita, in yo dalleien aurena, shi kenan bakina alaikum, abin da duk nake so shi zan bada umarnin a girka, amma ina daɗin raɓe-raɓe?"

Bai ce komai ba, ya kaɗa kanshi ya ƙara gaba. Inda sabo ya saba mitar Hajiya a kan aure. Ta kan manta komai ɗin da yake yi lokaci ne, Allah na kawo lokacin auren shi kenan sai ya yi, amma shi ɗin wurin shi bai wani fiye damuwa ba. Hidimomin gabanshi su ne mafi rinjayen abubuwa da yafi maida hankali a kan su.

Ya fito ƙofar gida ya yi tsaye jim da tunanin ina ne ma zai nemi abinci ko kuma shayi zai sha? Kai ina shayi ɗin ai ba abinci ba ne. Mutum tun da Rabbi ya hudu rana a ce bai ci komai ba sai ruwa? Kai *can't be possible.* Irin wannan lokacin bai fiye son shiga gidajen 'yan'uwansa ba, saboda dai lokaci ne da ko wane maigidanci yake zaune yana hutawa cikin iyalinsa. Dole uwar naƙi tasa ya dannan gidan yayansa na biyu.

Ya tarad a tsakar gidan an shimfiɗa ƙatuwar tabarma, yayansa da 'ya'yansa guda huɗu suna zaune suna cin abinci da yin hira.

Ya yi sallama yaran da yayan nasa suka amsa, ya ƙaraso gurinshi suna gaisawa da tambayar ya aiki, sannan ya yi masa Bismillah. Ya kalli kwanon da ya kusa cinyewa yay ce, 'A'a yaya ƙarasa kayanka kawai, ni ɗin ai babbar yunwa nake ji ba wai ƙarama ba. Ina matar ne ta zo ta sallame ni?" Kafin yayan ya bashi amsa ya ɗaga murya yana mata kwakwazo. Ta fito cikin kwalliyarta tana ƙamshi mai sanyin daɗi. Ya hararєta da cewa, "Sai ki wani shige ɗaki kina ta ɓatan lokaci, wa ya gaya miki anawa maigida haka, ai shi maigida da wuri ake sallamarshi da abin da zai kare cikinsa, tun da shi ne mai nemowa, wanda ko ke nemowa ba a gyara mai wata ran idan ya fita sai an bi sahu don nemo shi."

Ta ja kujera 'yar tsugunno ta zauna ta ce, "Haka ne

miyar lafiyayyar miyar kuɓewa busassa ya sa cokali ya tuno zuƙa-zuƙan nama ne na saniya, sai a kansu ya wuce ya ɗau tsokoki uku masu lafiya ya danna a baki. Yanda su kai masa daɗi a rai, ya so a ce dai abin da zai gamsarshi ne ya samu. Amma yanda ya kwaso yar taballan nan haka sakin ya lafci baƙin tuwon nan, ai sai ya yi masa illa a hanji. (Ku ji ni da Barista yana kushe gargajiyar Bahaushe, ai ko ba za a raina ta ba).

Ya koma falon gun hajiyarsa tana shafa addu'a ta ce, "Muttaƙa an dawo?" Ya durƙusa a gabanta ya ce, "Wallahi Hajiya Allah ya nufa. Ya wunin yau?"

"Komai lafiya."

"Ya wurin aikin naka, yau kam dai ka ɗan yi nutso da yawa, ina jin tun wayewar garin sai yanzun na ganka." Ya yi gajeran murmushi.

"Hajiya neman ne ya jawo tsayin lokacin, kuma Hajiya tun ɗan shayin da na kurɓa da safe ba komai a cikina yunwa nake ji sosai." Tana murmushi.

"Ai akwai lafiyayyens tuwan dawa, miyar busassar kuɓewa, hadda man shanu a ɗakin girki." Tana ta dariya, don dai ta san ba a take yi ita ma, ta san dai Muttaƙa ba ma'abocin tuwo ba ne, tun yana yaronsa. Ya miƙe tsaye ya ce, "Na tafi neman abinci Hajiya."

'Allah ya kiyaye hanya, ai dai ga irinta nan, ni ko saboda kai-kai ɗaya ba zan fasa girkin tuwona ba, ko kuma bayan na yi girkin, ka sani girka ma wani ba, da dai su Maryam na kusa ne. To wannan daiin da ni ce kai, wannan wulaƙancin duk da ake mini da yanzun na nemawa kaina mafita, in yo dallelen aurena, shi kenan bakina alaikum, abin da duk nake so shi zan bada umarnin a girka, amma ina dadin raɓe-raɓe?"

Bai ce komai ba, ya kaɗa kanshi ya ƙara gaba. Inda sabo ya saba mitar Hajiya a kan aure. Ta kan manta komai ɗin da yake yi lokaci ne, Allah na kawo lokacin auren shi kenan sai ya yi, amma shi ɗin wurin shi bai wani fiye damuwa ba. Hidimomin gabanshi su ne mafi rinjayen abubuwa da yafi maida hankali a kan su.

Ya fito ƙofar gida ya yi tsaye jim da tunanin ina ne ma zai nemi abinci ko kuma shayi zai sha? Kai ina shayi ɗin ai ba abinci ba ne. Mutum tun da Rabbi ya hudu rana a ce bai ci komai ba sai ruwa? Kai *can't be possible.* Irin wannan lokacin bai fiye son shiga gidajen 'yan'uwansa ba, saboda dai lokaci ne da ko wane maigidanci yake zaune yana hutawa cikin iyalinsa. Dole uwar naƙi tasa ya dannan gidan yayansa na biyu.

Ya tarad a tsakar gidan an shimfiɗa ƙatuwar tabarma, yayansa da 'ya'yansa guda huɗu suna zaune suna cin abinci da yin hira.

Ya yi sallama yaran da yayan nasa suka amsa, ya ƙaraso gurinshi suna gaisawa da tambayar ya aiki, sannan ya yi masa Bismillah. Ya kalli kwanon da ya kusa cinyewa yay ce, 'A'a yaya ƙarasa kayanka kawai, ni ɗin ai babbar yunwa nake ji ba wai ƙarama ba. Ina matar ne ta zo ta sallame ni?" Kafin yayan ya bashi amsa ya ɗaga murya yana mata kwakwazo. Ta fito cikin kwalliyarta tana ƙamshi mai sanyin daɗi. Ya harareta da cewa, "Sai ki wani shige ɗaki kina ta ɓatan lokaci, wa ya gaya miki anawa maigida haka, ai shi maigida da wuri ake sallamarshi ɗa abin da zai kare cikinsa, tun da shi ne mai nemowa, wanda ko ke nemowa ba a gyara mai wata ran idan ya fita sai an bi sahu don nemo shi."

Ta ja kujera 'yar tsugunno ta zauna ta ce, "Haka ne

kam, ai ka gani da idonka inda nake ƙoƙarina ko? Ba na bar ma ɗan'uwanka da yunwa bare kuma sanyin idanunka."

"Ban san wasa fa Hauwa ke ɗin sana'ar da kika iya kenan har tirenin ɗin wasu kike yi, ni tashi ki ba ni abinci wane maigida ne kuma kike magana bayan ni, gashi nan kina ta sakaci *ulcer* ta kusa cafke ni, idan na shuri ƙasa na ga wanda za a bari da takaba. Tun safe kin bar hanjina sai buɗe-buɗe suke." Ta yi dariya mai isarta ta ce, "Haiya ratata, dariyar mai mata uku, kanka ake ji wai mahaukaci ya faɗa ruwa, ya ce wankana nake yi. Ni ɗin ai na san kai ba ganinka ake yi ba, sai ranar da cikinka ke zikiri ka lalubi na Hajiya ka ji ba kanta, sai ka fara bin gidajen, tamkar dillaliya uwar gulma. In dan Aljannar gurinka ne ka ke mini wannan isar take kayarka ba sai ka ɗage ƙafar ba, bare na samu na shige. Na gode da takan, abincin kuma dai ba ka ɗanar za ka zo ba, bare a sa sanwa da kai, sai abi wani sarkin, amma dai ba Ado ba."

Ya kwantar da kai, "*Please* uwargida, daga ke fa ko kallon wata ba zan kuma ba, bare na yi ƙari, tashi za ki ki ɗan lalubo ko naki ne, ke ɗin ai waliyya ce, abincin ba damunki ya yi ba." Ta ja tsaki.

"Ni da amaryar ka ƙaramin dana huta da ganinka kana mini shishshigi a tukunya."

Ya ce, "*Please* manta da'allah ki yi wani abu man." Ya juya yana kallon wan.

"Yaya sa mini baki mana matar nan fa so take ta karta mini."

Yayan da ya yi burus a gurin bai ko sa musu baki ba, yana dai ta cin abincinsa ne yana kallon shirmensu, shi da 'ya'yansa. Ya ture filet ɗin abincinsa ya miƙe ya ce, "A'a ni me ye nawa a ciki tsakaninku, ami nemowa da mai girkawa

sai ku sasanta." Ya yi shigewarsa falonsu. Ya bishi da kallo galala, sai da ya ƙule ya dawo da kallonshi gare ta ya sassauta murya yana ban baki, sannan ta tashi ta shaƙo masa filet da dambun shimkafa mai kyau. Nan ya lalace yana ci yana santi, yana kuma ba ta labarin abin takaicin wai da Hajiya ta yi baƙin tuwo (Gardi da gyale). Ta yi dariya ta ce, "Ni kam kana ba ni mamaki matarka kam ta banu idan ita ɗin mai son tuwo ce, ce nake yi tuwo ba abin marmari ba ne? Ni kam idan na yi kwana biyu ni dai maigidana ba mu ci ba duk ran da na yi za ka so ka ga garar da za mu kwasa muna santi, sai dai yaranka ma kai suka biyo, da na ce tuwo an ringa zumɓure-zumɓure kenan, haka za su ringa can kulati-kulati. Don shi Nuraddin ma, idan ya ga tuwo kuka yake yi ya ce ba shi ba shi ba a bashi abinci."

Ya ce, 'A'a Madam da gaskiyarsu ki ringa girka musu kawai abin da suke so, tun da dai na kawo komai na aje a wadace a gida." "Haka ne sai dai ka manta ba ka kawo maigirki ba ka aje, ni ɗin ai ba zan iya wannan ba, yanda dai Hajiya take yi nima haka hake mai ci ya ci, mara ci ya bar shi, idan yana da abin da ci ya ci, idan babu a sha ruwa a ja lahaula."

"Ke an gaya miki yunwa na jin lahaula ne? Ai da a baki rubutu gara kwaɗon rogo."

Yara na gefe, suka ƙyalƙyale da dariya, shi ma ya taya su ya ce, "Allah ko, ku dai ku yi haƙuri, ku kuma sha kuruminku da zarar na kawo sabuwar Anti ai cin tuwan dare ya ƙare shi yake lalata hanji, kuma ganin arnen nan ya haɗe rai sai ku zuro a guje gurinta za ta ba ku abinci mai daɗi ku ci." Yara suka fara eh suna murna. Nuraddin ma cewa ya yi shi ɗin can zai koma da zama. Ya bubbuga bayansa kai dai kawai ka yi addu'a Allah ya kawo ta gari.

Ya turc kwanon ya cc, "Madam godiya sakallah, kin fita ko ba sabulu, ƙofar Jannatin nan yanzu *you are free to enter*, ai kin yi abin da Allah ke so. Bari ki ga na tashi na koma asibitin ko, 'yar mutane ta farko?"

Ta ce, 'Wa ke nan?"

Nan ya labarta mata labarin komai, ta yi saƙale tana jajantawa ta ce, 'Barista to haka za ka tafi ba ɗan wani abu da ko za ta ci, idan ta farkan?"

"Ai ina jin dai a asibitin ma suna bada abinci kin san *private* ne."

"Duk da haka a ɗan riƙa mata wani abun, ka san dai ai ba ko wane *private* ba ne suke ba da abincin, kuma ko suna badawa mutum kan buƙaci wani abu daga waje."

"Haka ne, to me za ki ba mu?"

"Ka ga a zuba mata dambun shinkafar nan abun marmari ne, ƙila ta so; kuma ina da wani sauran feffsuf zan haɗa mata." Ya yi zugum a ransa da tunanin ya ya marar lafiya zai wani so Dambu? To amma kar ya watsa mata ƙasa a ido, dole ya amsa yana ta godiya, ya saka kayan a bayin motarshi. Sannan ya koma gida ya canza kaya ya sa jallabiya mai dogon wando da gajeran hannu. Ya yi ma Hajiya sallama zai je ya dawo, ta ce, "Cin abincin ne dai ya yi nisa haka, duka a lungun ba abincin?" Yana sosa ƙeya yana dariya ya ce, "Haba dai Hajiya an samu gidan Kuluwa, kin san ita ba ta ƙaranta, ba kamar su o'o ba da abinci baki da baki don kar irinmu su samu."

"Maganinka kenan, mai kwaɗayi mai bin gidaje, in da kana da taka shekar mai zai dame ka, ba sai yanda ka yi ba?" Ya gyaɗa kai, alamar amincewa, ya fito.

Daidai lokacin da ya danna kan shi ɗakin, a daidai lokacin rayuwar yarinyar ta dawo. An kuma yi sa'a shi da

likitan suka shigo tare misalin tara da arba'in da biyar, ta raba idanu kan kowa. Lokaci ɗaya me ta tuno oho, kawai sai ta yi wani masifaffan yunƙuri ta duro daga gadon igiyar ƙarin ruwan ta biyo ta. Likita da Barista suka kawo agaji da hanzari suka cukuikuyeta. Faɗi take "Don girman Allah ku ƙyale ni, ku rabu da ni, kar ku cutar da ni, ba abin da na yi muku. In kun ƙyale ni ba zan gayawa kowa ba, na yi muku alƙawari."

Likita faɗi yake, *"Take easy baby,* mu nan da kika gani ba macuta ba ne, rayuwarki muke ƙoƙarin cetowa, daga hannun da kika faɗa, kin ga ni nan likita ne, wannan kuma shi ya kawo ki, ki nutsu." Ta kalli barista a zabure, sai raba ido take kamar na tsohuwar maiya.

Da ƙyar dai suka lallaɓa ta ta zauna, amma sai kallo take, duk wani motsi sai ta zabura. Tana wannan fisge-fisgen ƙarfin maganin da aka ɗora mata da allura su ka kuma dada rinjayar jininta barcin dai ya kuma ɗebe ta.

Su kau ajiyar zuciya likita da barista hadi da murmushin yaƙe. Doctor ya ce, 'Insha Allah *she will soon be rocover.* Ta fuskanci wuya ne ba 'yar kaɗan ba, kuma akwai tsoro mai yawa a tare da ita." Ya nemmi guri ya zauna lokaci mai tsayi yana ta tunane-tunane masu yawa, har shima ɗin barci ya fara cin ƙarfinsa an yi sa'a a ɗakin su kaɗai ne, sai ya koma wani gado nesa da ita ya kishingiɗa, kafi wani lokaci barci shi ma mai nauyi ya ɗauke shi, dama a gajiye yake don ranar ya sha hidima da zurga-zurga.

Misalin ƙarfe uku na sulusin dare kamar an ce ya farka ya buɗe ido, gabanshi ya yi wani irin faɗuwa, don ganin da ya yi yarinyar zaune a kan gado ta tsura masa dakwa-dakwan idonta, jajur da barcin gajiya suka rina, tana kuma ƙoƙarin cire filastar ƙarin ruwanta.

Bai san sanda ya ce, "Subhanallah ba." Ya miƙe da hanzari. Ita ɗin ba ta dainan kallon shi ba, ba ta kuma yi wani yunƙurin gudu ba, har ya iso gabanta ya zauna a gefe ya ce, "Kin tashin?" Ta gyaɗa kai.

"Kina buƙatar wani abin kamar abinci ko ruwan shayi, ko kuma buƙatar banɗaki?" Da sauri ta gyaɗa kai, shi ma da saurin ya haɗa mata shayi cikin kofi yana fifita mata, da ya yi sarau-sarau ya miƙa mata. Kafin ya ce me, ta miƙo masa kofin shan ruwa ta yi masa. Ya kalleta da mamaki ya ce, "A miƙo abinci?" Ta gyaɗa masa kai da hanzari ya miƙo mata dambun shinkafar, yanda take cin abincin sai abin ya bashi tausayi, da gani kwancen yunwa ce. Ta share shi tas tana suɗe hannu kamar bai isheta ba, ya ɓalle ledar *pure water* ta zuƙe ya ƙara wata ta sha rabi ta aje rabi. Ta koma gefe sai zufa mai yawa take yi, tana muzurai. Ya miƙe ya ƙaro yawan iskar fankar, yana ta kallonta yana mata sannu ya ce, "Bari a kira likita." Ba ta tanka ba, ya miƙe ya fito, ko kan su zo da likitan barcin ya kuma kwashe ta. Sai kallon ta kawai suka tsaya yi, shi barista na ma likita bayanin abin da ya faru, ya ce a ƙyaleta kawai mu jira dai ta dawo hayyacinta sosai. Shi kam barista bai samu damar komawa barci ba, sai alwala da ya yi, ya yi ta jera sallah har a kai Asubahi yana wazifarshi, barci ya sunkuce shi.

Wurin takwas ya farka, ga mamakin sa kuma a gefe ya ganta rakuɓe da alamar sallah ɗin ita ma ta yi. Yana murmushi ya kalleta ta yi saurin gaishe shi, ya ce, 'An tashi lafiya, ya jikin naki ki ke ji yanzun?"

"Lafiya lau sosai ni ɗin ai lafiya ta lau ban san kuma me ya same ni ba."

"To mun godewa Allah, bari na yi wa likita magana

sai ya duba ki, in ya amince sai kawai mu wuce na kai ki gidanku na san su ɗin duk inda suke hankalinsu na tashe."

Ba ta ce komai ba, sai dai idonta ɗa ya yi ƙwal-ƙwal. Likitan ya zo a gabanshi ya yi mata *check up* sosai ba wani damuwa take ya amince da sallamarsu.

Ya kwaso 'yan tarkacen da ya zo da su, ita ɗin ma flask ɗin shayi ta riƙe da kayan da ta cire, don da yana zuwa ya sawo mata doguwar riga, lokacin da ya sai kayan shayi ya zo mata da su.

Sun daidaita a kan titin sabuwar Jami'ar Bayero, ya juyo a hankali ya ce, "To ina ne gidan na ku?" Cikin sanyin murya ta ce, "Muna Gwauran Dutse ne, kusa da gidan Isyaka Rabi'u, tsallaken gidan Zakka layin gidan mai unguwa, layi biyu daidai *junction.*"

Saboda ya fahimci gurin, tun da unguwar ba baƙuwar shi ba ce, bai kuma ce mata komai ba, har sai da suka shiga layin mai unuwar. Sannan ya juyo ya ce, "Ina kenan zan yi?" Da hannu ta nuna mashi ƙaton gidansu, ya rage gudun motar ta tafi shuu a hankali har ya tsaya ƙofar gidan, kawai sai ta fashe da kuka, ya kalleta a tsorace, yana tambayar lafiya? Tana hawaye ta ce, 'Farin ciki nake, ni wai ashe da rabon zan kuma ganin gidanmu a duniya?" Ya yi galala da baki yana kallonta, ai ba ta kuma cewa komai ba ta buɗe motar da gudu ta yi cikin gidansu.

Yabi soran gidan na su da kallo. Sannan a hankali ya fito daga motar ya jingina ya harɗe hannaye a ƙirji, yana kallon soron gidan da jama'ar da ke wucewa jefi-jefi a layin.

Minti ɗaya, biyu, uku, har tsayin minti bakwai bai ga alamar jama'ar gidan za su kuma magana ba. Ya yanke shawarar aikawa don ya yi sallama da ita ya wuce nasa

wuri, kamar sun sani, kawai sai ya ga jama'a yuu sun fito. Samari biyu da kananan yara su uku sai wata matashiyar macce, rungume da jarir i da gani sun masifar kama da wacce ya kawo da gani ba tambaya 'yar uwarta ce, sai kuma matsakaitan mata su biyu. Kallo ɗaya ya yi wa ɗayar ya gane ita ce mahaifiyarsu sai wata da bai tantance matsayinta ba. Gaba ɗayansu suka yo gurinsa, cewa sukai, "Wayyo Allah, sannu malam, sannu dai, Allah ya biyaka mun gode kwarai." Matar da yake ganin ita ce mahaifiyarsu ta ce, "Ai ba ka tsaya daga waje ba, daurewa za kai ka shigo cikin kafin mahaifanta su zo." Bai musa ba ya bi umarninsu ya shiga aka buɗe masa falon Babansu ya zauna, duk suka zagaye shi, har abin ya fara bashi tausayi, ita kuma ta rukunkume Hajiya sai kuka take suma haka suna yi suna dariyar murna. Ba a fi minti biyar ba sai ga maigidan da wasu mutane har su huɗu, guri sai ya daɗa kaurewa da tasibihi, hailala, haukala da hamdala da Allah ya fito da Sakina, wacce sai lokacin nen ya san sunanta.

Bayan kura ta lafa wan maigidan ya ce, 'Samari mu kam dai ba wani abu da za mu iya gode maka da shi ko saka maka sai dai mu yi maka addu'ar Allah ya yi maka tukuici kai da iyayenka da abin da ya sani mafifici wurin daraja, domin ka dawo mana da farin cikin da ya yi kaura cikin ahalinmu, mun gode Allah dai ya biya amin."

Ragowar suka amsa da amin. Ya ce, 'Wai a ina ne ka hadu da ita?" Shi din ya yi godiya ya bayyana iyakar abin da ya faru da wanda ya gani, gur aka kuma kaurewa. Uwar sai kuka take yi a lokacin ita Sakina ta yi shiru sai hadiyar zuciya take yi kawai.

Baban nasu ya ce, "Ya ki nan uwata, matso kusa na ji ɗominki, matso nan na daɗa godewa Allah da ya fito da

ke daga duhu, kika fito haske. Kai madallah da Allah Ubangijin haske da duhu." Ta rarrafa ta isa cinyarshi ta ɗora kanta a kan shi, sai ta dafa fashewa da kuka. Shi ma duk dauriyarsa sai da ya ringa share hawayensa, ɗakin ma kowa sai ya shiga matsar kwallah a kai ɗif na ɗan tsayin lokaci. Sannan barista ya yi ƙarfin hali ya goge tasa kwalar ya ce, su yi haƙuri shi kam zai wuce Allah dai ya kyauta gaba.

Sai nan Alhaji Maikuɗi (wato yayan Alhajinsu) ya ce, "Samari muna dafa godiya kwarai, amma dai bai kamata ka tafi hakan ba, dole ne mu san muhallinka yanzun kai ɗin ai na mu ne zumunci ne kuma zai ƙullu tsakaninmu." A kai ɗan dariya ya bayyana inda yake cikin ƙofar Nassarawa nan iyayenshi suke Babanshi dai ya rasu, sai dai akwai mahaifiyarshi da sauran yayunshi maza a cikin unguwar. Su kai masa addu'a mai yawa gaba ɗaya aka rako shi har waje da alƙawarin za su zo har gida yi masa godiya da ban gajiya,, yana mai sunkuyar da kai yake cewa, "A haba ba komai, ai duka Musulmi ɗan uwan musulmi ne. A cikin Musulunci ai an hore mu da taimakon kai da kai."

"Wannan haka yake, mun gode, sai dai ka ganmu a giada magabata."

Ya juya zai shiga motar. amma sai da ya juyo don ya kuma ganin fuskar Sakinan. bai samu damar hakan ba, domin ta sunne ta a kafaɗar uwarta kukan ne dai. Kai lallai wuya ai ba ta da daɗi, kaga halaka ka fito ai dole ka koka ka kuma gode. Tausayinta ya ƙara kama shi. ya yi addu'a a zuciyarsa na neman tsari da mugaye azzalumai, na ce amin summa amin.

Ya shiga motar suna ta ɗaga masa hannu, har sai da ya ƙule, ya daina ganinsu ta cikin madubinsa. Ya hau titi

sambal don ya isa gidansu, shi ma ya samu ya huta, don duk jiya barcin dai *half done* ne. Cikin gidan kai tsaye ya shiga ya samu Hajiyar na zaune ita da autarta Maryam. Maryam ɗin na cin abinci, ya yi sallama su kai maza suka kalle shi, ya zauna kusa da Hajiya ya ce, "Ya gida Hajiya?" Tana ta bin shi da kallo har ya tsargu. Ta ce, "Lafiya lau, kai za a ma wannan tambayar lafiya dai, yau ba ka kwana gida ba? Ni ɗin ban san haka ba, sai dai Maryam za ta yi aike da sassafe ta ga ƙofar mu hanhai, ashe a buɗe ta kwana, an leƙa gunka ba kai ba motarka, tun safe ake ta neman wayarka ba a samu ba, yanzun nan nake cewa idan har Azahar ta yi ban ji wani labari ba, zan tuntuɓi 'yan'uwanka, don ma dai kar na yi saurin tayar musu da hankali da tun wuri Maryam ta gaya musu, ni ce na hana ta na ce kai ɗi ai ba yaro ba ne za ka kula, idan lokaci ya ja ne to lallai ba lafiya ba." .

Ya laluba aljihun wandonsa inda ya aje wayar, shi kanshi bai san ya ya a kai ta mace ba, koma har ya Allah tun da ya tashi yau bai neme ta ba. Ya kunna ta da *full charge* ɗinta, ƙila garin barci ne ya matseta abin da bai saba ba, barci da wasu karikice. Ya ja ajiyar zuciya, ya sunkuyar da kai ya ce, "Ki yi haƙuri Hajiya abuuwan ne kawai suka zo a hakan, ni ɗin na yi kuskure da ban shaida muku ba, amma kun ji, kun ji." Şuka çe, "Umh! Lallai Subhanallah ya ya 'anya ba 'yan mafiya ba ne suka sace ta?"

"Ba mamaki duniyar ai ta riga ta lalace, ga yadda ima... jama'a ya yi ƙaranci duniyar ce ake ta juta ta kow... ce siga ke dai kawai Allah ya tsare mu ... masu mu... nufi."

Hajiya ta ce, "Amin dai, amma na tausayawa ... yayen yar... da ita kanta ta ga mutuwa tsirara. Ko ha... tsayin

yaushe ne aka sace ta?"

"Allah ne masani sai ita ɗin." Cewar Baristan, ya ce. 'Maryam nima ba ni abincin na ci man, ban ko karya ba duk yau."

"To akwai koko da ƙosai, sai ɗumamen tuwo, wanne za a kawo." Ya harareta, don duk aba cimar shi a cewar shi koko fitsari da yunwa yake sashi, gara ƙosan, tuwo ko ai kun san caftar mu ta baya.

Ya ce, "Daɗa mini ruwan shayi na sawo biredi a waje." Ta ce, "Ai ma muna da biredi mu ma."

"Shi kenan ta kwana gidan sauƙi, bari na shiga ciki." Ya miƙe ya shige wurinshi. An yi wurin minti talatin, sannan ya yi sallama da Hajiya ya fita harkokinsa.

An yi wurin sati biyu, yana ta waƙar ya kamata ya koma ya duba ta ko ya take? Amma sabgoginsa da hidindimunsa ba su bar shi ya sami sukunin hakan ba, sai dai ya kan tuna haka a ransa.

Ranar wata Labara aka ce ta bawa ranar sa'a. Ranar ne barista ya samu nasarar shari'ar da ake ta ta awa tsakanin wani shahararren mai kuɗi da wani maka nsa talaka. nda ya ɓata mishi 'yarshi da ƙarfin tuwo kin hikiom irin na Ubangiji ya ƙaddari yarinyar ta samu ciki. ba a fahimci hakan ba sai da cikin ya yi wata biyar soda sirri da Allah ya ɓoye. Tun lokacin suka tuntuɓe shi a yi tsallan albarka ya ce bai san zancen ba, bayan ya sami ama tana K a tana dabo ne shi da shi. domin rigima su ba-'yar ka n ba, don sai 'yansanda ne suka shiga tsakan aka haƙurk tar da shi. har aka cusa masa kuɗi, ya cusa shar ya yi ah ya isa, ya yi tafiyarsa da Alhajin da 'yans dan sukai d nya, suka ce yanzun ai ka ga kun rabu wata ace don ya aina gaisheka? A banza wai talaka ya girmi s i..

To bayan lafawar wannan sai ga ciki, shi kuma bai shawara da kowa ba ya maka shi a kotun shari'ar Musulunci, Barista Muttaƙa shi ne lauyansa. Da taimakon Allah, tare da taimakon Adai-daita Sahu ta Malam Ibrahim Shekarau.

Wannan yasa yau yana jin shi cikin farin ciki mai yawa, abubuwa ne da ba su cika faruwa ba, domin me? Shi kansa talakan a kansa bai da jarumtarka da zai iya tunkarar wanda ya zalunce shi in dai mai kuɗi ne, kawai ya gwammace ya bar shi da Allah, ko ya ja shi ne ɗin dai a ƙasa. To ga wanda ya yi jarumtar kamar shi malam Musa, sai ka kai gaba, sai ƙarfin naira ta taka rawa yanzun sai ka ji gun ƙilama a bika da ƙaton sharrin da za ka ɓatawa mai kuɗi suna.

Ya iso gidansu misalin huɗu da sha uku, rigarshi ta aiki kawai ya cire ya yo alwalar sallar La'asar yana idarwa ya faɗa gidansu neman abinci. Abin da shi yafi ganewa kawai ya tsugunna ƙarƙashin uwarshi ya ci abin da tun usuli yaci ya rayu, baya wani biye-biyen gidajen abinci. (Sai mu ce matarshi ta caɓa).

Hajiya ya iske ita ma cikin farin ciki tana mishi maraba da yalwar fuska ta gabatar masa da abinci cikin irin abincincikan da yake so. Sinasir ne da miyar taushe da ƙashi, ya yi farin ciki ya zauna ya naɗa suna hirarsu gwanin daɗi.

Yana suɗe hannu ta ce, "Dazu kuma sai kai baƙi misalin sha biyu da rabi na rana, kun dai yi saɓani, sun ce a gaisheka har sun kawo ma tsaraba mai yawan gaske." Ya moɗi ruwa ya ce da ita.

"Su wa kenan Hajiya?"

"Iyayen yarinyar nan man da ka tsinta sun zo har da

uwarta da ubanta da yayyanta biyu har ita Sakinar yarinya lafiyayya. Na daɗa tausaya mata. Sun zo ne wai so ƙara maka godiya bisa taimkon da kai musu, a ga juna kuma a sada zumunci."

"Haka ne, nima na gode tun kwanaki nake son zuwa duba su to kin dai sanni da sabga ba ta ba ni sukunin yin hakan ba."

"Haka ne, ai yanzun zuwan naka ma ɗin ai ya zama dole bayan kai har da sauran yayyanka ku yi masu godiyar kyautar da sukai maka." Ya ɗan zaro ido.

"Kyauta wacce iri haka Hajiya?" Ta gyara zama tana mai murmushi ta ce da shi,

"Kyautar mutum zuwait, ka ko san wannan babbar kyauta ce da ta fi komai daraja. Babanta ya baka Sakina matsayin mata, in ka amince kawai a tura 'yan'uwanka ai maganar. Ni kam na yi na'am da zancen na yi ta godiya ina ƙarawa, wallahi na yaba da surukan naka suna da mutunci da karamci." Ya mutu murus a nan har bai ina san da wane irin lafazi ne zai magana ba, domin shi zancen ya zo a bazata. Wai mata lallai kam da sake.

Ya ce, 'Wane irin zancen ne wannan daga sama, haka ake yi? Ai da an fara tuntuɓata ba sai an zo an yi mini karan tsaye ba, wannan kamar dole ko abun ya yi mini ko bai mini ba.."

Ta ce, 'Wallahi kuwa, ka ko san ila an ƙi da an so uwar turare kwalba ce, kuma ko ka amince ko ba yardarka ban shige gaba na auro maka Sakina na kawo maka ɗakinka, in ya so bayan ta zo sai ka nuna ninin kai ɗin ka haihu, kai mata saki uku kwarara, to wai nan kawai za ka tsira da shi, bayan wannan insha Allah nan da wata huɗu masu zuwa gab da Azumi Sakina na ɗakin a. Ni mai zan ce

musu wanda ya ga darajata ya yi mini kyautar girma yaushe zan butulce? Na sani ita ɗin ai ba rasa miji ta yi ba, ba kuma kwaɗayi ne ya sanya su ba mu ɗiyar ba, alheri ne kawai a kai niyyar mayarshe shi alhairi, ai kawai mu ma sai mu yi adddu'ar fatan alhairi." Cikin sanyi jiki ya ce,

'Haka ne."

Bayan wannan bai tofa komai ba, ya miƙe ta bi ƙeyarshi da kallo ta ce, "Idan waje za kai leƙa mini gidan Hauwa kai mini kiranta idan kuma mijinta na nan ka barta ka kira mini shi." A ransa ya ce, shi kenan na kuma shiga uku, duniya za ta ji kenan na banu, mai neman kuka ne aka jefe shi da kashin awaki.

Da ya fita ɗakinshi kawai ya yi wucewar shi, ya kwanta rigingine a kan gado ya runtse ido yana tunanin shi a wani *class* yake a yanzun? Ajin farin ciki ko na takaici? Allah kenan wato dama dai matarshi ya tsunto da kanshi, ya yi ta ƙokarin ya harsaso hotonta duk *channels* ɗin sun yi *scasin no signal* sai duhu kawai. tun da ba haske sai kawai ya rintse ido ya cigaba da tunanin shi, kuma haka nasa yanayin auran ya ɓullo. Tun da Hajiya ta amshe ya sani kwarai da wuya abin idan bai yiwu ba. Hajiya kenan da ta rangahuma. Sai ya sami kanshi da dariya, shi ma ya na fatan lokacin dai ya zo ya dai yi auren ya huta ko kanwa ta kar tsami kwarrafi ya kwanta.

Ya miƙe zumbur ya yi gidan Kuluwa, tana ta ƙokarin haɗa sanwar dare yake gaya mata saƙon Hajiya ta ce, 'Lafiy dai irin wannan kiran bam-bara-kwai abin da Hajiya ba ta saba ba?"

"Ba na jin in wata matsala ce, ta ce ma idan mijinki na gida ke ki huta, kin ga ko ai ba wani *realy serious things* ba ne. Ki bari ma ko bayan Magriba kya je."

Ta ce, 'Haba dai, bari na kira Amina ta duba mini girkin nan tun da na hada komai na je na dawo Barista."

"Shi kenan Allah ya jisshe mu achairi amin." Ya rigata ficewa bai komai gida ba, wata sabgar ya fada kawai.Ta ringa dariya da suke tattaunawa da Hajiya ta ce, "Lallai ma Barista shi ne ya ringa basarwa, kamar da dai bai san a kan me kike kirana ba. Hajiya kai na ji dadi bana da mahuta dama ina shirin hada shi da Nalako Azumin ba nan don tuzurancin nasa ya yi yawa." Sukai dariya ta ce, "Kin dai san kamar mai aljanar dare aure shi kam ba ma na jin yana cikin tsarinsa, ban da dai a gabana yake ai da na ce kawai ƙadangarun bariki ne suke hure masa kunne suke gaya masa ƙarya, amma ban da haka sa'anninsa tuni sun tsufa da 'ya'yaye, mai shi yake nema wanda bai samu ba?"

Hauwa ta ce, "Ba komai Hajiya lokaci ne kawai, ba gashi ya zo ta yanda bai taɓa mafarkin samu ba."

Ta ce, 'Haka ne Allah dai ya sa alhairi, ya kuma sada mu za a yi. Amin."

Cikin kwana biyu zance ya cika dangi Barista ya samu mata har za a kai kuɗin neman auranta. Shi ɗin ba wanda ya kuma mashi maganar daga gida, sai dai a waje aka tare shi ana yi Allah ya sanya alkhairi. Har abin ya ringa bashi mamaki kwarai ranarar kwana uku Hajiya ta nada yayyansa da ƙanin Babanshi da wanta ta ce shi ɗin ya yi musu jagora su je godiya, bai musa ba ya sha wankanshi da boyel fari mai tsadar gaske ya ɗebe su sai Gwauran Dutse unuwar Yalwa.

Akasarin 'yan kasuwar Kano musamman na cikin gari ba su fiye zuwa kasuwa ranar Lahadi ba, ko kuma in za su sai a *late hour*, don haka gidansu Sakina ba su da masaniyar zuwansu, hakan kuma bai sa su ɗin sun daki

gurbi ba, babanta yana gida don shi sai lokacin ma yake karin kumallo. Gidan Alhaji Maikuɗi, a ƙarshen layin yake, nan da nan suka haɗu da wani maƙocinsu.

Bayan an yi gaishe-gaishe na al'ada Alh. Ibrahim ya yi godiya ga karamcin da sukai masu na basu 'ya sukutum, sun karɓa sun gode da hannu biyu. Alhajin ya ce, 'Ai ba komai abin da ya yi mana ɗin ai mu ba mu da wani abun saka masa, an yi hakan ne kawai da ganin ƙila ɗin an kamanta."

Suka ce, 'Haka ne, muma mun gode ga shi har mun zo da kuɗin neman auranmu da sadakinmu gaba ɗaya na naira duhu hamsin sauran bayani da shiri idan kun gama kwa aika mana, mu dai muan san matarmu kafin Azumi."

Tabɗi! Daɗi kan daɗi, sun yi murna kwarai ba su yi tunanin abun haka kusa kusa ba, Allah kenan. An rabu ana ta godiye-godiye da shi albarka.

Barista kam sun yanke shi don shi ba a sanar da shi haka ba, da bai biyo su har cikin ɗakin neman auranshi ba, yana raba ido ya wanda ya yi wa sauƙi ƙarya ba. Haka nan jikinshi ba wani kwari shi ya yi zumbur ya riga su fita, wannan kuma ya san duk shirin Hajiya ne. Koda suka shiga mota uffan bai ce musu ba ya sawa bakin makulli su ɗin ma ba su kula ba, hirarsu kawai suke yi.

A gidan su Sakina ma murna suke ta ta yi, ita ɗin dai ba ta ce komai ba, ba kuma a ganin yanayin komai a gurinta, sai ba a ta tata. An yi la'akari da yanda ta zama yanzu komai sannu take binshi ba zafafawa. Har dai Abdul wanta ya gaji ya ce, "Ke kowa na murna ke ɗin ban ga kamar abin din yi maraba da shi ba, a tunanina ke ɗin ce za ki fi kowa farin ciki, mutumin da ya ceto ki daga duhu ya kawo ki haske?"

Ta ce, "Haka ne rawa zan ta yi, mantawa na yi ai ku yi hakuri." Ya bita da ido kawai, kalamanta sun yi kama da bakar magana. Bai dai kuma cewa komai ba.

An sami wajen sati uku rannan Amma Mamarsu Sakina ta ce, 'Ni ko kin ga mutuminki din shiru ban ji ance ya zo ba, ko ya zo din ba na nan?"

'Ai ina ganin abin da yake ranshi ne yake nunawa kila kyautar da ku kai masa ce ba ta gamshe shi ba." Hajiya ta bita da ido kawai, a ranta ta dan jiwo kamshin gaskiya, amma sai ta ce, "Bai amince din ba, har suka kawo kudin aure da sadaki gaba daya ke din nan fa jama'a kawai ake jira su hadu a shafa ki zama ta su."

Ta ce, "Na yane, amma kika sani ko yardar wasu ce? Mazan yanzun nan fa ba a yi musu irin wannan daren sai ki ga komai tsawon lokaci suna ma mutum dage tunda dai ba da guminsu suka nema ba. Ina jin kawai tilastawar wasu ne?" Tana fadfa tana share hawaye. Amma ta yi shiru can jim ta ce, 'Kin ga ni din ba kuka za ki mini ba, addu'a kawai za ki yi nima zan taya miki, idan akwai alhairi a lamarin nan Allah ya sani a kulla, idan ko ba wani haske, Allah to ya musanya shi da alhairi sai ki ga komai ya zo da sauki ta yanda baki zata ba. Kuma ke din ma na fahimci kamar ba ki yi maraba da abin da a kai ba?" Ta girgiza kai tana hawaye.

"Amma ba laka ba ne ko ku din ba ku yi hakan ba ai ni ya cancanta na yi haka da kaina, domin bayan ku a duniya ai ba na ganin wani da daraja sama da shi, ni wahalar rayuwa ke sai rake gudu."

"Wannan da ai Allah za ki bar wa auren yanzun na soyayyar ma kark yake yi? Ai gara ai 'ya haka ko ya ringa tuno alhairin da a kai masa, ya ringa rangwanta miki a

yawancin lokuta, don ya san ke ɗin ba wai rashin malayi kika yi ba, ko kuma wani dalili, alhairi kawai a kai niyyar yi, ki yi haƙuri kawai ki bar komai a hannun Allah."

Ta ce, "To Amma."

Kamar da sani washe gari da safe Barista ya tashi cikin nishaɗi kuma bashi da wasu hidindimu da zirga-zirga hutawa kawai yake son yi, amma zuciyarshi ta raya mishi yau dai gara ya je ya ga 'yar yarinyar nan ji yake shi ɗin bai kyauta ba, don a kan sa bai neme ta ba, duk da da komai yake magarrtata nan ranshi.

Ya miƙe zumbur ya shigo cikin gurin Hajiya don ya karya, ya samu sun yi wainar shinkafa da miya ya ja kujera nan kusa da *kitchen* aka zubo masa yana ci, ya ce. 'Maryam yau man ki shirya ki yi mini rakiya wani guri?" Ta ɗago daga kan murhu ta ce cikin fara'a, "Ina yaya?" Ya juya ya kalli Hajiya ya ga shi take kallo, shi ko take kallo ɗin ya yi murmushi yana sosa ƙeya ya ce, 'Share zan gaya miki." Hajiya ta yi dariya ta ce, 'Gara ka gaya mata ba dai gidansu Sakina ba ne, kai kana da muhimmin gurin da yafi sama da aikin ka?"

Yana dariya bai tanka ba, har ya ƙarasa ya miƙe ya ce, 'Wurin sha biyu ki shirya zan fito mu je." Ta gyaɗa kai.

Ta juya ta kalli Hajiya ta ce, 'Hutun dai bai samu ba? Na je gidan mutane ba wani ɗan abu da zan riƙa musu?"

"Haka ne to me za ki riƙe?"

"Hajiya tunda muna da *flour* zan mata donot zan kuma tura gun Anti Hauwa na karɓo *cake* na san a a samu tun da da wuri take yi."

Ta ce, 'Shi kenan sai ki aika mata ɗin, kar a sami matsala."

Kafin sha biyu har ta yi wanka ta naɗe kek ɗinta

donot a *foil paper* ta yi wa Yayan *flashing* ya bugo ta ce. "Ni fa *am ready."* Ya ce, "Haba dai, to ba ni minti goma na watsa ruwa, kin ganni kallo nake yi."

"Shi kenan ina jira." Ta ce da shi.

Ya fito cikin kyakkyawar riga, *jean* ... *shirt* sababbi fil, sun kuma amshe shi so... ya yi kyau cikakken saurayi mai hankali ba gaya ɗan fafa ba. Su kai wa Hajiya sallama sai Yalwa.

Sha biyu da ashirin Maryam ta yi sallama a gidan kishiyar Mamansu ce a tsakar gida ta amsa ta ce, 'Maraba." Ta yi fara'a ta bita har ɗakinta, bayan sun gaisa ta ce, "Sunana Maryam inan tare da Yayana Muttuƙa na zo ne gurin Sakina." Ta faɗa da fara'arta ta ce, 'A'a lallai to maraba zo mu je." Ta bi bayanta zuwa gun Amma. Bayan sun gaisa Ummin ta ce, "Ga baƙuwar Sakina da mijinta nan sun zo." Daɗi ya kama Amma ta ce, "Lallai maraba lale. amma kuma kin yi sa'a yanzun ba ta daɗe da fita ba yayanta ya kaita gidan yarsu." Ta ji wani iri, amma sai ta ce, "Ba komai tun da na ga guri na dawo idan an kwana biyu, a gaida ta, yayan ya ce a gaishe ku."

Suka ce, 'Muna amsawa ya Hajiyar ta ku?"

"Duk lafiya lau, ita ma tana gaishe ku."

Duk sun yi jigum nan rashin daɗi ta miƙe ta ajiye kayan da ta zo mata da su ta ce, "Gashi a ba ta in ji Hajiya sai anjima." Suna ta godiya, amma ta ce tsaya mana ki amshi ko goro ne, ta ce "Na gode wallahi, ku bar su, ba komai ai zan dawo nan da kwana biyu." Sun kaɗa sun raya sai ta yi har zari ma ta yi waje.

Parketa yana zaune shiru, yana jiran ya ga wanda zai fito sai ga Maryam ita ɗaya, ta fito tana fara'a ta buɗe motar ta shige ta rufe yana kallonta ta yi dariya ta ce, "Ba ta na

ƙa, mun daki gurbi." Ya wani zaruo ido,

*"What?* Ita ba ta daddara ba ne, ce nake garin yawo a ka sace ta yanzun kuma za ta kuma fita, kuma fita ba tare da izini ba." Maryam ta riƙe baki, "Yaya a gaban ƙa iyayenta take, kuma da yardar su ɗin ta fita, ba kuma yawo ne ba zumunci ta tafi, gidan 'yar'uwarta ne kuma tun da ta dawo ba ta taɓa fita ba ita ɗaya sai yau, yau ɗin ma kuma yayanta ne ya goyata a lifan ɗinshi ya kaita." Ya yi wani huci na ɓacin rai kamar ya daki Maryam ɗin, don haushi. Ba ta ce komai ba, tana ta kallonshi tana mashi dariya a cikin ranta yanda ta ga yana bala'i.

Can ta ce, 'Ka yi haƙuri mu tafi, ai kai kana da dama ko da dare ne ka dawo."

A hasale ya ce, "Ba zan dawo da daren ba, waye ne bawanta da izinina ta fita, ko ta manta ni ɗin har sadakina na biya ne?" Maryam ta riƙe baki, "Lallai abun *is biger."* Ta ce to yi haƙuri, bari na koma na tambayo kwatancan gidan da ta je sai mu bita." Bai ce komai ba har ta buɗe mota ta fita, lallai ya amince. (Kun ji mu da mutum, ashe da ana so?).

Amma ta kuma ganinta ta yi mamaki ta ce, "Au ba ku tafi ba?" Ta yi 'yar dariya ta ce, "Yaya ne da rigima faɗama yake ta yi wai ta fita ba sani ba, sai an kuma ɗaukcta, yanzun dai kwatancen inda take za a mana mu bi ta."

Amma ta rufe baki cikin dariya zuciyarta kamar auduga. Lallai dai ya yi na'am ba kamar yanda suka zata ba. Ta ce. 'Ai ba ma wani nisa ta yi ba, nan Gadon Kaya ne kwanar F.C.E. in kun shiga ta Kofar Famfo layi na biyu ku kalli hannun hagu, ga gidan nan mai bene da farin fenti shi ne gidan."

Ta ganc kwatanccn da kyau, su kai sallama ta fito ta samc shi ya kifa kai da sitiyari, ta rufc motar bayan ta shigo ta cc, 'Mun yi sa'a ba ni sa ba nc duk hanya cc, Gadon Kaya nc." Ta yi masa bayani kawai sai ajcta ya yi a ƙofar gidan. Ta fito a hankali ta taka ta shiga ciki, gidan ya yi mata sosai mai kyau da tsari. Ta yi sallama yaran gidan suka amsa tabi bayansu har falon gidan. Tana shiga da Sakina su kai ido hudu, haka kawai zuciyarsu ta buga a tarc ta yi sallama da fara'a ita ma ta amsa mata ta ajc kofin ruwan hannunta ta cc, "Bismillah mana zauna." Ta zauna ba ta raba ɗayan biyu ita ce Sakina, saboda kamar da ta ga suna yi da babarsu sai kuma hotunan da ta gani nata a falon; kafin ta cc wani abu Zainab ta fito matar gidan goye da yaronta ta juya ta gaisheta sai da ta zauna ta amsa duk suna mata kallon baƙonta. Ta yi dariya ta juya gun Sakina ta cc, "Ba ki sanni ba, amma dai ni baƙuwarki ce." Haka kawai ta raya wani abu, amma sai ta cc, "To na gode sannu da zuwa bari na kawo miki ruwa."

Ta ce, "To." Ta kawo mata lemun fanta da *purc water* da kofi ta tsiyaya mata duk biyun, sai da ta sha. Sannan ta tsarcta da ido ta ce, "Sunana Maryam, ni ƙanwar Muttaƙa ce, na je gidanku Hajiyarku ta cc ba ki nan ta yi mini kwatanccn nan shi ne na biyo ki."

Kawai sai ta dafe ƙirji cikin fadfuwar gaba matsananci ta ce, "Haba, da'allah kai na ko godc. sannu kin sha hanya ya gidan?" Ta yi murmushi, domin dai ta burgcta. Kyakkyawa da ita, komai na ta cikakkc mai ƙiba. ƙibar mai tsari wanda mai ita zai mori, domin dai wanda ya yi ta ya kiwatata da kyau kwarai, ko'ina fa laushi nc da nama mai tsari, komai an ajc shi muhallinsa. Ta cc, "Lafiya. tarc fa da yayan mukc yana wajc."

Zainab ta ce, "Haba da'allah shi ne ki kai shiru, aka bar shi a rana, da kin yi magana ai. Kai Mus'ab ɗauko *key* ɗin ɗakin baƙi a kan *dressing mirrow* ka buɗewa *uncle* ka fita waje ka ce ya shigo."

Hakan ko aka yi, Zainab ta sa aka kai masa ruwa da lemo mai sanyi, ita ɗin ce ta sa hijabinta ta leƙa suka gaisa sun gane junan da kyau, sun ɗan yi hira har ya karɓi yaron bayanta Almustapha. Ta ce, "To bari na wuce na turo Sakinan." Ya yi murmushi.

Sakina da Maryam hira suke, har suna hasashen sanin juna. Maryam ta ce, "Na yi *secondary G.G.S.S.* Kwa." Ita kuma ta ce Danzabuwa ta yi *form one to six,* to sanayyar ba ta nan ba ce. Ta ce, "To ni ina B.U.K *Department of Edu,* ina karanta *English Education level 200."*

Sakina ta faɗaɗa murmushi ta ce, "Kila to a nan na sanki ni ɗin ina karanta *Hausa Education,* amma ni *level 3000* nake." Su kai dariya ta ce. "Ba mamaki, muna ganin gilmawar juna shi ya sa muka gane fuskokinmu." Suka shiga hirar abin da yake faruwa tsakanin *lactures* da Yar Adua', har ya jawo yajin aiki (strike). Yaya Zainab ta dawo ta ce, "Ke Sakina ki je man kin bar baƙo, bar mini Maryam za mu yi hira da ita." Ta miƙe a hankali duk wani jinta take fanko gaban ta sai faɗuwa yake yi. Ta ɗau gyalanta ta fito. Tafi minti uku a bakin ƙofa tana tsaye ta kasa shiga, sai da ta yi namiji ƙoƙari, sannan ne ta kira sunan Allah, ta ɗage labulan haɗi da sallama da murvarta mai sanyi. Wani irin faɗuwar gaba suka samu a lokaci ɗaya, shi ɗin sai duk ya wani rikicee ya gigice, saboda har ga Allah bai taɓa zaton wannan zabirar ba ce. Zuƙi, ka barikallah, masha Allah! Abin da yake ta faɗa kenan. A fili ya yi ta maza ya haɗiyi

wani miyau ya ja fasali, sannan ya ce, "Bisimillah man ƙaraso, kin cake."

Ta yi murmsuhi mai kyau ta ƙaraso dab da shi, sai ta zube nan gabanshi tana gaishe shi, shi kuma sai ya hangame baki kawai yana kallonta kumatunta ya yi na'am da shi, sha'awa yake bashi, inda yake kallon nan na ta kamar kawai ya ya ɗauke ta ya goya yake ji.

Ta saci kallon shi ganin bai amsa ba, ta ga murmushi yake ta yi kawai yana nkallonta. Wata irin kunya ta ji matsananciya,, ta sunne kanta. Ya ɗan motsa ya ce, "Kya ɓoye kan ki man, kin kyauta mini kenan, wai ni ina can ina ta ɓoyan mata a gida ashe ke yawo ma kike ban sani ba, sai an sace mini nke kuma na zo na shiga uku?" Ta ɗago kai, ta rausayar da ido ta ce, "Lah!K Allah ba na zuwa ko'ina, gidan ne ya yi mini zafi nasa yaya Muji ya kawo ni nan ai nima tsoran fita nake yi."

Yanda ta yi maganar gaba ɗaya sai ya sukurkuce, kallonta kawai yake yi ya ce, "To me ya sa gidan ya yi miki zafi haka ba dai laifi na ba ne ko?"

Ta ce, 'Ah bame kai mini?"

"Na yi laifi man, ai ban zo ba ko?"

"Ga shi nan ai ka zo yanzun."

"Haka ne, to ya kike, ya kufan jiki duk da na gane kin yi sumul, kin yi *free* kamar kazar *Agric,* ashe haka Allah ya yi miki tsari mai kyau, shegun duniya za su yi mini ƙwalele." Su kai dariya tare, ya ce, "Gaskiya da an cuçe ni,, an taɓa ce miki *you are so beautiful* irin haka?" Ta girgiza kai alamar a'a. Ya ce, "Ba mamaki, Allah ne ya sanya hijabi a kan fuskarki don da samari sun ganki ba abin da zai hana su sace ki." Dariya kawai take masa. Zuciyarta na mata dadi tana yi tana satar kallonshi, shi ɗin ma mai

kyau ne komai nasa *fresh* alamar yana jin daɗin shi yana rayuwa cikin godiyar Allah. Yatsun ƙafarshi zara-zara *chocolate colour,* sun luf-luf da su. Wani irin daɗi ya ratsa ta matsananci. Gaskiya Allah kam ya yi mata baiwa mai yawa, don da gani ya bata miji na gari, mai usuli mai kyau, da gani babban goro ne sai magogin ƙarfe. Kafin a ba ta shi sai da aka jarrabata, jarrabawa mai tsanani. Lallai kam ƙila da ba dan wannan silar ba da ba a ba ta shi ba.

Tana wannan zancen zucin aka yo masa waya ya ce, 'A'a ya ya Barista *wake up?* Kai na manta gobe ne zaman shari'ar? Gaskiya yanzun ina tare da mai ɗakina ne." Ya yi dariya aka ce maka ko yaushe jiya ce? Yau ai daban take mai sabon salo, Allah da gaske nake yi in ka musa kuma ka zo nan ka gani da idonta. Ya shiga yi masa kwatance. Su kai sallama. Ya kalleta yana mata murmushi ya ce, 'Abokina ne na gurin aiki ƙut-da-ƙut, wai yana zaton wasa nake masa na ce gani ga mai ɗakina, kin san ni gaskiya ba mai irin wannan halaiyar ba ne, wacce akasarin maza ke yi." Ta jinjina kai.

Ya ce, "Kin ko san mijin naki lauya ne?"

"A'a yanzun dai kana gaya mini."

"To haka ne, na samu a ƙallah shekara goma ina aiki kuma Alhamdulillahi ina ganin nasara a kan duk abin da na sa a gaba na aiki."

Ta ce, 'To mun godewa Allah, Allah ya taimaka, amin."

Ya ce yana murmushi, "Ke din fa *J.S* nawa kike?" Sai ta ƙyalƙyale da dariya. Dariyar tata ta burge shi shi ma sai ya tayata ya ce, "Na yi ba daidai ba ke nan?"

Ta ce, "Ni din na yi kama da 'yar *J.S.S* ne?" Ya ce, "Wai dai kar na yi zari ki ce na zura jiki?"

"Haka ne, to *J.S. 300 level* nake a Bayero ina karantar Edu Hausa."

Ya zare ido hadi da rike baki ya ce, 'A'a, a'a lallai ashe *execellency* ce ke tsoro kawai nake miki." Ta yi murmushi. Ya ce, "To bari na yi sallah sai na wuce, amma da daddare zan dawo hirar ba ta ishe ni ba kar masu gidan su kore ni." Ta ce, "Haba kora, yanzun ai ka zama na su suma." Ya ce, "Haka ne, ke ma shiga ki samo mini ruwan alwala, idan kuma Shehu ya roka mana ne sai ki zo ki yi gadina kar wata ta ṣace miki ni." Ta yi dariya ta ce, 'Ashe dai ka iya barkwanci, amma idan an ganka kamar ba mai fara'a ba." Ya ce, Ko? Nima din mamaki nake ashe zan iya zance gaban 'yanmata na zaci sai a gaban *judge."*

Fita ta yi kawai har tana tuntuɓe, don tsananin farin ciki da jin dadi. Ta samu Maryam ta zama 'yar gari har ta ci abincinta ta yi sallah, tana hutawa. Yaya Zainab ta ce, "Yauwa shigar masa da nasa abincin." Ta dauka ta kai ma, har ya yi kabbarar sallah ta dawo ita ma don ta yi tata. Bayan ta idar ne ita tama kasa cin abinci, sai da ta bashi ratar minti sha biyar sannan ta koma, ta tarar wannan abokin nasa ya zo tare ma suke cin abincin. Ta yi sallama suka amsa ya ce, *"Wonderful,* kan dai ba ke din ba wace za ta make mana shi, har ya ringa sambatu wannan mai bakin ran?" Ta yi dariya ta tsugunna nesa da shi ta ce, "Ina wuni?"

Ya amsa, 'Lafiya kalau Madam, gaskiya na yi farin ciki kwarai, ba na abokina zai fita daga gorin Nalako zai yi aure, amma abin da ya ban mamaki shi ne, wai har yaushe abin ya faru kuma har manya sukai magana aka zartar duk ba mu da labari, to da sai dai ka gayyace mu daurin aure ko ko? Kai fa mugun kulli gareka." Ya kyalkyale da dariyar

nishaɗi ya daɗa kashingiɗa yana wani kallonta ƙasa-ƙasa, shi kansa mamakin kansa yake wai shi ne a gabanta yake wannan sangartar.

Ya ce, 'To yaushe zan ringa buɗe harkata *so open*, ni da ke da masu ƙullina, kana jin ko wannan Alhajin da mu kai shari'a da shi ya fahimci ina da wannan ba ya zago ya yi mini mugun ƙulli ba, gobe kawai sai dai na ji ta a gidansa." Suka ƙyalƙyale da dariya ya ce, "Wai da na mutu ni mut." Ya yi ƙoƙari suka haɗa ido da ita, ya kashe mata ido, ita ɗin bala'in mamaki kawai yake ba ta. To da jan ajin na maye da ya share kamar bai yi na'am ba? Ko kuma dai maganar Amma ce da ta ce ƙila hidimomi ne suka ɓoye shi? Ta ƙi yarda ta kuma kallon shi don yana ba ta matuƙar kunya ga kuma bárista Ibrahim a gabansu.

Ibrahim ya wurga naman miya ya taune ya kura ruwa ya ture kwano ya ce, "Ko dai ba ka ci ba, ba ganewa za a yi ba, cewa za ai dai tare muka ci tun da kai soyayya ta cika maka ciki, kuma wallahi tashi za kai ba-sabam-ba, haka kawai ka sani bulayi ni ɗaya a Kano. Haƙuri za ki yi *exellency* ki ara mini shi zan rako miki shi da dare, idan tawa matar ta yi *approving*, wani muhimmin aiki ne ya taso *pls.*" Ta sunkuyi da kai tana matsa hannu ta ce, "To ba komai, Allah ya taimaka ya bada sa'a."

"Yauwa edcellency godiya nake." Ya miƙe har da rankwafa mata, sannan ya tsaya gaban shi ya ce. "Oya to tashi man duk ka wani [illegible]

Ya miƙe haka [illegible] sai, haka kawai mutum na tare da iyalinsa ka tsige shi? Ina cewa yau ɗin hutu na ne, shi ya sa na ɓabi sakewa da su?"

"Oho dai tun da an ba ni *approval* tashi za kai." Ya miƙe ya ɗau mukulinsa ya ce, "Na ji, to yi gaba za mu [illegible]

ko?"

"To wannan kuma, ina waje zan jira, a fito lafiya."

Ya ɗan dafa kujerar da take zaune ya ce, "To *exellency* zan wuce ina tabbatar zuwa na dare nan, amma ki ba ni *phone number* ɗinki ma soye ta waya." Ta ɗan matsa gefe saboda hucinsa sosai take ji, har tsakar kanta. Sannan ta ce, "Ni ba ni da waya ta faɗi." Ya kalle ta.

"Kin matsa ne don na takura ki?" Ba ta bashi amsa ba. Ya ce, 'Shi kenan, ungo *Starcoms* ɗina zuwa gobe duk wanda ya kira ki ce ba na kusa, kuma dai yanzun tun da na bude wuta kuma ke ɗin sai hakuri, ina fatan ba za ki gaji da ni ba ko?"

"Haba gajiya dai, abin da rai ke so?"

"Ko?" Ya yi tambayar.

"Gaskiya ni ɓarayin nan dai sun mini daidai, don ni kawai suka satowa ke, ƙila da badan hakan ba, ni dai ban ga inda zan ganki ba, har nima na sace kin."

"Ka manta rabon kwaɗo baya hawa sama, ko ya hau faɗowa zai yi?" Ya ce, "Haka ne, na gode kwarai da gaske, yau ba zan iya kwatanta miki farin ciki da nake ciki ba, domin dai da zuciya a zulumi take, yanzun ta yi *fresh* na san ni ɗin wani irin mai sa'a ne mai yawan gaske, an mini baiwa da kyakkyawar mace, mai ilimi da usuli mai kyawu ko? Gode maśa kawai zan ta ta yi ina ƙara yi. Allah ya bar mu tare ki ce amin da ƙarfi na ji." Ta sunne kai tana ɗariya. Ya fara tafiya ya ce, 'Ki ce Maryam ta fito kawai mu wuce, wancan bawan Allah kar ya gaji da jirana." Ta ce, 'To." Ta juya ta shige ciki ya bita da kallo komai nata ya yi mishi, lallai ta wahala a ganin da ya yi mata lafiyayyar macece sosai. A fili ya godewa Allah sosai.

Har ƙofar gidan ta yi wa Maryam sallama sun rabu

nishaɗi ya daɗa kashingiɗa yana wani kallonta ƙasa-ƙasa, shi kansa mamakin kansa yake wai shi ne a gabanta yake wannan sangartar.

Ya ce, 'To yaushe zan ringa buɗe harkata *so open,* ni da ke da masu ƙullina, kana jin ko wannan Alhajin da mu kai shari'a da shi ya fahimci ina da wannan ba ya zago ya yi mini mugun ƙulli ba, gobe kawai sai dai na ji ta a gidansa." Suka ƙyalƙyale da dariya ya ce, "Wai da na mutu ni mut." Ya yi ƙoƙari suka haɗa ido da ita, ya kashe mata ido, ita ɗin bala'in mamaki kawai yake ba ta. To da jan ajin na maye da ya share kamar bai yi na'am ba? Ko kuma dai maganar Amma ce da ta ce ƙila hidimomi ne suka ɓoye shi? Ta ƙi yarda ta kuma kallon shi don yana ba ta matuƙar kunya ga kuma bárista Ibrahim a gabansu.

Ibrahim ya wurga naman miya ya taune ya kura ruwa ya ture kwano ya ce, "Ko dai ba ka ci ba, ba ganewa za a yi ba, cewa za ai dai tare muka ci tun da kai soyayya ta cika maka ciki, kuma wallahi tashi za kai ba-sabam-ba, haka kawai ka sani bulayi ni ɗaya a Kano. Haƙuri za ki yi *exellency* ki ara mini shi zan rako miki shi da dare, idan tawa matar ta yi *approving,* wani muhimmin aiki ne ya taso *pls.*" Ta sunkuyi da kai tana matsa hannu ta ce, "To ba komai, Allah ya taimaka ya bada sa'a."

"Yauwa edcellency godiya nake." Ya miƙe har da rankwafa mata, sannan ya tsaya [illegible] ya ce. "Oya to tashi man duk ka [illegible]

Ya riƙe [illegible] ne kai, haka kawai mutum na tare da iyalinsa ka tsige shi? Ina cewa yau ɗin hutu na ne. shi ya sa na zaɓi sakewa da su?"

"Oho dai tun da an ba ni *approval* tashi za kai." Ya miƙe ya ɗau mukulinsa ya ce. "Na ji to yi gaba [illegible]

ko?"

"To wannan kuma, ina waje zan jira, a fito lafiya."

Ya ɗan dafa kujerar da take zaune ya ce, "To *exellency* zan wuce ina tabbatar zuwa na dare nan, amma ki ba ni *phone number* ɗinki ma soye ta waya." Ta ɗan matsa gefe saboda hucinsa sosai take ji, har tsakar kanta. Sannan ta ce, "Ni ba ni da waya ta faɗi." Ya kalle ta.

"Kin matsa ne don na takura ki?" Ba ta bashi amsa ba. Ya ce, 'Shi kenan, ungo *Starcoms* ɗina zuwa gobe duk wanda ya kira ki ce ba na kusa, kuma dai yanzun tun da na bude wuta kuma ke ɗin sai hakuri, ina fatan ba za ki gaji da ni ba ko?"

"Haba gajiya dai, abin da rai ke so?"

"Ko?" Ya yi tambayar.

"Gaskiya ni ɓarayin nan dai sun mini daidai, don ni kawai suka satowa ke, ƙila da badan hakan ba, ni dai ban ga inda zan ganki ba, har nima na sace kin."

"Ka manta rabon kwaɗo baya hawa sama, ko ya hau faɗowa zai yi?" Ya ce, "Haka ne, na gode kwarai da gaske, yau ba zan iya kwatanta miki farin ciki da nake ciki ba, domin dai da zuciya a zulumi take, yanzun ta yi *fresh* na san ni ɗin wani irin mai sa'a ne mai yawan gaske, an mini baiwa da kyakkyawar macce, mai ilimi da usuli mai kyawu ko? Gode maśa kawai zan ta ta yi ina ƙara yi. Allah ya bar mu tare ki ce amin da ƙarfi na ji." Ta sunne kai tana dariya. Ya fara tafiya ya ce, 'Ki ce Maryam ta fito kawai mu wuce, wancan bawan Allah kar ya gaji da jirana." Ta ce, 'To." Ta juya ta shige ciki ya bita da kallo komai nata ya yi mishi, lallai ta wahala a ganin da ya yi mata lafiyayyar maccce sosai. A fili ya godewa Allah sosai.

Har ƙofar gidan ta yi wa Maryam sallama sun rabu

suna begen juna, ta mikawa Maryam ɗin ledar da Antie ta bata ta karɓa tana godiya. Barista ya yi mata hom ita kuma ta ɗaga masu hannu ta dawo a guje cikin gidan ta yi *super* kan gadon Antie, ta ce, "Kin ga Allah ko Antie?"

"Ah to mai na gaya miki ne? To da a ce ba su yi *follow up* ba, da a ka kai musu zancen shi ne sai ki ce wani abu, ba gashi ba yanzun? Ni kam na yi miki murna sosai don kin yi sa'ar namiji *very handsome* wallahi wayayye, mai ilimi." Ta ce, "Bari Anti Lauya ne guda fa."

'Ah lallai Allah ya tabbatar da alhairi, amin."

Ta wuni cikin wani irin farin ciki marar misaltuwa, ba ta taɓa fadawa soyayya irin wannan ba, da ta shigeta farat ɗaya mai yaji.

Ta miƙe ta ce, 'Yaya Zainab, don Allah sa Malam Sani ya kai ni gida." Ta riƙe baki, "Au! Dama zuwan ba na kwana ba ne?" Ta langaɓe kai tana murmushi. "Cewa ya yi zai zo gida fa da daddare, kin ga dai gara na je, ya kamata na ringa ɗaukan al'amuranshi da muhimmanci sosai." Ta gyaɗa kai.

"Hak ne, Allah ya kiyaye, kira Sadiƙ ya yi masa maganar sa, ya kai ki."

Ta shigo gidansu cikin walwala tun a soro Sa'adatu avar karaɗi ta tare ta tana ba ta labari mijinta ya zo da ƙanwarshi sun kawo musu kek mai daɗi. Ta rungumeta tana jin daɗi har ta leƙa ɗakin Ummi ta yi mata barka da gida. Sannan ta yi ɗakin Amma. Sai daï ta samu tana *kitchen* wurin hidimar girkin dare. Ta leƙa ta yi mata sannu, sannan ta wuce ɗakin kai tsaye. Sa'datu aka kinkimo mata ledar kayan. Ta tsugunna tana buɗewa, ta ɗau kek ɗaya ta gatsa, daɗinshi ya yi mata har tsakar ka. Sai Amma ta shigo ta tsaya kawai tana kallonta da mamaki, ita kuma

suna begen juna, ta mikawa Maryam ɗin ledar da Antie ta bata ta karɓa tana godiya. Barista ya yi mata horn ita kuma ta ɗaga masu hannu ta dawo a guje cikin gidan ta yi *super* kan gadon Antie, ta ce, "Kin ga Allah ko Antie?"

"Ah to mai na gaya miki ne? To da a ce ba su yi *follow up* ba, da a ka kai musu zancen shi ne sai ki ce wani abu, ba gashi ba yanzun? Ni kam na yi miki murna sosai don kin yi sa'ar namiji *very handsome* wallahi wayayye, mai ilimi." Ta ce, "Bari Anti Lauya ne guda fa."

'Ah lallai Allah ya tabbatar da alhairi, amin."

Ta wuni cikin wani irin farin ciki marar misaltuwa, ba ta taɓa faɗawa soyayya irin wannan ba, da ta shigeta farat ɗaya mai yaji.

Ta miƙe ta ce, 'Yaya Zainab, don Allah sa Malam Sani ya kai ni gida." Ta riƙe baki, "Au! Dama zuwan ba na kwana ba ne?" Ta langaɓe kai tana murmushi. "Cewa ya yi zai zo gida fa da daddare, kin ga dai gara na je, ya kamata na ringa ɗaukan al'amuranshi da muhimmanci sosai." Ta gyaɗa kai.

"Haka ne, Allah ya kiyaye, kira Sadiƙ ya yi masa maganar sai ya kai ki."

Ta shigo gidansu cikin walwala tun a soro Sa'adatu awar karaɗi ta tare ta tana ba ta labari mijinta ya zo da ƙanwarshi sun kawo musu kek mai daɗi. Ta rungumeta tana jin daɗi har ta leƙa ɗakin Ummi ta yi mata barka da gida. Sannan ta yi ɗakin Amma. Sai daï ta samu tana *kitchen* wurin hidimar girkin dare. Ta leƙa ta yi mata sannu, sannan ta wuce ɗakin kai tsaye. Sa'datu aka kinkimo mata ledar kayan. Ta tsugunna tana buɗewa, ta ɗau kek ɗaya ta gatsa, daɗinshi ya yi mata har tsakar ka. Sai Amma ta shigo ta tsaya kawai tana kallonta da mamaki, ita kuma

ta yi sukui na rashin gaskiya. Ta ce, 'Sannu rasa kunya ɓeran tanka baki iya tsayawa har a gabatar miki da shi?" Ta miƙe tana dariya ta ce, "Afuwan Amma ba zan kuma ba, yunwa nake ji, ban samu nutsuwar cin abincin ba gidan yaya Zainab."

Tana murmushi ta ce, "Sun je miki ne?" Ta gyaɗa kai.

"Sai dab da La'asar mam suka tafi."

"Da kyau kin ga abin da nake gaya miki ko? Kila dai wata matsalarce ta ɓoye shi, ya ku kai da shi?"

"Lafiya lau, shi ma ɗin abin da ya ce kenan, wai ba na tsoran kuma abin zai ƙara sa ni fita. Na ce, yaya Muji ne ma fa ya kai ni." Ta ce, nan ma haka ƙanwar tashi ta ce mai kirki kuwa, wayayyya."

"Wallahi Amma ai na santa haka sama-sama dai makarantarmu ɗaya sai dai na fita da shekara ɗaya, kuma karatunmu yana da alaƙa da juna."

"To da kyau Allah ya ƙula alkhairi ya sa haske a cikin lamarin, amin." Ta amsa a ranta, amma sai ta yi saurin matsawa daga gaban Amma.

Tun bayan sallar Magriba take baza kunne ta ji aike har bayan ƙarfe goma, sai ta saddaƙar bai sami zuwan ba ne, ranta ya yi mata wani iri, ta lashi zumar fa mai zaƙi, dole ta ƙudundune a gadon Amma rungume da waya tana wassafa shi a ranta wannan tunanin sai ya sakar mata barci mai daɗi.

Cikin barci ta ji wayarta da ke ƙarƙashin *pillow* tana *ringing*, ta yi firgigit ta tashi, kowa a ɗakin ya yi barci, Amma kuma na ɗakin Baban. Ta awo *pillow* sai ta ga sunan Maryam. Muryarta ta yi sanyi kwarai ta amsa, "*Hellow* Maryam kun je gida lafiya?"

"Ke Maryam, ce za ta kira *around this time*, me za ta ce miki? Kin kalli agogo ko ƙarfe nawa?" Ta kuma yin *cooling* ta ko kalli agogon ta ce. "Biyu da rabi." Ya ce, *"Good*, yanzu lokacin soyayya ne. Ya na ji ki *so cool* ko kin yi barci ne na tashe ki?" Ta kuma muskutawa ta rife wayar sosai ta ce, "Ni ko mai zai hana ni barci har zuwa wannan lokacin? Tashi dai na yi da ka kira."

Ya ce. 'Ni ko kin ga soyayyarki ta hana ni barci, yanzun haka tangararau nake, bayan na gama rubuce-rubucena ma *Film* nake kallo yanzu, na ce to bari na tashe ki mu gani tare ko ma raya daren tare." Ta yi ɗif. ya ce, "Kin yi shiru?"

"Me zan ce?"

"Au! Ba ki ji abin da na ce ba, na maimaita?"

"A'a na ji ka sarai, amsar ce dai ba ni da ita."

"Ko? To ni ina da abin faɗi, kin san yanzu mai jarumin *film* ɗin da nake kallo yake wa budurwarsa?"

'A'a."

"Na gaya miki?" Ta yi shiru. Ya ce, 'In ba ki so ki hana ni in ba haka ba zan faɗa." Ta yi ɗan murmushi yana jinta ta ce, "To ka yi haƙuri."

"Na yi wallahi, don abin da girma a gunki, ni ɗin ba komai ne a guna ba, saboda dai na biya sadaki, kuma ni ji nake ma ina ma tare da ke nake ƙarƙashin mayafi ɗaya." Ta ce, 'Sai da safe." Ya kyalƙyale da dariya ya ce, "Ke ashe matsoraciya ce ko? Ai gara ki sabo ni wallahi ban taɓa soyayya ba, don haka duk soyayyata haƙuri za ki yi ki ɗauka, don duk akin ki zan ƙare ƙarfina, na fi hude wuta sai haƙuri." Ta ja tsali ta ce, ' To shi kenan "

"Yanzun in haƙura in bar ki ki yi barcin ko kuma na faɗa miki [illegible]

"Kin yi shiru, kin amince kenan?" Nan ma shiru. Ya yi dariya ya ce, "Matsoraciyar soyayya, bari na Kyale ki tun da ta Kare miki."

Ta ce, "Haba dai ogana na dai Kyale ka ne."

"Au! Haba bude mini mayafin ki to na shiga." Ta Kyalkyale da dariya ta ce, *"Good night."* Ba ta jira mai zai ce ba ta kashe wayar.

Zuciyarta ta ringa bugawa da sauri da sauri, saboda tsananin jin daɗi na soyayya, abin da take matuKar buri ga mijinta ya so ta ya rintata, ya koyar mata soyayyarshi mai daɗi, ta ko samu. Kai godiya ga sarki Allah da iyayenta da su kai hikimar ba ta shi a matsayin mijinta.

Waɗannan tunane-tunanen masu daɗi suka saukar mata da barci mai daɗi da nutsuwa, har ya so makarar da ita sallar Asubahi sai da aka fito masallaci, sannan ta farka ta shiga banɗaki ta tsaftace kanta ta ɗauro alwala ta zo tana sallah ta daɗe tana sujjada tana Kara godiya ga Allah ga ni'imar da ya yi mata da wasu buKatu a kan shi.

Da safe da kuzarinta take komai, rabonta da cikakkiyar walwala irin wannan tun kan a sace ta, domin da ta dawo wani irin sanyi ta yi komai ba ta ɓaɓa za fafa shi, ita da ta riga ta sallatma. Ba dan ita ɗin mai addu'a ba ce, kafin da bayan abin ai da ta zauce ko kuma kafin ta dawo daidai a raya, irin abubuwan da ta gani.

Kowa ya amince farin cikinta da raharta ya dawo, saboda soyayyar Mustufa. Da rana misalin sha biyu, ya zo bai shigo ba ya aiko da kan waya *Starcom* sabuwa dal ya ce a bata zai dawo da daddare, ta amsa da farin ciki mai yawa ta nunawa su Amma da Ummi suna sun yi farin ciki, dama tun jiya aka tsaiguntawa Baban zawan Barista tun da har an fara Korafin bai zo ba, shi ɗin shiru ya yi bai ce komai ba.

har ta gama tsegumi ta fita. A ransa ya ce mata ƙenan masu duniya.

Da yamma ta bayar aka sayo mata kayan ciki mai kyau, ta yi masa farfesu da dankalin turawa daƙwa-daƙwa. Ai ko kamar a unguwar ya yi sallar Magriba, don ana idarwa ba daɗewa ya aiko. Amma ta ce, "Wannan dai ko tuwan dare dai bai tsaya ya ci ba." Ta ce, "Ba sai ya ci wannan farfesun ba."

'Au! Barfesu abinci ne?" Ta yi *smilling.*

"To Amma ai tuwo ku kai, yanzun sai kawai na lafta mishi tuwan dawa na kai masa?"

"To me ye, tuwo ba abinci ba, an gaya miki kowa ke ce, da ke gudun tuwo, ƙila shi a gurinsa ya zama abincin marmari." Ta taɓe baki.

"Ni dai bari na je idan zai ci sai kawai na dawo kar na yi kayanshi na dawo da shi, kin sanfa 'yan yanzu ba kamar ku ba ne, wani baya son cin mai nauyi da dare." Ta ce, "Allah ya kiyaye Sakina."

Ta gama shiryawa da atamfarta *Super England* wacce ta yi mata *Nevia roll on* ɗinta *sure cool blue,* sai *powder* ta *beauty fair,* sai kuma turarenta da take mayata Lailatus Sahra. Ta yafa gyale ma baɗin kayan, ta yi kyau kamar yau ne dai za ta shiga ɗakinta. Ta tura Aisha ta kai masa abin da ta shirya masa da ɗan lemunta na zoɓo. Ya ko ba ta kuɗi ya ce su raba ita da ƙannenta.

Ta yi sallama ɗakin Muji a nan a kai aro za a soye. Yana kishingiɗe sai ya tashi zaune, yana cewa, 'Aiɓ lale da amaryata kin yi kyau, kamar in saki gaban mota in ta yawo da ke." Ta yi *smilling* mai kyau da yake ƙawata fuskarta, ta je gabansa ta ɗan rankwafa tana gaida shi. Ya shaƙi ƙamshinta ya ce, "Kai na gode duk. Allah ya biya, an

dadada mini rai, ya kin wuni lafiya?"

"Lafiya lau, ya su Hajiya da Maryam?"

"Duk lafiyarsu lau, suna gaida ki har da Antie Hauwa ma."

"Wacce kenan?"

"Matar Yayana da na fi shiri da ita."

"To ina amsawa ya gajiyar aiki?"

"Gata nan, amma ai an fara kawar mini da ita, jibi fa irin kwalliyar da aka mini." Ta yi murmushi ta zauna sosai ta janyo tire din ta ce, "Bari na ba ka wannan kila dai ba a tsaya an ci abinci ba." Ya ce, "Kamar ko kin sani na ranar mu dai *snacks* kawai na ci." Ta tsaya da bude kwanon ta ce, "Haba dai ya zama da yunwa irin wanna?"

"To ya za'a yi kai ka katangala rai ba gata, sai sanda ka samu sukuni dan abin da aka girka a sammaka, in bai maka ba duk ka fita gari nema." Ta yi jagale . Ya ce, 'Ai gara ki yi, ki yi ki zo ko nima dai na zama dan gatan nan, a daina mun gori duk inda na je neman abinci. Allah tsine ranar da Hajiya ba za ta yi mini gori ba, hakuri kawai nake yi tun da na san ba mai ba ni." Ta yi dariya ta ce, "Har da Hajiyar?" Ya ce haba. "Tabdi! Ai gara kowa ma da ita Hajiyar, ke dai bari kawai garama na koshi, yau idan ta yi mini tayin abinci na ce na ci a gurinki." Ta yi dariya.

"To ai ni wannan dai ba abinci ba ne, abin washe baki ne, amma dai a gida sun yi tuwo Amma ta ce na zubo maka, ban zubo ba, bari na je." Ya yi saurin daga mata hannu ya ce, 'A'a *wait*, wane irin tuwo?"

"Na dawa."

"A'a kai bar shi, ba ni wannan din na kawai ya isa." Ta sunne kai tana dariya ta ce. "Ba dai kai ma ame da cot din nan baya cikin 'yan kayanka ba?" Ya ce, "Ke dai bari."

Ba ta labarin artabunshi na tuwo da su Hajiya, su kai ta dariya ta zuba mishi farfesun, ya fara ci. Ta ce, "Bari na zo." Ya ce, 'Kar ki daɗi." Ta yi murmushi ta fita tana shiga gida ta gayawa Amma abin da ke da akwai ta ce, 'To me za a ma shi ina da guntuwar miyar rana, na san za ta ishe shi cin abinci."

"Amma bada kuɗi a je kantin Isuhu a sawo kus-kus leda ɗaya, sai a dafa da sauri." Ta ce, 'Shi kenan je ki."

Yana ta zuƙar rumanshi ya yi mishi daɗi, ta dawo. Ya ce, "Zo nan mu ci tare."

"Na gode na ƙoshi."

"Au! Haka za ki ringa mini kina cinye abincin kina ƙylale ni?" Ta ce, "A'a, ka yi haƙuri ba zan kuma ba."

"Na yi."

Ba a kai minti ashirin ba, sai ga kus-kus ya sauka, yana tururi, ya ce, "Ke wahala ki ka je kika sa mutane?"

"Haba wahala ka manta kai ɗin ɗansu ne da suke ji da kai?"

"Eh ban manta ba, duk da haka kamar an takura."

"Ko ɗaya wallahi." Ya ce, 'To na gode kwarai." Ta jawo ta fara zuba mashi. Ya ce, 'Ba kuma isa ba, sai kin matso mun ci tare, don wannan dai yanzu ya sauka bare ki ce kin ci tuni, kuma a filet ɗaya za ki zuba ." Ta ce, 'To Oga."

Ta zuba kus-kus da miyar a tire ta samo cokali, ta ringa hilatarshi suna hira ya ci sosai yana haɗuwa da fef-suf ɗin shi, ya ƙoshi sosai, har ya ringa jin kasala da barcin bayan ƙoshi.

Ta ce, "Ko na miƙo filo ne?"

"Haba dai idan na yi miki barci ya za ki yi da ni?"

"Sai na lulluɓe ka na yi ta gadinka, har sai ka tashi."

Ya yi dariya.

"Na ƙi wayo, so kike na bar tarihi a ce nan da yana neman auranta har barci yake musu à gida."

"To maye duk a cikin so ne.".

"Haka ne, to zo matso ki yi mini tausa mu ga ko barcin zai zo." Ta yi saurin ja baya, har abin ya bashi dariya ya ce, 'Kin ga daɗina da ke baki da jarumta, da ni ce ke zuwa kawai zan yi me ye a cikin tausar?"

"Ba komai, ba sai na zo ba, na amince ni ɗin ba ni da jarumta." Ya ce, 'Gaske kuwa."

Sun yi hirarsu mai daɗi, har kusan goma saura kwata ya ce, "Bari na tafi, sai kuma na kira *midnight call,* kin san ai ɓa iya barci zan ba, tun da kuma ke kin shigo *system* ɗin."

"Haba dai ka yi haƙuri ka yi mini, rashin barci illa ne da shi babba, gashi da safe ba samu za kai ka rama ba harƙokinka za ka fita.' Ya ce, "Shi kenan na ji ko kokenki za a duba mai yiwuwa." Ta yi masa rakiya har gurin motar shi, ya buɗe ya ɗauko mata leda *Viva,* cike da kayan shafe-shafe da ɗan na kusa da baka. Ta ce; "Haba baka gajiya ne, hidima dai ɗazuma fa na ga waya ko godiya ban ba." Ya taɓe baki.

"Ke kin san ko irin daɗin da za ki jiyar da ni, ki ke wani surutu dan na kawo wannan? Toshiyar baki ce fa, ta yanda za a ringa bari na ina ta iyo a cikin ruwa yanda nake so." Ta yi saurin ɗaɗe fuska, zancen ya girmi kakarta, ta miƙa mar wayarsa, ya amsa ya dungura mata ledar ta amsa [illegible] bashi guri, ya shiga mota, ya ce, "Masoraciya sai da safe, ai mafarki mai kyau, amma kar anan rowa, a ɗan buɗa mini." Ta yi saurin juyawa tana ɗaga hannu ta shige gida, sai da ya ga shigarta, sannan ya ja mota cike da

farin ciki ya tafi.

Ta shiga gida ta aje kayan, sannan ta ɗawo ta tattara kwanokan da ya ci abinci, ta shiga gida da shi. Muji ya ce, "Ya dai tafi ko? Ni barci nake ji." Ta ce, "Ya tafi an gode wallahi." Ya ce, "Ba wani an gode miƙo ledar za ki yi mu ga, mai kuma mutum zai samu a ciki." Amma ta ce, 'Wannan dai halin banza ne haka girma yake?" Ya ce, "Um-um Amma kar ki ce komai, idan na hana ɗakin nan fa haushi za ku ji ai ko gara nima a ba ni toshina kawai." Ta zazzage kayan gabansu, *set* ne na kayan shafa *Niven* kamar ya san irin su take shafawa, sai *Dove* shima *set* har da turarensa. Sannan biskit da alawas masu daɗi da inibi a ledarsu nunannu.

Ya ɗau biskit ɗaya da alawa ya fasa ledar inibi ya ɗiba, ya ce, 'Sai da safe." Amma ta harare shi ya yi dariya ya yi gaba. Ita ko sai dariya take ina ruwan sakis gonar auduga akwai fara'a kamar ni a gari.

Ta rarrabawa kowa kayan kwalam, kayan shafawa ko ta kammale kayanta a ɗaki, ta yi barcinta mai lafiya. Bai ko kira ɗin ba. Da ya je gida su Hajiya sun rufe ƙofarsu sai kawai ya kulle ainahin ƙofar gidan ya yi addu'a ya je ya yi sallar Isha'i da Shafa'i da Wuturi ya yi addu'a ya kwanta da tunanin uwargidanshi a ransa. Wani irin hasken su ne ke haskawa a ranshi har kamar ya faso ƙirjin ya fito. Ya ringa tunanin ashe haka so yake? Lallai a ringa ganin bekensa da ya gaza to ina kuma gaya ci harawa ya yi birgima a cikinta? Wayyo da wannan sambatun wani irin barci mai daɗi ya yi gaba da shi. Bai aje shi kusa ba sai a fadar Sakina tsundum.

Soyayya ruwan zuma, in ka sha ka ba ina masoyi. Allah ya haɗa kowa da masoyinshi na alhairi. Amin, ('Yan mata a yi ƙoƙarin tsarkake soyayya don ta yi danƙo ta yi

inganci'in un je fa. Ni da kaina zan bada tsaraba don a moc ta da kyau. Dariya).

To haka dai, wata irin soyayya mai danko ta shiga tsakanin, wanda har abaa iya ɓoyewa ko a gaban waye ne. Fadi take Ogana shi kuma ya ce *Excellency* ta ce kaza-wa-kaza. Har dai rannan Amma ta ce, "Ba dai kya ko jin kunya Sakina gaban kowa fada kike Ogana-Ogana, sai ki nuna mini wanda bai da Ogan?" Ta sunkuyi da kai wata irin kunya matsananciya ta ratsata ta ce, "Ki yi hakuri Amma. Ta ce, 'A'a ke kadai, ni me ye nawa? A dai ringa farsa baki."

Haka abin yake shi din ma Hajiyar har mamaki take wai yau Muttaka ne ke gigi a kan mace, abin da baya kayansa, ta dai amince lokacin ne dai kamar yanda ya sha fada mata. Kornai Sakina za ta yi sai Oga ya sani ya bada *approval*, in ko fita ce in ta furta tana san zuwa guri kaza ba musu zai amince in lokacin ya yi masa to sai ya yi kokari ya kai ta, in kuma yana da ta shi sabgar ne sai a sa wani lokacin ya kai ta. Dukkan 'yan uwanta sun san shi farin sani, da ke kuma shi ma mutum ne wayayye, na jama'a, mai sabgar jama'a ya sa ko'ina ya shiga sai an karɓe shi, an kuma yaba masa shi ta ko ina. Kyakkyawa da shi, gogagge, kalar kyan dai Hausawan da suka sami nutsuwa da kwanciyar hankali. gashi da dogon hannu (Kyauta). To wannan ya sa yake da farin jini sosai.

Hakan abun yake a gurinta, ba ta aje shi kusa ba, kaunarshi take son ai a ganinta bayan iyayenta ba mutumin da ya san darajarta aye da shi. Ko Kuma fa haka ne? Don haka dukkansu sun amince su din hadi ne kawai daga Allah. A zuciayr ta da take tunani idan ta aure shih ta huta da takaicin dai duniya, kuma fa haka ne, yayin da 'ya mace

ta yi sa'ar namijin ƙwarai a kai sa'a ita ɗin ta san darajarshi sai su mori rayuwarsu mai kyakkyawan inganci.

Ku ji ni da Sakina na ta sambatu ta ji garɗin soyayya, ta ɗauka da son soro da nan ɗaki *are ekual* a ina? Bari dai ma ji ma gani an bunne tsohuwa da ranta.

Komai aka samar to dole ya zama ƙararre, illa Ubangiji wanda yake (Al-Hayyu, Al-Kaiyumu), wanda mutuwa ba ta ƙarshensa, farkon da bai da farko, haka kuma ƙarshen da bai da ƙarshe. Allah kenan.

Lokacin bikin ya ƙarato sosai, har ya kasance sauran kwana ashirin da uku, wato tsayin sati uku da kwana biyu, a yi abin. Yayin da masoyan ke ta nuna maitar junansu a sarari, har gani suke anya ko za su kai l abari irin wannan zumuɗi ko dai iyakarta kenan? Wannan ce damuwar da Barista yake yi a wani dare da ya zo mata da katiunan ɗaurin aure. Ta ce, 'Haba, Ogana mantas kawai da ranka da lafiyarka za ai komai har ma ka girbi abin da ka shuka da hannunka. Kana mantawa da Allah ne da sanya so da ƙi a doran ƙasa, duk fa albarka so ne mu, domin ƙarfin son da Allah ke wa Rasulillah (S.A.W.) shi fa muke dangwala."

Ya ce, 'To Allah ya sá muna raye amin."

Ta gyara zama. "Ni dai tsoron dai da nake ji ɗaya Barista a wayi gari ka daina sona, ka daina shagwaɓa ni, da riritani, to ina zan saka kaina?" Ya ce, "Au! Kina shakkar son da nake miki kenan?" Ta girgiza kai alamar a'a. Ya ce, "To *trust me my dear edcellency* zan baki mamaki, ke kin ko san amfaninki gare ni?"

Ta ce, "Na sani, wai lokacin da ka gama tsotsewa aya zaƙinta ba tofar da tukar za kai ba?"

Ya ce, 'Eh to haka ne, ba haka ba, ya danganta daga wani zuwa wani, wani da ya tsotsen sai ya tofar, wani ma

ko gama tsotse ɗan ruwa-ruwan bai ba zai zubar domin shi burinshi dama ya ji garɗin ayar kawai ne, amma yayin da wani kuma sai ya taune ya tsotse tas ƙarshe ya haɗiye tuƙar don in ta je cikin maganin basir za ta yi masa. Kin ga a nan ra'ayi ne kenan, ya danganta da kai fahimtar da kai wa aya, da kuma irin darajojinta da suka zo kunnenka. Kuma kin sani sosai a cikin kayan sawar ki akwai atamfar da ta yi miki, kallon farko za ta kwanta miki a rai ne, sai ki sawo a tsala miki ɗinki ki yi ta ji da ita, kina lallaɓata ta inda har ta tsufa da kyanta, kuma duk wani biki na musamman da ita za ki. Amma wata fa ga ta nan ne dai, wani ma wanki ɗaya za ki yi mata ta fita a kan ki ki bayar. Ko na yi ƙarya?" Ta girgiza kai.

"To kin ga *is like that,* don haka ba na fatan Allah ya sa na dainan sonki, zan ta addu'a Allah kullum ya ƙara mini sonki, ke kuma ya ƙara miki ganin darajata sai ki ga mun yi rayuwarmu mai daɗi, har ai ta sha'awar mu a ringa Allah ya ba ku mu samu ko Allah ya samu a danshinku ko baki fata?" Ta kashe masa ido da yin wani *smilling* mai burgewa irin wada yake kashe shi. Ya ce, 'Au! Za ki fara ko? Ni fa sati ukun nan kamar shekara uku ne nake ganinsu." Ta ce, "Haba dai Oga, rufe idonka kafin ka buɗe har an yi an gama ma." Ya ko rufe ya buɗe, ya ce, "Ya ba ai ba?"

"Gajan haƙuri ka yi, da ka hari na ce ka buɗe da kan ka." Su kai dariya.

To haka dai har yau saura kwana uku a sata a lalle amarya ta je gidan gyaran jiki an gyareta, an mulmule a sumul, ke kya ce 'yar baby ce *natural beauty skin* ɗin nan ya dada fitowa zahiri ga wani hadaddan ƙamshi, duk motsi kamar ƙeso turare take yi In ta kalle ki kya ce wani abu ta ɗisawa idanunta,, don wani haɗaɗɗan kyau da ta yi. Barista

har baya iya cewa komai, sai ya zama *so silent,* sai dai ya yi zuro yana kallonta. Har sai ta gaji ta ce, "Kai, Oga gaskiya kar ka gama kalle ni tun ban shiga ɗakina ba, irin wannan kallo?" Sai ya yi ɗan gajeran murmushi ya yi irin abin tausayin nan, ta ce, "Ya ne, ba baka sai ido da kunne?" Sai ya yi dariya.

Ko ni miyau na haɗiya mukut, ina zan kai ta? Ai sai irin su Oga Barista.

Yau Alhamis yau ce ranar da za ai kamunta, kamun da aka shirya yinsa a gidan Yaya Zainab a harabar gidanta. An shirya gun da fararen kujeru sun zagaye shi, sai aka bar tsakiyar ba a sa komai ba sai aka shimfiɗa ƙatuwar tabarma, aka ɗora kafet. Sannan dadduma da ɗan tuntun taushin nan nan sarakai, nan ne amarya ta zauna tare da ƙawayenta sun zagayeta a gefe danginta ne uwa da uba, gefe kuma nan aka warewa dangin miji ina za su zauna don zaman kamu, a ɗaya gen kuma Sayyada Tasallah Nabulsi Baƙo ce, malama da za ta yi wa'azi a gurin kamun.

Yanda na ga yanayin kamun ya yi matuƙar kyau da tsari, an gabatar da wa'azi mai tsauri dangane da wuta da waɗanda za su shige ta. Sannan an kuma karkato akala kan aure bautar Ubangiji inda malamar ta ƙare bayani da wata 'yar Hausa da Hausawa ke faɗi, Duniya sai da kuɗi, lahira sai da hali, zaman gidan miji sai haƙurin. Wannan haka yake kam, gidan miji fagfe ne na yaƙi ko kai nasara ko ya yi nasara a kan ka, don haka sai ka ƙulla ɗamarar cin kaɗo da ko wane irin *hardship* a cikinsa da fatan ganin bayansa, ba kamar yanda 'yan mata da wasu sakarkarun zawarwan ke tunani ba. Aure a hole kawai a ji daɗin duna. Tabɗi kan ka ji daɗi ɗaya, ka ji wuya goma. *Take care,* tabbas za a hole, amma me kar ka sa holewar ita ce ginshiƙi ka gane bauta ka

je yi, in ko aka ce bauta, magana ta ƙare, bawa ai wahalalle ne sai yanda Ubangijinka ya yi da kai.

An gama taron wa'azi lafiya lau, jama'ar da za su tafi sun ware waɗanda kuma za su yi wa amarya rakiya fatin da dangin ango suka shirya da su kai wa laƙabi da *Grooms night*, suna nan an shiga shirye-shiryen tafiya. Na hango amarya shingin ƙiris ta ɗige don azabar kyau, ta ci wani irin kaya, shi ba *less* ba, ba *material* ba, yo ni na kasa gane ko me ye, hatta takalmin kalarsu ɗaya sai gwaggoron mai kalar zaibar kayanta. Kai masha Allah, amarya dai da kyau, ranar auranta.

Takwas da rabi dai-dai aka fara turo motocin ɗaukar waɗanda za su, ba su da wani yawa su ashirin ne kawai. daga shaƙiƙan ƙawaye sai kuma wasu daga cikin yayyanta 'yan gidansu. Kowa ya tafi sai amarya da babbar ƙawarta, inda daga baya angon ya iso cikin *Humer Jeep* ya gigice ganin amaryarsa ita kuma sai wani karairayewa take tana narkwwa, 'yar fara'ar da ya saba gani ma duk babu daya kalleta sai ta wani marairaice. Ya maƙalo hannunta yana shaƙar ƙamshinta ba dan idon Maimuna Nagudu ba da ba abin da zai hana shi matsata. Haka dai ya lallaɓa suka isa motar, har Allah ya kai su *Hotel de Francais* inda za a yi.

Gaskiya biki ya yi biki, 'yan mata ku sha shagali, bikin ya yi armashi matuƙa. Goma da rabi aka watse. amarya ita ta fara tafiya da angonta. Maimakon ya kai ta gida, sai ya wi *branch* a *See Sweet and Bakery* ya haɗe rai ta ce, "Lafiya ni fa na gaji barci nake ji, duk yau ban huta ba." Ya kalleta ta wani masifar haɗe rai, sai ya rage fara'ar fuskarshi ya ce, 'Wai lafiya ne tun da aka fara bikin nan ki ke wani ciccin magani, ko kin ga wani abu da bai gamsar ki ba ne?"

"Ko ɗaya kawai magana ce ba na so, ka kai ni gida na buta."

"In na ƙi fa?"

"Ba lallai, sai na bi motar haya." Ya ƙofula don haushi ya ce, "Baki da hankali ai ke, garin gantalin yawan motar haya ne ai aka kusa cire miki kai." Ba ta ce komai ba, kuma fara'ar da yake nema bai samu ba, ya ce, "Bari na shiga na samo miki *ice cream* da *cake*, don na ga baki ci komai ba gurin *dinner* ɗin." Ta yi saurin cewa, "A'a in don ni ce wallahi ka bari, kafin na fito daga gida sai da na kai linta, ni ba na buƙatar komai sai kwanciya, sai dai kai ko buƙatar ka." Yan da take magana tana basarwa ta ma ƙi ta kalle shi, sai abin ya bashi haushi kawai ya kaɗa kai ya figeta sai gida. Koda ya ajeta bai kula ta ba, sai cewa ya yi, "Komai dai wayon amarya dole wata rana za a sha manta, a juri zuwa rafi wata rana tulu zai fashe."

Ta kalle shi a hankali ta buɗe ƙofar motar ta sauka ta rufe masa ta leƙa ta windo ta yi masa wani shegen kallo ta ce, "*Sorry Oga,* wa ya gaya maka ana fushi da amarya ranar auranta? *See yo, good night, and haɓe a nice dream with me.*" Ba ta jira ya ce komai ba ta wuce gidansu.

Washe gari ranar Juma'a ita ce ranar da ta yi walima da ƙawayenta da 'yan'uwanta da misalin ƙarfe huɗu na yamma, walima da masha Allah an ci kaji an sha su kafirin ɗa, an more 'yan uwa da dangi, ƙawaye duk sun yi kara shi ma taron ya watse lafiya inda kowa ya taho da ledar ko jakar biki da silbeniyos, na bikin, saboda haɗuwa, haɗuwarsu a hoton sai an taaƙa a kan ce kai tubarkallah *nice couple*.

Ranar Asabar, ranar ce da ɗaruruwan al'umar Musulmi suka shaida ɗaurin aurensu, inda *honourable* mai

Dala ya ɗaura auren, Grandikadi na Kano ya wakilci ango. Taron da ya samu halarcin manya da ƙananan mutane, 'yan kasuwa da ma'aikatan gwamnati, lauyoyi ranar su ce, don aƙan idonsu aka ɗaura a kan sadaki naira dubu ashirin da Barista ya biya tun a waccan karo an faɗa jama'a sun shaida.

Bayan dangin ango sun tafi, waɗanda ya rage daga ɓangaren amarya aka goce da fito musu da tuwon shinkafa, waina, sinasir, funkaso, da ruwan lemo. Sai gani kike mutane na saɓe babbar riga ana zuba loma, bayan ka gyatse sai kuma a damƙa maka goro da alewa na shaidar ka halarci ɗaurin auren Sakina da Barista Muttaƙa. Suma taron na su ya watse sumul uban amarya da danginta sai watse baki suke, faɗi suke ku gaida gida mun gode.

Ango bayan sun ja tawargarsu suma ɗin ɗan *reception* suka tafi a can Amir *Place* inda za su ɗan ci abinci ai hirar sada zumunci aga wanda ba a gani ba. Ango can na hango shi baki kamar gonar auduga, ya kasa zaune ya kasa tsaye, an yi masa ƙarin girma, ya tashi daga gwauro ya koma mai daraja mai aure. Can na gano maku su Barista Ibrahim ana wakewa da *pride rice* da *pep-checken* ana korawa da Ziza milk. Taro kam ya yi daɗi ƙwarai yanda ake so ka jiyo mini shewar abokai ciki ya ɗauka an ji wara mai maiƙo da magi.

Yawancin manyan abokanshi sai bayan La'asar suka bar s hi, kowa kuma ya kama gabanshi bayan an yi hotunan tarihi da yawan rai.

LAHADI ita ce *final day*, da duk wani jan rai da wahalarwar da ake ce Barista za dai a bashi matarshi, kuma ita ce ranar da Hajiya ta cakare cikin atamfarta Super, ka ji mai girman ɗata, take ta hidimar bikin autan mazanta

Muttuƙa, badaƙala dai ta ƙare tuwon ne ko rice? Yau za ta sallame shi ya yi gaba can Sharaɗa Kwanar Ganduje, inda ya ɗanɗasa gininshi ɗan ƙaramin gida mai azabar kyau, to Allah ya sa alhairi.

A ɓangaren amarya Amma da Ummi suma dai ƴau ne suke gwangwaje shagalin bikinsu na 'yar 'ya mai rabon ganin baɗi ko mai ta haɗiyo? Matar da ta je ƙanwar lahira ta ga ƙannen azara'ilu ta dawo. Lallai ma gani, ƙila *twin-twince* za ta fara bawa Barista a wata taran farko. Suma an yi cikar mamaki, jama'a sun amsa kira an yi kara sosai, taron ƙuni ya ƙare sumul, jama'ar da ba su zuwa kai amarya suka ragu, yayin da wasu ma sai lokacin suke leƙowa kamar maƙota za a tsegumi, Samira nawa aka jera ko ba hakan ba ne?

Kai Allah dai kai mana mai *nice* gidan amaryar dai amsha Allah, ango ya bugu dangin amarya sun ƙwalu, kowa ya tatse aljihu ya yi kuka, don ƙawata gidan ni wata haɗuwar ma ido kawai nake ba ta. To ban san ko me ye ba, bare na fesa maku, sai dai na ratse *kitchen* inda na lalace don ƙiris ya rage na zaci a *Ceɗi-ceɗi and Sons* nake sai da na ji an rafka guɗa, sannan na farko, abin da na ce, 'Kai Masha Allah, Allah dai nima taimake ni ka ba ni 'yar budurwa man mai albarka, kyakkyawa, ka arzurta ta da miji nagartacce, wanda ya san ciwon kansa. Amin, don Allah kuma ku ce, do ni gidana cike yake da ***president, governor, minister, and commisioners***, ai kun gane ko?

Karfe goma aka kawo Sakina gidan fama, ta tsarkake kanta tun a gida da alwala, don haka cikin tsarki ta shigo da kuma ƙafar dama. Jama'a suka rfka guɗa dangin miji da ke gidan suka tabbatar ta sun ta iso, sai su kai zumbur don girmama ta, da taran *Excellency* kamar yanda Brista ya ce.

Kowa ya yi nasa guri, komai ya yi tsit. Gidan sai ƙamshin sabunta, saboda kaya sabbin ma'aurata. To Allah ya sa a sabunta sabuwar rayuwa mai cike da haske ba duhu.

Barista da 'yan abokansa uku suka rako shi sayan bakin al'ada, sun sayi fuska dai bakin bai samu sayiwuwa ba, amarya ta ƙudundune kuke take yi, kun ji gulma bayan ita ce a da mai ƙarfafawa ogan gwiwa ga kuma reshe ya juye da mujiya? Ai dama haka ne idan giji ta zo kuma sai neman sauƙi yanzun bayani ya rage na Barista.

Ya rasa inda zai sa ranshi, bakin nan wasai yau dai ƙanwa ta kar tsami. Allah ya mallakamar Sakinarshi. Ya yi wa abokan rakiya bayan ɗan shaƙiyancin da aka saba na al'ada, sannan su kai masa fatan alhairi suka tafi.

Ya shigo cikin aminci, inda ya bar ta nan take sai dai ta buɗe fuskarta da gani, kuma ta ci uban kuka. Ya zauna a kusa da ita ya ce, 'Sannu dai Sakina ya gajiya?"

"Lafiya lau." Ya ɗan riƙe hannunsa ta yi saurin janyewa ya yi murmushi ya ce, 'A'a *excellency* har yau ma?" Ta harare shi ya ce, 'Na gane, amma kafin mutattauna tashi mu je mu yi sallar godiyar Allah yau fa kin zama tawa." Da ƙyar ya lallaɓa suka yi sallah an daɗe ana godiya ga Allah da ya kawo wannan rana mai tarin albarka da tarihi.

Komai ya lafa har an sami sake inda ake cin 'yar kazar nan da lemun amarci, ya yi ƙoƙari kwarai wajen hilarta, har ta saki ranta ta tsakuri abin da ya kawo. Suna hira jefi-jefi, har suka gama. Ya ce, 'To ɗan tashi ki yo mini kwalliya da ɗaya daga cikin kayan barcinki musamman wannan jar rigar." Ta ɗan sha kunu, ta ce, "Ni ba zan zo da su ba" Ya share kamar bai gani ba, ya ce, "Ai ko kamar dai na ga an kawo miki akwatunanki bari mu ga." Ya miƙe ya

dumfare su, ya buɗe ya laluɓe rigar, ai ko ya samu mutumin nan ya ɗaukota ya matsa dole aka sa, daga sawar nan ba a ƙare ƙalau ba. Duhu sai na buɗo haske.

Ban muku tsegumi ba, Barista fa da 'yan'uwanshi sun yi ƙoƙari sosai da sosai sun wa Sakina lefe mai kyau daidai su, akwatunta saiti guda-guda da kit, turmin kayanta hamsin cif, su *Super* ne, England, lesis, Galilas, da *materials*, sai mayafai da Undis su ma masha Allah duk *classical* ba na banza. To Allah ya sa rai ya more abinsa. Amin.

Barista Muttaƙa Lawan Kofar Nassarawa, shi ne ɗa na goma sha biyu a gidansu, kuma a cikin maza shi ne ƙarami. Mazansu su takwas ne, matansu su biyar. 'Ya'yan Hajiya Uwa su tara ne, maza bakwai mata biyu, autar ita ce Maryam. Ragowar 'ya'yan huɗu na uwargidanta ne wacce Allah ya yi wa rasuwa da daɗewa, mazan ta uku mace ɗaya, to ga zuriyar gidansu maza ne suka fi yawa.

Alh. Lawan shi ne mahaifinsu mutumin kirki, wanda ya shirya rayuwar gidansa cikin soyayya da aminci, da wayewa, domin wayayyen mutum ne ɗan kasuwa, wanda ya yi kasuwancinsa a ciki da wajen ƙasar, don ita Hajiya Uwa 'yar ƙasar Salo ce, mahaifinta ɗan can ne, kasuwanci ya kai shi garin ya auro ta, ta zo ta zauna cikin aminci a ƙarƙashin jarumar uwargidanta Hajiya Baraka, to da albarkar 'ya'ya sai a kai rayuwa mai inganci mai cike da rufin asiri mai yawa.

Duk 'ya'yansa ba wanda bai yi karatun boko da na Arabi ba, don haka yawancin 'ya'yansa manyan ma'aikatan gwamnati ne. Yaya Musa ne kawai babban ɗan kasuwa a Kwanar Singa, amma yawanci daga *Director*, sai manyan *officers*. Rayuwarsu gwanin sha'awa da zumunci da haɗin

kai mai yawa, ba ruwansu da wani 'yan ubanci ko wani bambanci, to kowa na rayuwarshi cikin rufin asiri ba mai nema gurin wani, sai dai idan hidimarsu ta samu sai su haɗu su rufawa juna asiri, sai ka ga komai a can a can. Kuma komai ɗaya zai godanar 'yan'uwan na sani, tun kafin baban ya rasu ya fito da tsarin mitin duk Lahadin ƙarshen wata, inda dukansu za su haɗu a ci abinci a gaisa da juna, ai hirar zumunci a kuma tattauna matsalolin da ke da akwai.

Wanda yake da matsala a taru a warware ta a cikin gida ba tare da wani ya ji ba. To wannan gini da ya yi har yau bayan ranshi hakan suke yi, shi ya sa aka haɗa ƙarfi da ƙarfe a aurar da Barista, yanzun Maryam ce kawai ta rage auta a gidan ita ma Allah ya ba ta miji na gari. Hajiya kuma ya ja da rai ta ga auran autan mata lafiya, kamar yanda ta ga auran autan maza lafiya.

Da safe misalin bakwai Sakina ce zaune gaban diresin miro tana lakutar mai kamar ba ta so. Barista ya shigo ya dafa kafaɗarta ta wani ƙara marairaicewa, har da 'yan kwalloli a cikin idonta, ya kuma gigicewa.

"*Come one, excellency,* ki daure don Allah ko sallar ne kawai ki yi ni na ɗau nauyin yi miki komai." Ta share kwallar ya ce, "*O'o pls* ki gafarce ni, ni kuma yanzun ai sai kin amince, daure ki tashi ki yi sallar lokaci na tafiya." Ya ringa ƙoƙarin ɗaga ta ɗan tawul ɗin jikinta zai zame ta yi saurin ture shi, ya ko matsa. Ta ja can gefe tana ƙunƙuni, ya yi dariya a ranshi, amma a fili ya ce, "Ban ji ba *excellency.*" Ta haɗa rai.

"Na ce kaya zan sa."

"*Okcy,* to bari na jira dai a waje, wannan ma lokaci ne, wata ran ni za a kira na sa kayan." Ya yi mata gwalo ya yi waje. Ta yi kwafa ta sanya kayanta cikin dauriya da

ƙarfin hali. A ranta ta ce tabɗi wai dama ashe auran bala'i ne? Heye amma ake ta rawar kai an ya zata jure? Jiya ta kusa sheƙawa barzahu, amma duk Allah da ta ringa ambata bai ko ji sau ɗaya ba. Kai lallai Barista mugu ne ashe dama abin da zai mata kenan, shi ya sa idan ya yi mata kyauta ya hana ta godiya wai toshiyar baki ce, dama da sani ai.

Da ta idar da sallah ta ja jiki, kan gado tana can ƙasar zuci ta ji hadari na ihu kafin nan sai ruwa ya gocc mai ƙarfi, sai kawia ta rintse ido, ita ma barci mai ƙarfi ya ɗauketa.

Barista ko na can *kitchen* yana dafa mata ruwan shayi da ƙwai, ya ɗunɗuma mata ragowar kazarta. Sai ya samu tuni ta yi barci, ya kalleta cikin tausayi wani irin so mai yawa ya yi gaba da shi. Sai ya koma da baya a hankali ya juye mata su a cikin *flasks* shi kuma ya karɓi shayi, ya zo ya ratsata ya raɓa ya kwanta shi ma ɗin dai barcin ya yi. Ba su tashi ba sai bayan goma, ko da ta tashi sai ta ji ta samu *relief* sosai a kan da har tana iya haɗa ƙafafunta da kuma walwala ta farka sai ta sa hannu ta bubbuge shi. ya yi firgigit.

"Ya ya *my dear any problem?"*

*"Nothing"* rana ta yi fa, kar kuma mu zo muna yin baƙi a taras ko barcin safe ba mu tashi ba."

Ya bararraje a gadon amarci ya ce, "Akwai mai bin mu bashi ne? Kuma dama wa ke zuwa gidan amarci da safe?" Ya janyo ta.

"To ya kike jin ki yanzun?" Ta hangaɓe, ya ce, "Haba dai kar ki karya mini gwiwa man, *you look freesh* yanda idona ya gani." Ta ɗan harare shi. "Bari ni na shiga *kitchen* tun da kai kana nan." Ya jawo hannunta ta faɗa mai ya ce, "Me za ki yi?" Ta kashe ido.

"Abinci man ko ba ka da buƙata?"

"Na gama miki karin kumallo *excellency*, bari mu je kawai na baki." Cikin shagwaɓa ta ce, "Lah! Ogana kai ne ka yi da kan ka maimakon ka huta?"

"Ke duk aikin da ki kai daran jiya, yau kuma don rashin ga ta da so da tausayi sai a ƙara miki wani? Ai ki bari kawai sai kin dausashe, sai kuma mu yi *handing over.*" Ta sa hannunta buge shi su kai dariya. Shi ɗin ne ya ciyar da ita abincin, har suka ƙoshi, a tare su kai ɗan gyare-gyaren da ba a rasa ba, ya yi kwalliya haka ita ma, sai suka kuna turaren wuta, su kai zaune a falo ta naɗe cikin jikinshi shi kuma ya ci gaba da riritata, suna kallonsu suna hirar soyayarsu. Misalin sha biyu ragowar 'yan biki 'yan gidansu suka fara zuwa, sai ya yi sallama ya fito nemo cefa ne, don yin girkin amarci.

To haka dai suka ringa kwankwaɗar amarci, suna ririta junansu har ba sa son wani abu ya zo ya ratsa su. A hutun amarcinsu ya kai ta gidan Hajiya sau biyu ɗaya da daddare ɗaya kuma wuni guda ta yi, aka ringa zagawa da ita gidan 'yan'uwansa cikin unguwa tana gaida su suna sa albarka, ana lallai Muttaƙa ya yi sa'ar amarya mai kyau, saura kyan hali, shi ma ana fata. Lokacin da ta shiga gidan Anti Hauwa nan ne tafi sakewa, don ta same ta warkan da ita, kuma tun kafin ma ta zo ta sha samun saƙonninta, don haka mafiyawan zama a gidanta ta zauna, sai da Muttaƙan ya dawo suka koma gidan Hajiya a can su kai cimar ɗare shi ma ɗin dai na Hauwa ne.

Rayuwar amarcinsu mai daɗi, har ya gama ɗan hutunshi na amarci ya koma aiki, ita kuma ta ci gaba da zaman gida tun har lokacin ba a gama sassantawa da malaman jami'a da gwamnati bare a janye yajin da suka

daka suna hambuɗa. To Allah ya kyauta.

A wannan lokacin ne barista ya ce, "Ki dai yi addu'a wasu 'yan canjina su gama haɗuwa a samu 'yar ƙaramar mota ko ta ɗari uku a saya kafin ku koma makaranta." Ta ƙanƙame shi cikin jin masifar daɗi. Ta ce, "Ogana anya ba za a takura ba?"

"To me ye *you deserve that*, kuma dole ina da hali haka za a yi saboda dai ba zan juri kai ki makaranta kullum na ɗauko ki ba, saboda ni ɗin mai sabgogi ne, wata rana ma idan na fita sai dare, to wa zai ɗauko ki? Karfina bai kai na aje direba ba, ya ringa mana wannan sintirin, rufin asirina kawai a samu 'yar motar."

Ta ce, "To Allah ya rufa asiri ya bada yanda za a yi. Amin."

To rayuwa tana ta cigaba da tafiya ana ta samun cigaba daga ɓangarori da yawan gaske. Masoyan na daɗa mannewa juna, kullum Barista ya tuna sai ya ƙara godewa Allah da waɗanda suka sace ta su kai sanadin haɗuwarsu har ya ganta ya aureta.

Rannan da ta bashi farin ciki da ya ji daɗi, kawai sai ya burkitata ya ci kwalar rigarta, sai ta ɗaga hannu sama ta langaɓe kai ta ce, "O! Na shiga uku, wane bashin kuma na ci?" Ya yi dariya.

"Kullum zuba miki ido nake yi na ga ranar da za ki biya, amma na ga baki da niyya, to yau ni na tambaya, sai a bani na sha." Ɓuskarta ta nuna yanayin mamaki.

"Me kuma Ogana?"

"Tun sanda muka ƙulle nake baza kunne na ga ranar da za ki bani labarin abin da ya same ki lokacin ɓatanki, amma ban ga alamar hakan daga gare ki ba, ni kuma yau na shirya ji in kuma baki son gaya mini ne to na sani." Ta ja

fasalı ta sauko hannunta ƙasa, ta ce, 'Oh, ni na zaci wata sabuwarce ashe ma ɓacin rai ne, ai fahimta na yi kamar jin zafin abin kake sosai wanda har ba ka maraba da jin labarin, tun da sai ranka sai ya ɓaci kake gwaba mini zanccn, shi ya sa ban yi karmbanin faɗa maka ba, tun da dai ba abin alhairi ba ne."

Ya ce, "Gaskiya ne hasashenki, kullum in na yi niyar tambayarki sai gabana ya yi ta faɗuwa, ni kuma tsoro na ɗaya kar garin bani labari ki gaya mini wani ya cuce ni ya shigar mini gonata, to gani nake wannan zai karya mini zumuɗin da nake yi a kan ki, to shi ya sa nake jan bakina na yi shiru, kar kaza da tone-tone ta tono wuƙar yanka wuyanta."

Ta kalleshi wani iri, "To da kuma ka samun *already* haka ta farun sai ka maida ni gida?"

"Haba-haba dai, haƙuri kawai zan yi na cigaba da sonki da tausayinki don zan gano kin ci azaba ba 'yar kaɗan ba. Kullum kuma na yi sallah na ringa tsinewa wanda ya cucan don ni aka ƙwara. To Allah ya amshi roƙona ya haɗani da salihar mace tsarkakkiya. Um hum! Ina jin ki."

Ta yi shiru lokaci mai tsayi, har kamar ba za ta yi magana ba. Can kuma sai ta muskuta ta ce:

Wata rana, ranar Juma'a da safe, ina kwance na yi juyi na kuma juyawa, raina ne a ɓace, idan na tuna karatu ya taho gangara haka sakin ana neman tauye mu, kan ban da haka na maye aka tsiri wani yajin aiki rana tsaka don kawai a cuce mu? Sati biyu ya rage kawai mu shiga *level 400* don mun yi hutu, mun dawo har an turamu *T.P.* to me kuma ake so? Na ja tsaki na kuma juyawa kawai sai na ji zaman gidan duk ya gundure ni, dan tun da a kai yajin aiki ina gida ban je ko'ina ba, ina ta hutawa to yau hutu na ji duk

ya gundure ni, kawai ai na miƙe tsidik na jawo wayata samfurin L.G. na duba agogo sha ɗaya da kwata, kai tsaye na nufi banɗakinmu, na yi wanka, na shirya tsaf. Na sami Amma na ce mata yau dai zan je gidansu kaftin. Ta kalli aggo, amma dai kin ɗau rana ga shi kuma yau Juma'a ba kya tsoron *go-slow* ɗin 'yan masallaci. Na ce, "Amma kafin ai su fito na kai da sauran lokaci sai dai idan mota na rasa." Ta ce "To Allah ya kiyaye a gaida su Ummanta."

"Za su ji." Na amsa na fito. Ashe tsautsayi ne ya kirani ya fito da ni daga gida, dama mutuwa na yi haka za a ce tana kwance fa ta tsiri tafiyar. To komai da Allah ya ga dama shi yake hukuntawa a kan bayinsa, mu dai na mu miƙa wuya ne kawai da fatan dacewa.

Na fitowaje na shaƙi iskar waje na ji wani sanyi a raina, amma cân ƙasan zuciyata ina jin wata sarewa kamar zan *lossing* ban dai dawo ba na ringa tafiyata a hankali. Har na fito titin Isyaka Rabiu na shallaka a hankali na yi tsaye jiran mota.

Kamar da gayya motar Jakara shiru, ta fito daga dabai mu samu ta tafiya shiru, ga uwar ranar bazara, ga shi ranar Juma'a lokacin huɗowarta. Ina nan tsaye ina raba ido, tsakanin ƙarya da gaskiya sai ga wata *plashing car* ta wuce idona kamar walƙiya na bita da kallo a raina motar ta yi mini sosai kalarta *dark blue, Honda new model.* Na ce kai masu kuɗin nan suna hutawa, to Allah ya ba mu mai albarka na halak. Wallahi kamar ƙiftawa da Bismillah, sai kawai gani na yi motar tana dawowa baya a hankali, na juya baya inga wanda takewa ribas, ban ga kowa ba, ni kuma lokaci ɗaya sai na shiga nutsuwata na ɗauke kai daga kallon ƙurullar da nake mata. Ta yi *parking* daf da ni, gilashin motar ya sauki shuu, wani matashin yaro ne sosai

wanda kuɗi da hutu sun gama huda mishi jikinsa, kyakkyawa mai hasken kala, sai dai ba fari ba ne da gani hutu ne dai. Cikin sanyin murya ya ce, "Assalamu Alaikum." Na kasa ƙin kula shi, na amsa ba yabo ba fallasa. Sai ya ɓalle motar ta shi ya fito hannunshi riƙe da wani ɗan carbi yana ja. Ya matso kusa da ni ya kuma mini sallama, na amsa, ya ce, "Ba ki jin rana madam, ranar fa ta buɗe sosai."

"Eh ina jiran motar Baban kowa ne yanzun zan bar gurin da ikon Allah."

Ya ce, "Haka don Allah idan ban miki shishshigi ba me ye sunanki?" Yana tambayar cikin yalwar fara'a. Na yi ɗan gajeran murmushi na faɗa mishi, shi kuma ya gayan su nansa Falalu. A raina na ce, tabɗi kai daban sunan daban me ye wani Falalu? Hira mai yawa muka yi inda ya gaya mini shi ɗin ɗan kasuwa ne ɗa yake safara tsakanin Kano da Legos, yana kawo kayan da suka samu komai ya zo ƙasa siyarwa muke yi, har ciniki dala ma yi suke na ce, to da ya gama zuƙamin ya ga kamar maganar ba ta gamshe ni ba bare wannan ya ruɗe ni, sai ya ce ina jin dai Sakina kin fahimci abin da ya tsaida ni na ɓata lokaci a nan ko? Kin san 'yan magana na cewa in ka ga kare na shinshinar takalmi ɗauka zai yi, gaskiya sonki nake yi da kuma aure, har na wuce zuciyata ta ringa gaya mini ga matata can uwar 'ya'yana na gano, nan komo da baya. Zancen shi sai ya ban dariya, kai in gajarce maka labari har sai da na bashi kwatancen gidanmu da komai da komai. Ya amince zai zo yau da daddare. Bayan nan ya ce, "Sakina tun da motar nan dai ba ta samu ba, bari kawai na kai ki, sai na zo na wuce masallaci kar na rasa Juma'a."

Na ce, "Wallahi ba komai, kai wuce warka kawai ni

tafiya ta ba mai zafi ba ce Jakara na a cikin gari kawai na nufa." Ya ce, 'Shi kenan ma hanya ta ce, ni ɗin Makwarari zan shiga ba sai kawai na aje ki ba." Na kafe ba na shiga lift, ya kafe sai na shiga a cewarshi wannan ɗin in Allah ya yarda motar mijina ce. To rabon ƙaddara sai kawai na saddaƙar na shiga don kar na ɓata mishi lokacin masallaci. Ina shiga motar wata irin tsigar jiki na ji, amma sai na alaƙanta hakan da sanyin raɓar da na ji a cikin motar ni da na fito daga rana. Ashe abun ba haka ba ne, komai da zai faru lokacin ne ya faru. Ina ji ina gani aka wuce kwanar shiga Jakara aka karya kwanar hanyar maƙabartar ɗan Dolo, a kai cikin unguwar Tudun Yola daga nan aka ɗau hanyar Kauyan Bajallabe, to daga nan ne kuma na rasa saiti komai da za a yi ban sani ba, ban kuma sanin ba, sai l okacin da na farko daga barcin dole zan yi juyi a tunanina ina kan gadon Amma ne sai na ji ni a tsandaurin sumunti, nan da nan tunanina ya dawo na buɗe ido da sauri, sai gani na na yi a wani ɗaki ni da wasu yara ƙanana uku da wata mata mai goyo sun tsura mini ido.

Gabana ya yi wata irin mummunar faɗuwa, don tsabar mamaki na tashi da sauri na ce, "Ina ne nan?" Yaran suka fashe da kuka, cewa suke Anti ki kai mu gidanmu za su kashe mu sun kashe baby. Kai ba sai na yi wata zanbarma ba, kalamansu sun dawo da ni nutsuwa sosai, na fashe da wani irin kuka na tsananin tsoro da nadama, amma lokaci ɗaya na toshe bakina, hawaye ne kawai ya ke ta zubowa, na yi kuka, kuka mai isa ta, har ina jin kuma na sare garama kawai na yi shiru na kuma zuba ido na jira hukuncin Allah mai girma.

Mu kai wuƙi-wuƙi da mu har lokacin da dare ya raba ni da matar nan ne kawai ba mu yi barci ba, ni tunani

nake ita kuma tana ta ƙoƙarin jijjiga yarinyarta da ke son yin rigima, don ma 'yar mai tsananin haƙuri ce, ban ji ta ce komai ba, tun da na zo, sai ko yanzun illa dai maƙale take da nonon uwar rai-da-rai tana tsotsa uwar ta yi wani irin fita daga hayyacinta. Ina tausayin kaina amma tausayin matar nan da yaran nan ya kashe ni kawai. Kai lallai lahira da kallo, irin wannan rashin imani ƙarara?

Na muskuta ina ta kallonta har 'yar ta samu ta yi barci akan zanin goyansu ta yi ajiyar zuciya mai ƙarfi, sai kuma ta matsa gefe ta jingina da bango ta runtse ido, ina ganin laɓɓan bakinta na fahimci addu'a take yi. Wannan sai ya tunasar da ni addu'a, ni da nake da yawan addu'a, amma bala'i ya buga mini kai na manta da komai.

Cikin sanyin murya na ce, "Ke kin daɗe a nan ne?" Ta ɗago kai ta buɗe ido karo na farko da mu kai magana tun da nan dira a gidan. Ta ja fasali ta ce, "Yau kwanana huɗu da shigowa gidan nan, kuma a cikin kwanakin a ɗauke mutum huɗu an fita da su ba a dawo da su ba, ciki har da 'yar yarinyar da aka sato waɗannan yaran tare da su. Mu kam muna cikin bala'i ne babba, ƙila kwanakinmu ya ƙare, ƙila kuma taimakon Allah da Rahamarsa su sauka ta inda ba mu zata ba, wannan ikon ne, ga Allah idan ya ga dama zai yi yanda yake so." Na gyaɗa kai na yarda da duk abin da ta ce. Na ce, "Ke ɗin waye ya kawo ki?" Ta ringa girgiza kai tana hawaye, tabbas abin da za ta faɗa mai ciwo ne. Ta ce, "Hmn! Ni ɗin mutuniyar Katsina ce, amma ina zaune a nan Kano, saboda karatu da nake yi nan Kabuga daf gidan Biredin Kowa na So. Jin da na yi an ce ana yawan sace-sace a Kano, kuma an fi samun hakan ta hanyar shiga *taxi*, gaskiya sai idan ta yi masifar ƙure mini ne zan hau ko kuma idan mu ɗin muna da yawa, in ba haka ba sai

dai na hau bus, máshin ko Adaidaita Sahu.

Yawancin lokuta kana gudun ƙaddarar ka guzuri kake yi na taratta, kai ba ka sani ba. Rannan na fito daga makaranta na tsaida bus wata kwararraɓaɓɓiya, na ce musu asibiti a ciki da maza biyu da kuma wata 'yar dattijuwa, don haka hankali kwance na s higa, ina ta kalle-kallen waje, don hankalina baya cikin motar tun da ni a gindin taga nake, ni ban aune ba sai ji na yi wani abu ya daki kaina kafin in tantance kome ye ke faruwa, ni dai sai buɗe ido na yi na ganni a nan a yashe da yarinyata a gefe." Ta share hawayenta. Na ce, 'Oh! Mu mun shiga uku bayin Allah, a rayuwar yau ina mutum zai fake ne ya ce ya tsira? A da can san ɓarayin mota kala ce da su ƙila da ka gani ka gane, amma yanzun abun ya canza salo, duk inda kuke tunanin za su ɓullo muku to suma sun gane sai su kauce inda kuma duk kuke tunanin kun kuɓuce nan ne nkuma matattararsu. Ya Allah ka kuɓutar da waɗanda ba su ji ba, ba su gani ba, Allah ka bankaɗe asirin tsinannu, irin wannan bala'i haka kawai ṡaboda ŋeman duniya. To bayan an samu kuma sai me? Mutane ba sa tsoron Mahaliccinsu?

To haka muka kasance da matar nan muna bayyanawa juna abin da ke da akwai. Goshin Asuba barci ya yi gaba da mu a zaunen nan, na yi mafarki da Baba da Amma suna gaya min in ta karanta La'ila ha'illa anta subhanaka innikuntu minazzalimin. Allah ya yi gaskiya. Na ko farka firgigit hasken rana ya fara hudowa. A raina na ce, ta ina mutum zai yi sallah, ba ruwa, ba kyakkyawan muhalli, amma wannan ba uziri ba ne. Kawai sai na kintaci gabas na ringa shafar bango ina sallah. Matar nan ta ce, "Kin ko kawo dabara ni ai da na hakura ne." Na ce wannan ba uzuri ba ne, tun da Allah ya ce bai ɗauke sallah ba a

lokacin da ake tsananin gwabza yaƙi, cewa ya yi rabi su sallah raka'a ɗaya, rabi su yi gadinsu, sai su kuma rabin su koma su sallaci ta su sallah, saboda kar su ɗunguma su duka ana yin sallah abokan gaba su far musu. To mutumin da ke cikin wannan sammatsin ba a ɗauke masa sallah ba. To waye kuma za a ɗaukewa? Don haka sallarmu kawai za mu yi. Ta ce to. Har yaran duk mun yi sallah da su, mu kai da'ira muna ta addu'a, La'ilaha illa'anta ce muke ba adadi. Mun yi Falaƙi da Nasi, sun yi dubu. Haka Ayatul Kursiyyu, muna neman tsarin Allah daga sharrinsu, muna masu miƙa wuya kuma muna masu kwaɗayin rahamar Allah ta sauka gare mu. Mun yi tsaka da addu'a matar ta kallan ta ce, "Zuwanki ya kawo cigaba da yawa, tun da na zo nan cikin tsananin tsoro nake da ruɗani, amma yanzun zuciya ta dake ƙata nake idan zan gamu da Allah na gamu da shi ina Musulma, mai tsananin tsoransa da kwaɗayin rahamarsa. Na ce haka Allah ya sa mu cika da imani, amin.

An sami misalin goman safe, sai ji kake kiririf, ana shirin buɗe ƙofa. Cikina ya bada wani irin sauti na tsananin fargaba, to ta mu ta ƙare daga ni har su muka kalli ƙofar cikin tsananin tashin hankali. Wani gabjejen ƙato ne ya shigo, hannunsa riƙe da kwanon ya kallemu kallon wulaƙancin da rashin imani, ya ce. "Me ye wani ku ka zuran ido? Idan lokacin yanka ku ya yi za ku hana ni ne?" Sai kawai na ji zuciyata ta ɗake, na wurga idona cikin nasa na kafe shi da su ɗodi nake.

'Allahumma inna naj'aluka fi nuhuri him, wana uzubika min shururihimi" Ya yi ta kallona ina kallonsa kawai sai ya dangwarar da samira ya juya bai kuma cewa komai ba. Kawai sai na ga yaran sun matso jikinsu na ta rawa za su buɗe. Kun san sanda na daka musu tsawa ba.

Matar mai suna Fatima ta kallan ta yi murmushi ta ce, "Ki ƙyale su, abinci ne ake kawo mana shi." Na ce sai ku ci?

"To ya za mu yi tun da da sauran kwananmu ai dole muna nda buƙata." Na jawo abincin na buɗe taliya ce jalof, cikin samirar. Na sata gaba ina ta mata tofi duk abin da ya samu na iya dangane da addu'ar neman tsari, suma na ce musu kowa ya karanta Kulhuwa, Falaki, Nasi, Li'ilafi da Ayatul Kursiyyu, sannan ai Basmala kafin a ci, su kai kuwa suka sa abincin gaba suka fara ci. Fatima ta ce, "Ba za ki ci ba?" Na gyaɗa kai. Ta yi murmushin yaƙe ta ce, "Ki yi haƙuri ki daure, don ke ɗin ai ba sani ki kai ba na ranar da za ki bar gurin, kuma abincin dole ne inda kana rayuwa lafiya da numfashi. Na ce, "Haka ne, ku dai ku ci kawai, ke ɗin ai ko dan buƙatar yarinyarki mai shan nono." Ta juya ta kama ci ba ta kuma cewa komai ba. Na jingina da bango na rintse ido na ringa halarto Ubangijina kawai. Wallahi mantawa na yi da duk wani wanda na sani, wuya ta yi wuya.

An samu kwana uku ana mana haka ba mai kulamu sai ran da za a kawo abinci, idan an tafi kai ka ce ba wani ɗan adam mai lumfashi a cikin gidan. Ni kuma na kai matuƙar galabaita yunwa da ƙishirwa, na neman halaka ni. Rannan dai da aka kawo abincin na kalli ƙaton na ce, 'Don Allah ruwa " Ya wani tsare ni da ido, nima na kafe shi da shi. Ina ta addu'a mai kuma ya tona sai ya juya ya fita, can kamar ba zai dawo ba sai gashi ya kawo cikin ɗan bokitin fenti, na damƙi ruwan nan na sha na sha, haka suma suka sha 'yar yarinyarta Ummi aka ba ta ta moɗa, duk sai mu kai gefe muna maida numfashin azaba, sai da muka huta sosai, nima dai ranar na yi shahada na ci abincin kamar yanda Fatima ke mini na ci bayan na tufe shi da addu;'a kamar

yanda nake musu kullum.

Wurin misalin huɗu na yamma, Sadiƙ da Halifa da Umar suna rakuɓe a kusa da ni, Ummi ta ringa wani irin kuka mai ban tausayi, Fatima duk ta daɗa gigicewa tana ta safe da marwa tana jijjigata, amma yarinyar ta ƙi shiru, duk ma wani motsi da a kai sai ta kuma buɗe wuta, ba uwar ba, har mu mun tsure na ce ta saukota, ta sauko ta na karɓeta na sata kafaɗata ina jijjiga ta. Ina! Sai na saukota kan cinyata ina karanta mata abin da ya sauwaƙa daga Alƙur'ani, maimakon ta yi kukan sai kuma wata irin shaƙuwa ƙut-ƙut, duk sai muka daɗa gigicewa, to abin ne Allah cuta, Allah magani, kar mu cika motsi kuma a zo a ci kwalarmu, ga kuma cuta ina za mu yi?

Uwar addu'a haka nima, sai ta ware ido ta ja ajiyar zuciya mai tsayi, sai ta lumshe ido barci ya ɗauketa, mu duk muka maida ajiyar zuciya. Fatima ta yi gajeran murmushi ta ce, 'Wai yau mun ga idi." Na ce, "Umh! Ke dai, Allah dai ya taimaka ta samu barci, ina jin tausayinta ina tausayawa kan mu." Ta ce, "Haka ne na gode Sakina."

"Kar ki damu yiwa kai ne, ni da ke ai duk ɗaya ne."

Ta amshe ta ta kwantar kan ɗan zanin goyansu, na matsa gaba na jingina da bango ina abun da zai fisshe mu. An fi awa uku, Fatima ta ce, "Kin ga Sakina, anya ko yarinyar nan da ranta?" Gabana ya yi wata irin faɗuwa matsananciya, na matso ina kallonta kamar yanda take yi, nima sai na ga komai na ta ya saki kamar ba ta numfashi, na ɗaga hannunta sai ya biyo ni da sauri na ware idonta shi ma ko motsi. na ji wani dom a raina na runtse ido na yi shiru. sai hawaye ne yake zuba. Ta yi ta kallona, ina buɗe ido ga mamakina sai na ga murmushi take. Ta ce, "Tafa mutun ko?" Ban ce komai ba. Ta ce, "Na sani tun ɗazu na

dai gaya miki ne don ki tayani tabbatarwa, to ni ba abin da zan cewa Allah sai in ta gode masa ina ƙarawa, na san ya amsa mini addu'ata, tun da na shigo gidan nan na ɗaga hannu na roƙe shi cewa idan ya ƙaddari ƙarar kwananmu ni da Ummi nan gidan to ya kashe mu cikin suttura ba tare da waɗannan azzaluman sun cutar da gangar jikinmu ba. Allah ya amsa tun da ya karɓi Ummi a gaban idona ba tare da an rabata da ni ba, ina ji ina gani an kcta mini ita, ko kuma ni a ɗauke ni a barta ina kallo. To mai abun ya karɓi abarsa cikin suttura, mu kuma sauran mu ya kashe mu cikin imani da suttura."

Kuka nake yi sosai da a ce ruwan ido na ƙarewa da dai zuwa yanzun ruwan namu idon ya gama ƙarewa, saboda azabar kuka. Ta lulluɓeta tana mai shafa fuskarta.

"Ummi Allah ya jiƙan ki da Rahamarsa mayalwaciya, mu ma tafe muke da izinin Allah. Allah ya suturce miki gangar jikinki kar ta tozarta, Allah na gode maka kai mini baiwa a lokacin da nake ƙishirwar samu, ka kuma karɓi abinka lokacin da ya dace. Ummi na same ta ne a lokacin da nake cikin shekara ta goma sha ɗaya da aure. A lokacin da takaici da gore-gore su kai mini yawa na naƙi haihuwa tun daga miji na har zuwa 'yan'uwansa wanda ya tilasta mini barin Katsina bisa yardarsa na taho Kano neman karatu. Ina shekara ta biyu a makaranta Allah ya bani cikin ta, yanzun gab nake da kammala karatuna ita kuma ta shiga cikin shekara ɗayar farko a irin lokacin da iyaye, 'ya'ya ke s higa ransu sun fara gane yawancin abubuwa, sun fara takawa ana ta gwalan-gwalanton magana gwanin sha'awa to sai ga shi kuma abin da Allah ya yi mana."

Na ce, 'Haka Maman Ummi ki yi haƙuri an taɓa

ranki." Ta ce, 'Wallahi ko ɗaya ba na tare da ɗamuwa, hakan da Allah ya yi mini babbar rahama ce." Na gyaɗa kai. Ka ji fa uwar da aka karɓe mata 'ya take farin ciki daga baki har zuci, lallai wahala ta yi wahala. Allah kasa mu dace, amin.

Haka muka tusa gawar Ummi muna kallo, ranar dai ba wanda ya runtsa har yaran mun zama abin tausayi kwarai ainun, lokacin ba mu abinci ya yi. Wannan gabjejen ƙaton da yake kawo mana abinci ya shigo ɗauke da abincin, shi da kansa ya gane akwai sauyi sosai a tare da mu, ya kalle mu da muguwar fuskar nan tashi ɗaya bayan ɗaya, har idonshi ya kai ga Ummi da ke ƙudundune cikin zanin goyanta ba ƙofar da za ta iya shaƙar numfashi, ga yanayi na uban-uban zafi. Ya tsaya jim can ya ce, "Wannan fa da aka ƙudundune ku ka sa gaba?" Ba wanda ya yi magana sai ni na ce, "Ta mutu ne?" Shi kan shi kalmar ta buge shi sosai, don yanda ya nuna ya dawo ya tsugunnaya buɗe fuskar yarinyar kamar mai barci. Ya mayar ya rufe ya miƙe zai fita na yi karaf na ce, "Don Allah ka taimake mu tun da dai ta zama mushe kar ku cutar da ita ka haƙa mata rami ka ɓinne ta." Ya zuba mini shegun idanunsa, zuciyata ta ringa bugawa ina fargabar abin da zai mini, amma a zuciyata addu'a kawai nake yi bai ce komai ba, ya kaɗa kai ya yi gaba.

Fatima ta ce, "Ina jiye miki sharrin mutanan nan fa, ki daina yawan magana da su, kin ga ke budurwa ce, za su iya amfani da wannan abin su cutar da ke." Na ce, "To ya za mu yi Faty, zan kuɓucewa ƙaddara ta ne? Ni da ke cikin komin su? Amma Allah yana ji yana gani, komai da yake gudana a doran ƙasa."

Ya tafi sham har kamar ba zai kuma waiwayarmu

ba. Bayan Azahar ana zuga uwar rana, ya shigo ya kama mu ni da Fati ya ƙulle mana hannaye da baki ya hankaɗa ƙeyarmu ya sunkuci Ummi, sai yaran suka fashe da wani irin kuka mai ban tausayi, ya maida ƙofa garam ya kulle, ya ce mu yi gaba tsayin katangar gidan, haka muka ringa tafiya idanunmu sun yi rauni sosai, saboda rana mu kuma ba ganinta muke ba, tun da muka shiga gidan.

Can bayan gidan ya yi da mu tafiya sosai gidan babba ne. Gidan gona ne irin kallon da mutane suke masa, amma ashe da wata manufa a ƙarƙashinsa. Muka sami wani guri ya tsaya ya sauke Ummi, sai ya janye wani kwali, ashe ko rami ne ya haƙa, ya ɗauki Ummi har zanin goyanta muna gani ya turata, ya sanya ƙasa ya ringa rufeta har sai da ta rufu ruf, ina ganin uwar ana fara zuba mata ƙasa ta runtse idonta hawaye ya zubo mata. Bai ce mana cikan ku ba, ya tiso mu gaba ya hankaɗo mu ɗakin da muke, ya cire mana abin da ya ƙuƙƙulle mu, ya yi gaba.

Wannan ya nuna baya buƙatar maganarmu yana fargabar kar mu yi wani yunƙuri, amma mu ai ya yi mana Haji da Umara ai.

Kwananmu tara, aka ƙaro wasu yara su biyu duk mata. A lokacin ne suka shigo da wai da shi suke kira Oga. Na yi tsaye baki buɗe inan kallon Ogan, kai duniya! Hmm! Kyakkyawan mutum, Bafullace sosai, wanda zai gaza shekaru arba'in a yanayinsa ya fi kama da liman ba wai ɗan ta'adda ba, ashe shi ne Ogan. Ya ƙare mana kallo ya kafe idonshi a kaina ya tambaye su wannan fa wa ya kawo ta? Ya ce, 'Ai ita ce ta gurin Falalu, waccan matar kuma ita ce Oska ya kawo, wannan yaran kuma ni na kawo su su uku ai ka sani. ɗayar an yi amfani da ita da su Alhaji Zarai suna buƙata." Ya gyaɗa kai.

"Okey, a cigaba da riƙe su ga wasu na hađo daga a Jos da na je na taho da su, cikin satin nan za a bukaci kuđi sosai, ku ma kuma za a ganku." Suka tafa sosai, đaya yaron ya ce, 'Ka ce za mu yi iyo a ruwa a gari, mu sha ruwa mu kwanta cikin ruwa, a lulluɓemu da yayyafin ruwa." "Sosai ma, su Ladi za su fantama ai." Suka ƙyalƙyale da dariya, ya matso sosai gabana yana mini wani duban ƙanƙanci na sha'awa, ya kai hannu ya shafi kuncina ya ce, "*Yah baby how far?"* Yana rufe baki, hannuna ya yi kwanciyar ruwan zafi a fuskarshi, ji ka ke kaukau! Har sau uku, abin ka da farin mutum sai gurin ya yi ja. Ba shi ba, ba yaransa ba har irinmu sai suka buđe baki ba su taɓa zaton zan iya wannan ƙarfin halin ba, nima ban zaci hakan ba, kawai ji na yi ina yi.

Ya dafe kunci, yana mini wani irin kallo. Đaya daga cikin yaran ya iso da gudu ya damƙe ni ya bani kyakkyawan mari guda biyu, zai mini naushi, shi ogan ya janye shi ya ce, "Kyale ta, ƙyale ta, kawai ku shirya mini ita zan đan huta da ita, wannan shi ne kawai zan huce, amma ku tafi da ita ku rage mata gashin kanta, idan na gama ganawa ta zan zo." Kan ka ce me? Sai aka mini wata irin damƙa, na saki fitsari da wata irin ƙara, saboda tsananin azaba.

Haka aka tankađa ni suka biyo bayana. A cikin gidan a kai wani loko da ni aka kai ni gurin aski, abin *barber* ne sosai, irin wanda ake aski, shi aka mini ƙwalƙwal ina ji ina gani. Đayan ya ce kawai a aske ragowar đayan ya ce a'a, kasan dai Ogan maye ne kamar đan bunsuru, ya fi son ya ringa ganin đan duhu-duhun, ji fa wannan yarinyar da muka aske mata ba fađa ya yi ta yi ba, yana ta sakin maganganu? Su kai dariya suka tafa. Sai suka fita suka

nuna mini banɗaki wai na yi wanka na gyara kaina kar Ogansu ya ji tsami. Ban ƙi ta su ba, nima ko don na sami sa'ida na yi wanka, na ɗauro alwala na yi sallah, ina ta kuka ina gayawa Allah ya dube mu ni da jama'ar da aka sato ya tsare mu. Amin.

Na idar na zauna ina ta raba ido ni ɗaya da solin kaina, ina fargabar abin da zai faru *next.* Ba a neme ni ba har tsayin daren ranar. Sai dai wajen tara an kawo shayi da biredi na kuma sha soisai bayan na yi addu'a, suka ƒice, na sa sakatu na zauna jiran tsammani. Ni da ke wannan mataki na ƙarshe a rayuwa, zugun ɗin da na yi sai ya bawa barci damar sace ni. Tabɗi! Barci na yi sosai har Assalatu na farka ƒirgigit, ni kaina na yi mamakin barcin na share miyan barci na faɗa banɗaki na yi alwala na yi sallah, na san hakan baya rasa nasaba da wanka da ɗan ɗan *tea* da na sha.

Ina zaune har wurin sha biyu wannan ƙaton da yake kawo mini abinci ya shigo, amma hannunshi baya ɗauke da komai, ga mamakina sai ya zauna dab da kujerar da nake zauna ina jiyo wani masifaffan tashin warinsa, sai ya yi ɗan murmushi ya ce, *"Baby you are so beautiful* fa." Ganin da na yi jiya ban ji da daɗi ba, sai kawai babara ta ƒaɗo mini gara na yaudare su ko hakan ya zame mini mafaka ta samun tsira. Na yi ɗan murmushi na kashe ido na ce, 'A hakan duk kun tsotse ni?" Sai ya wani wangale baki ya ce, "Haba dai ai kin san dai na ganki tun zuwanki ko? Kuma ma yanzun ai yana nan rashin kula ne, baki gane har Oga jiya ya yaba ba? Yanzun ma shi ya turo ni ya ce in je masa da ke, amma ni alfarmar da nake nema idan ya ci ya rage dan Allah ki yi mini alfarma nima ki ɗan sam mini, kuma ki kwantar da hankalinki duk abin da Oga ya nema ki bashi ina mai tabbatar miki in dai ya samu abin da yake so sakin ki zai yi,

kuma ko shi ɗin bai yi hakan ba ni na yi miki alƙawarin zan ƙyale ki ki gudu a lokacin da basa gidan saboda ni ɗin ni ne mai kula da gidan nan, makullan ko'ina a hannuna suke, muma da muke zaune ciki ba wai ɗan san mu ba ne, kawai don ba yanda za mu yi ne."

Na ce, "Haba dai kamar ya ya? Kai da ba kullcka a kai ba, kana da damar da za ka gudu?" Ya girgiza kai ya ce, "In ma na gudu ina za ni? A cikin gari ni ɗin ai mai laifi ne, wannan ita ce babbar katanga da ba za ta bari a ganmu ba, bare a kama mu, don masu gidan su ne da garin ta kowacce fuska mu ɗin daga 'yan sace-sace na unguwa aka kawo mu nan, aka jibge dole ba don mun so ba muke bin umarnin don rana zafi inuwa ƙuna ne.

Talaka gatanshi kawai Allah ne, zafin talauci, rashin ilimi, rashin gata, ƙarancin ci da sha, shi ya assasa wa iyayenmu sakin mu uwa tumaki, ya zama kawai ana rayuwa irin ta 'yan marina kowa da inda yake fuskanta, mu ba su ba ne gabanmu don ba abin da za mu kalla mu ji daɗi daga gare su, sai dai ya taɓa mana zuciya, haka suma ɗin mu ba abin kallo ba ne gare su mun zame musu *liability*, kullum kuma sai ɗaukƙo musu magana muke yi. To wannan ne ya sa mu gara ramɓa, tsakanin ƙarya da gaskiya. Rayuwa ta yi wa talaka karan tsaye, shiwagabanninmu sai Allah ya yi musu kamun kazar-kuku, abubuwa da yawa akwai sakaci da son zuciya, kan su kawai suke da niyyar bautawa, amma ba wai al'umma ba, saɓanin 'yan mazan jiya da suka gaba mu, irin su Sardauna, Tafawa Balewa, Malam Aminu Kano, Gambo Sawaba, Sabo Bakin Zuwo, Wada Nas, Mal Lawan Mai Turare, haƙiƙa sun bautawa ƙasarsu da r..u da jikkonansu, masu arzikin cikinsu sun bautawa har da aljihunansu, amma na yanzu fa *common consider* idan ka

ga bujimayen da ya ɗaure abin zai ba ku mamaki *out of his salary."*

Na gyaɗa kai na ce, "Wannan kuma ai ba dabara ba ce, duk rashin tawakali ne da karɓar ƙaddara da kuma rashin mai da dukan al'amura gare shi, falalar Allah tana da iyaka ne? Wani abun sai bayan an haifi jikokin mutum za a kuma samun shi na daga falalar Ubangiji, to don me mutum zai haƙura ya zauna sai wani ya ba shi? Ku ji tsoron Allah, akwai mutuwa, akwai kwanciyar kabari, akwai kuma hisabi, wannan babu fashih ko kaɗan. Gani muke uwa ƙarya kamar abun ba zai faru ba."

Ya gyaɗa kai, "Haka ne, to muna nan muna neman shiriyar Allah." Na ce, 'Wallahi ba ku nema, domin zama ku kai har sai Allah ya shirye ku. Me Malam mai Ahalari ya ce, yana daga alamar rashin arziki da taɓewa da damsil basirati." Ya miƙe da sauri, "To Sayyada za a yi ne, yanzun dai ki zo mu je gun Oga yana jira, kuma kar ki yi masa gardama, abun da duk ya nema ki bashi, in Allah ya yarda za ki bar gidan nan. Ni ɗin ma na haƙura da suɗin da na nema." Ban ce komai ba na miƙe, ya tusa ni gaba mu kai can bayan gidan wani *build...g* ne mai kyau, kamar gida guda muka shiga ciki nan zauna a falo, shi kuma ya shiga ciki gurin Ogan.

7 Na kalli ƙofar falon ta *glass* ce akwai makullinta a jiki, ta waje kuma akwai *padlock*, a jiki an dai saƙale tun da ƙofar buɗe take, guda biyu. Na ɗan yi jim nan ji ba su da alamar fitowa na tashi sadaf da sa... ...makullin na kwashe wayar Ogan, na fice na sa masa makullin, na kulle su na sarƙafe su da duk *padlock* din, na sheƙa a guje na kaina ban san inda na nufa ba, saboda girman gonar na kuma sanin kanta na yi ba, kawai sai na gani ƙofar ɗakin da

aka fito da mu, shi ɗin na ganc shi tun da na fito har sau biyu, har na gota na dawo da baya ankwacc saƙalc a bayan aka sarƙafa, cikin hukuncin Ubangiji ba a datse da kwaɗo ba, na ware ta da sauri, a nufina duk mu kuɓuta, ko kuma dai wasu daga cikinmu wanda Allah ya nufa.

Suka min caa da ido, ina haki na ce. "Duk ku fito kowa tasa ta fishshe shi, amma a nutse don haka. Mu kai wani gu a nutse cikin sanɗa da ƙarfin Allah, ashe gun ƙofar muka nufa babban *get*, an kukkullc da kuba ta ciki, muka zare a hankali mu kai waje da gudu, bayan mun sarƙafe su ba kwaɗo. Na ce, "To kowa fa tasa ta fishsheshi, da daban-daban muka zo don haka kowa ya yi ta kansa. Na sani kawai Ubangiji ne ya amshi addu'armu ya kuɓutar da mu daga wannan masifa, amma ya ya su da suke wannan mugun aiki za su yi sakaci har mu rai takwas mu gudu? Allah kenan, shi ne ya shirya komai ba wai iyawarmu ba, girman gidan gonar nan ya isa, ana kiwon dabbobi da mutane. A saida mutum, a saida dabba.

Muka runtuma a guje gabas, gudu muke har ba mu san inda za mu ba. Mun yi gudu a ƙallah na minti arba'in ba ko hutawa, kuma duk tare muke, sai Khalifa, ɗaya daga cikin yaran nan kawai sai ya ci da baka ya faɗi, ni ce a gaban su sai na tsaya na ɗaga shi, ya kalleni har yana numfashi sama-sama, ragowar ai ba su tsaya ba, gaba su kai, na waiwaya gaba, na waiwaya baya na ce, "Daure ka tashi kawai ba gurin tsayuwa ba ne nan." Ya yi shiru yana fidda numfashi ta hanci, ta baki. Ai kawai sai ji mu kai ɗin-ɗin ana *born*. kafin na juya tuni Khalifa ya rigani da ka tsalle ya figa a guje, nima sai na runtuma ban ko tsaya ba, muka nausa. To ka ji rabuwarmu da su. Ina wannan gudun ne, ban kuma san mai ya kuma faruwa da ni ba, sai da na

ɓuɗe idona na gan ku. To ka ji."

Barista ya ja doguwar ajiyar zuciya ya ce, "Tabɗi! Lallai kun tsallc rijiya da baya, kuma ke ɗin sai kika zama rahama gare su, don an yi amfani da ke ne, wajen kuɓutar da su, idan har sun sami nasarar hakan. Ko ya tasu ta kasance? Allah masani, to Allah ya cigaba da tsaremu lafiyarmu da imaninmu, ya cigaba da tsare mu daga sharrin duk abin da ya halitta. Amin. Amma dai ni ai ni a kaiwa wannan hidima, ƙila da hakan ba ta faru ba da abn da hanyar ganinki har na kwashi wannan roman." Ta doki kafaɗarshi ta ce, "Ko?" Ya gyaɗa mata kai cikin wani shauƙi, ta ƙara matsawa kusa da shi, ya amsheta suka kasance cikin aminci da rahamar Allah mai yawa.

Rayuwa ta yi musu yanda suke so, har 'yan canjin sun samu. An siyo mata mota takumbo *Honda Civic*, mai kyau kalar ja. Ta yi tsallc ta yi murna sosai, ta yi godiya, ya dungureta ya ce, "Da'allah ja can kin cika ni da hayaniya kina nufin wannan ce godiyar?" Ta riƙe ƙugu ta ce, "Haba nawa share kawai, ka dai bari ni idan na ringa maka godiya yau sai ka gudu bari dai duhu ya shigo, za ka sha mamaki." Ya yi dariya ya kwantar da kai a jikin kujera yana shafa ƙirji cike da tsananin jin daɗi. "Aure rahamar Allah."

Shi ne da kan shi idan ya sami lokaci sukan fita da yamma, ko wataran da safe ya je yana koya mata a *Civic Center*. Mai hazaƙa ce, kafin cikar wata ɗaya sai gata an bata mota tana ja a hankali shi kuma yana gefe. Kafin wani lokaci hannu ya faɗa sosai, sai fatan Allah ya tsare. Amin.

Ba ɗaɗewa kuwa aka sasanta da gwamnati da hukumar jami'oi ta kasa suka koma bakin aiki, inda kawai kawayenta sai ganinta su kai da amaryarta, ana ta kallonta ana sha'awa da mata fatan alhairi, domin ita a yajin aikin

nan da ya faru abubuwa da yawa sun faru garcta, wani na dadi, wani akasin hakan. Haka daɪna rayuwa ta gada.

To haka abun ya kasance, ta maida hankali kwarai kan karatu da hidimar mijinta, rayuwarsu mai sanyin dadi da ban sha'awa, wane-na-wane-wane.

Cikin watanta na tara da aure ciki ya samu a lokacin kuma tana gab da kammala karatu ga ciki mai azabar laulayin tsiya, amma a haka ta ringa maganin rayuwarta, tare da kwarin gwiwar mijinta, iyayenta da surukarta. Ta rike Hajiya da kyau suna son juna, suna mutunta junansu, abun da duk ya kamata uwa ta yi wa 'yarta Hajiya na yi wa Sakina, haka Sakina na iyakar iyawarta. Lokuta da yawa tafi son zuwa gidan Hajiya fiye da gidansu, don Hajiya na tattalata, komai ta yi sai a ce me take so, me za a kawo mata, har hakan na sata tunanin wai to me yake haddasa bala'i tsakanin uwar miji da suruka? A ganinta idan har kowa ya san matsayinsa ya kuma kare kimarshi to na maye abin jarabar? *A times* zaman tare na haifar da hakan. To koma dai mene ne sai a ringa sanya tsoron Allah wanda zai zama tsani a kan dukkan abubuwan da za mu yi a rayuwa, sai ku ga mun zama masu saiti a dabi'u da halaiyarmu.

Ta gama karatu da nasara ta dawo zaman gida, ciwo kuma ya ce salamu Alaikum, na ji dare, har ba ta iya hassalawa kanta komai, abinci ma ba ta jin dadinsa a yawancin lokuta lemon zaki shi ne kawai yafi kwanta mata idan har ta sha. Wannan ya kawo wani gagarumin canji a rayuwar aurensu.

***

Yau Litinin da misalin hudun rana Sakina na ta malelekuwa a kasan *tiles* dinta na tsakar daki, komai na duniya ya yi mata duhu, ga tsabar yunwa, kadaici, rashin

lafiya ga damuwa. Yau duka tun da Barista ya fita ba ta hassalawa kanta komai ba ban da kwanciya. Ta runtse ido hawaye ya zubo mata, damuwa ce sosai, ciwo ya isheta mijin da suka dama furar tare ya barta sai ita ɗaya take shanyewa, 'yar wayar ɗa ya saba yowa ya ji ya take, ya ɗauke wuta, taimakon shi take so babu. Ita ga ta saboda yanayi na karatun da ta kasance bai bari ta san maƙotanta ba, bare har ta yi wata mu'amala da su bare su saba. Don haka zafin ya yi mata yawa sosai. Har lokacin da duhun Magrib ya shigo ta daure ta watsa ruwa da ƙyar, ta yi sallah. Sannan ta ɗan sha ruwan *lipton*, sannan ta tsotsi lemonta, sai barci ya ɗauketa.

Misalin goma da rabi na dare Barista ya shigo gidan ya kulle ko'ina na gidan, ya yi addu'a ya shigo falonsu cike da gajiyar aiki. A ransa ya san Sakina ta daɗe da yin barci, saboda barcin da ya aureta. A lokuta da dama da suka wuce tana zaune zaman jiransa an yi kwalliya an gyara mishi gida tsaf, cikinsa ma an gyara masa, shi ɗin kawai ake jira, amma yanzun fa sai maleji kawai abincin idan ta kwaɓa tun safe shi ne zai kasance a *flask* ɗin, sai dai 'ya dawo ya yi *serving* da kansa. Yana wannan tunanin sai ya ji wani iri a ransa. Ya miƙe daga zaman gajiyar da ya yi ya buɗe *fridge* ya tsiyayi ruwa mai sanyi ko ya samu *relief* ya sha. Ya ci ayaba guda ɗaya, ya cire *coat* ɗinshi ya duba gurin da ake aje mishi abinci bai gani ba. Sai ya wuce cikin *kitchen* yanda ya ga komai a bushe, ranshi ya bashi anya ko an ma ɗora tukunya a gidan? Ya gama lalubε bai ga komai ba, wani irin ɗacin rai ya ziyarce shi a rai, saboda dai ya kwaso bakar yunwa tun *breakfast*, sai *fresh milk* kawai ya sha guda ɗaya ana ta kujiba-kujibar neman na ɓatarwa. Ya kalli agogo misalin sha ɗayan dare, ina za shi yanzun ya samu

abinci. *Infact,* ma ya gaji, kuma yunwa yake ji da gaske. Gaskiya idan ya ce shayi zai sha ya ƙwari kansa, to ya zai yi? Ya fesar da iska daga cikin bakinsa, ya yi shiru. Can kuma sai ya kwashi kayanshi ya wuce ɗakinshi ko ɗakin matar bai kalla ba, saboda takaici, ya tuɓe kayanshi ya yi yo wanka, ya sa gajeran wando. Sannan ya fito falo ya haɗa shayi ya sha. Sannan ya koma *kitchen* ya ɗau indomie yana dafawa ya haɗa da ƙwai don ya ji dama-dama, tun da shi bai ɗauke ta abinci ba, matar gidan ce ke ci a yawancin lokuta.

Ya kai ya kawo har ya gama girkinsa ya juye a *plate* ya kawo falo, ya ɗau ruwa ya aje ya kunna *T.V. C.N.N.* yake kallo yana cin abincinsa ranshi ya ɗan saki daga damuwar da yake ciki.

Can kuma Sakina ta yi juyi don jin daɗin barci, ta ɗan buɗe ido har, sai kuma gabanta ya faɗi, ta buɗe idon sosai ta kalli agogo sha biyu har saura kwata. Nan da nan barcin ya bar idonta, ta miƙe a hankali ta fito. Idonta cikin idonsa sai lokacin ya ji wani iri, na yanda ya share yana harkarsa bai ko duba ta.

Ta iso gurinsa cikin ƙarfin hali da shagwaɓa ta zube a jikinsa ta ce, "Ogana ka dawo ne, amma ba ka tashe ni ba? Yau duka Allah kamar na mutu, ni haka ake yin ciki dama mutum duk ya takura ya tsani komai har kansa? Ni fa rayuwar nan yinta nake y[illegible] kawai ba wai don tana ba ni sha'awa ba." Ya ɗan ru[illegible] kafaɗarta yana riritata.

'Sorry sai hakur[illegible], a[illegible]ahalar ta wani ɗan lokaci ne, da ya wuce shi kenan, sa[illegible] ga kamar ba a yi ba, kin dawo *normal* rayuwa." Ta ce, "Uhm!" [illegible]a kalli abinci ta kalle shi.

"Au! Oga girki ka yi ne? Ba ka ga abinci ba ko? Allah yau dai gani nan tsananin rayuwa da mutuwa,

kwance kawai nake ina tsananin jin yunwa, tun ruwan bunu da na sha, na kasa jin dadin komai jiranka nake yi ka dawo ka samo mini wani abu ko 'yar gurasar mai balangu ce ina jin ran iya ci." Ya kalle ta ya ce, "Kin san da karfe nawa kike magana? Ni dìn da na dawo na iso gida da bukatar abinci da hutu, sai ban samu yanda nake so ba, kin ga inda na yi maleji, in kina iyawa sauko mu ga ko zai zauna." Ta kalli abincin sai kawai ta ji zuciyarta ta tashi sosai, ta dauke ido ta runtse shi ta jingina bayanta da kujera ba ta kuma magana ba, har ya gama cin abincinsa ya kwashe kwanukan ya mayar. Sai lokacin ya fara lallabata ta yi hakuri su je su kwanta gobe zai shigo mata da abin da take bukata ko da rana ne tun da yanzun dare ya yi. Haka nan ta mike tana layi kanta na wani irin tsananin sarawa na tsananin yunwa, rashin kwarin jiki da damuwa.

Haka suka isa har gadon barcinsa, yana ta tarairayarta, lokacin da ya je ya yi *brush* ta kwanta daidai 2+2 take hadawa ta kasa ba ta hudu, har ya iso gareta, ya fada mata a hankali zai fara rudarta da soyayyarshi, ta janye da hanzari ta ce, "Oga zan mutu ne?" Ya kalle ta wani galala ya ce, "Ba ki gani ina da bukata ba?" Ta marairaice ta ce, "Haba Oga wai me ya sa kwana biyu kake acting kamar ba mai sona ba?" Ya dan tsareta ya ce, "Amma dai kin san kwana biyu ina takura ko ba na samun yanda nake so ko?"

Ta ce, "Na sani hakuri fa za ka yi ba ka gani ni yanda nake, yanzun ba na jin dadin komai. yunwa nake ji da rashin kwarin jiki." Bai ce komai ba sai ya juya baya ya yi shiru. Can sai ta ji shi yana munshari har ya yi barci. Ta yi dif tunani take yi sosai har ita ma daga can barci ya daukéta.

Da Asubahi ya tashi bai tashe ta ba, saboda tashen barci da take yi. Ya yi sallarshi ya gama addu'o'insa, ya yi wanka ya shirya ragowar *tea* ɗin shi na dare shi ya motsa ya sha. Sauri yake yi, saboda Kaduna za shi don gudanar da wani bincike kan wata ƙara da ke hannunsu. Har ya gama shiri bakwai da rabi ba ta tashi ba, sai ya yagi *paper* ya yi rubutu ya aje mata da ɗan kuɗin kashewa ya bar gidan.

Sai bayan takwas ta farka ta yi tasbihi ta ware idonta, haske sosai ya haske mata ido, ta duba ba ta ga Barista ba, ta miƙe ta fito falo. *Kitchen, toilet* duk baya nan ta leƙa ta baranda ba ta ga motarshi ba. Sai ta ji wani irin ƙunci a ranta, ta haƙura ta shiga banɗaki ta yi alwala. Tana sallah tana kuka, ita dai ba ta gane irin wannan hali da Barista yake tsiro mata ba. Ɗama su haka maza suke gangar jikinka kawai suke so a lokacin da take da lafiya suna kuma muradinta? In bacin haka duk wannan ƙyaliya, shariyar da Barista ya tsira ta maye, saboda ya mata ciki tana cikin lalura ta gaza biya masa buƙata? Cewa take yi shi ne silar wanda ya jefa ta halin da take ciki, ba zai tausaya mata ba? Wai ashe haka aure yake? Ina duk soyayyar nan? Soyayyar da ke ganin da ko wuta aka ce ya faɗa saboda ita zai yi, amma sai wani sharcta yake yi, ya barta ta ci kanta da kanta. Idan ta ce baya son cikin ne kamar ta zalunce shi, don ɗan tsakon da aka samu kafin cikin ya ɓulla kullum mita yake yi yana lashe cikin da tambayar shi yaushe cikin zai shiga? Ya shigan kuma ya gaza sama mata farin ciki da kyakkyawar kulawa. Ta yi kuka sosai da sosai ta miƙe cikin ƙarfin zuciya tana gyara gadon ɗakinta da na ɗakinsa, ta yi shara sama-sama a ɗakunan falon, kuma ta barshi tun da ba wani datti ya yi ba, saboda yaran ɓatawa. Tana shara ne ta ga *note* ɗin da ya bari.

***Excellency***

***Kin tashi lafiya? Ina ta sauri zan je Kaduna ban tashe ki ba, saboda ɓa a tashin ku manya kuna barci (ko yana dariya) sai na dawo zan iso miki da kayan daɗi. Sai na kira ki.***

***Love Barista***

Ta taɓe baki, kalamanshi ba su wani burge ta ba. Ko wanka ba ta yi ba, doguwar riga kawai ta zunbulo, ta ɗauko makullin motarta, mayafi da jakarta, gida kawai ta yi niyar zuwa, lokaci ƙarfe tara da arba'in da biyar. Ta yi addu'a ta kullo gidan ta tada motarta sai Gwauran Dutse, a lokacin Alhajinsu ko fita bai yi ba.

Amma ta ce, "Kai Sakina wannan sammakon fa lafiya?"

Ta zauna a gefen gado ta ce, 'Kalau Amma asibiti na je, ban samu ganin likitan ba, sai na yo gida." Ta yi ajiyar zuciya.

"To Allah ya kyauta." Ta kalleta cikin kulawa da tausayawa ta ce, "Ko akwai abin da kike so?" Ta daɗa narkewa ta ce, "Idan kuna da koko ku ba ni na sha. Ko a aika gidan Rakiya ko za a samo mini wainar masa, ina ga ko zan iya ci? Allah Amma ba na iya cin abinci, idan na ci sai na yi ta amai, kuma yau kwana biyu ban da lemo sai ɗan ruwan shayi baƙi kawai na sha." Cikin tausayawa ta ce, 'Sai haƙuri, ai lokaci ne da shi da ya kauce shi kenan, kun ɗebo shegen laulayin nan namu mai wahala, Allah dai ya rangwanta. Amin."

Duk abin da ta buƙata an samu ta sha kokon sosai. wainar ce guda uku kawai ta ci, sai barci ya ɗauketa. ko da ta tashi sai ta ji ta ɗan samu nutsuwa da kwarin jiki. daɗin daɗawa ma kuma sai yaya Zainab ta zo ita da 'ya'yanta. Sai

gidan ya yi armashi sosai, har ta ringa jin uwa ba ita ce wannan maridiyar, kun san ciwo shí ma yana son kaɗaici, laulayi na da wani siddabaru a gida kamar ya cinyeka, amma kuma idan ka fita gari ka sha iska sai ka ji ba ya kai, in ɗan miyau ne ma duk sai ya tsaya.

Yaya Zainab ta kalle ta ta ce, "Kai Sakina wannan irin kwantsamewa?" Ta marairace ta ce, "To ya Zainab ya zan yi kin ga yanda na ke ji? Ba ni da wani kuzari fa, kullum a kwance nake ga gida ni ɗaya uwa maiya, sai sanda ya dawo fa zan ji motsin mutum, wata ran ma sai ya kai goman dare bai dawo ba."

Ta ce, "To ki samu mai aiki man, ta ringa taya ki yawancin aiyuka ta kuma ɗebe miki kewa, kaɗaici ga ciwo ai masifa ne." Ta ce, "Um! Ni ina ta kaina ba na ma iya tuna ire-iren waɗannan abubuwan."

Ta ce, "To ai yanzun an tuna sarki, akwai wata mata Ta Birni tana kawo yara daga ƙauyuka, zan wa maƙwabciyata magana babarta ake kawowa ta samo guda ɗaya kya rage, har in kin haihu ta tayaki hidimar abun da Allah zai ba ku." Ta yi jum kamar ba ta yi maraba da abin da ake bata shawara ba. Ta ce, "Me ye ki kai zungum? Ko ba kya so ne?" Ta girgiza kai.

"A'a ba wai ba na so ba ne, ki dai bari na yi mishi maganar kafin ki yi tun da dai shi ne mai biya." Ta harareta.

"Ban gane ba, Barista ne kuɗin 'yar aikin zai gagare shi." Amma ta katse ta ta ce, "Kin ga batta tun da ta ce za ta gaya masa tun da dai gidansu ne su kaɗai suka san yanda suke rayuwarsu." Ta yi gum ba ta kuma cewa komai ba. Sai suka cigaba da hirarsu.

Da rana ca ta yi ai mata faten tsaki mai yaji da yakuwa, an yi, ta kuma ci, har ta rufe ragowa za ta yi guzuri

da shi. Ai ba su bar gida ba sai bayan shida lokacin da Alhajin ya dawo gida ya ce, "Kai Sakina har yau kina nan baki tafi ba, ko?" Sai suka miƙe kowacce ta fara haɗa kayanta da sun wa Amma kunnen uwar shegu. Tare suka fito kowa ta yi hanyar gidanta. Bayan Sakinan ta yi wa Barista guzuri da abincin da su kai na dare da tsarabar kasuwa ta Alhaji.

Har ta dawo Barista bai dawo ba, wannan ya ba ta damar bayan ta yi sallar Magariba ta gyara falonta, har da sa turaren wuta, abun da ta daɗe ba ta yi ba. Ta yo wanka, ta yi sallar Isha'i ta zauna tana kallonta. Sai lokacin zuciyarta ta taɓu, tun jiya rabonta da mijinta, wayar da ya ce zai yo bai yi ba. Lafiya kenan shi da ya yi tafiya ko dai shariyar ce? Ranta ya raya mata ta yi masa *flashing,* ɗayan ɓangaren ya haneta tun da shi bai neme ki ba ke don me za ki neme shi (Abun da ke damun mu kenan matan Hausawa, a koda yaushe miji kawai muke jira da nuna ƙauna da kulawa ta ɓangaren hidimar gida da shimfiɗa. Kowane rai fa ku sani yana ƙaunar wanda yake kyautata mashi. Wani jiƙon idan ya nuna miki soyayyarshi ke ma nuna mishi taki ƙaunar mai sanyin daɗi, wannan shi zai sa ya mutu a kan sonki, koda ƙaddara ta samu rabuwa ko ƙarin aure ko ma kina da kishiyar ya ringa ji ba yake. Ke ɗin wata [illegible] wacce a kai wa baiwa mai yawa, don haka mata mu kula).

Daya zuciyar ta rinjaye ta ta janyo wayar tata ta yi masa *flashing* har ya ɗauka ya ce, *"Hello."* Sai ta kashe. Shi kuma ɓangarensa sai ya ga kira, shi da kansa ya bawa kansa laifi, ƙin maganar da ta yi ya san komai, don haka sai ya ringa kira ƙememe sai ta ƙi ɗauka, ya kira ya fi sau goma sha biyar tana kallon w a yar na *ringing* ta ƙi ɗauka. Wannan ya sa ya yi masifar ruɗewa gani yake yi kawai

wani babban al'amari ne ya same ta, ita da ke wani hali, ƙila *assistance (taimako)* ɗinsa kawai take nema.

Ya miƙe tsaye ya ce, "Ka ga Ibrahim bar neman kuɗin nan ni zan wuce gida, Madam ta yi kira na ɗau barami." Ya harare shi, "To gayawa gwauro, wai ba ka jira sauran minti nawa ne, sai da aiki ya zo ƙarshe mu ɗin ... na mu mata ai na da buƙatarmu." Ya fara haɗa *papers* ɗinsa ya ce, "Sai kuma ka yi, sau nawa nake gaya ma matata *patient* ce, kana sani share ta, ka bari kawai ta lallaɓa aurena, tun jiya rabon da ta sani a ido, gara na je, Allah ya kai mu gobe ma ƙarasa tun safe ka ke wahalar da ni, kai shegen sun kuɗi gare ka."

Ibrahim ya kalli Mukhtar ya ce, "Ka jini da sheger sama ni yake wa gori, ko wa ya samo *contract* ɗin? Saboda sabon shiga ne dadi mace zai mana iya shege." Ya rataye jakarsa ya ce, "Kun ga tafiyata, Allah ya ba mu alhairi." Bai ko jira mai za su ce ba ya yi gaba abinsa.

Ibrahim da Mukhtar suka kalli juna suka gyaɗa kai. Mukhtar ya ce, "To sai da safen ko, nima fa a gajiye nake gara na koma gida na shiga alfarmar matata." Ya harare shi.

"Ai wallahi ka yi kaɗan idan tasa *patient* ce ya tafi kai kuma fa? Hakurin duk za mu yi, mu ƙarasa gobe kawai sai mu shigar da ... ɗin ofishin mai girma gwamna yaushe za mu ringa *delay?*" Haka shi ma ya hakura suka kammala, misalin sha ɗayan dare kowanne ya komawa iyalinshi.

Barista a gurin mai gasa balangu ya tsaya ya sa aka yanka mishi shi, da kuma gurasa daban. Sannan a gefe ga mai tsire da gurasa shi ma duk ya saya, aka zuba naman daban, gurasar daban, don ya sani idan ya haɗa ƙila ta ce naman da ta gani ya hanata cin gurasar, ya biya ya samo

mata *fresh milk* tun da ko lafiya ba mai bukatar kayan zaki ba ce, ya nufi hanyar gida, komai yake yi, yana yi da hanzari ne don ya isa gida *on time*.

Ya kulle ko'ina bayan ya yi addu'a, zuciyarshi ta dan buga shi kansa ji yake yi kamar ya yi *losing*, ko kuma wani me laifi. Ya ringa taku da nutsuwa ya dage *curtain* din falo, yana sallama, komai tsaf, kamshi ne da sanyin gurin mai dadi ya ratsa shi. Sai dan kira da yake tashi sannu-sannu daga *T.V.* din da take kallo. Ya hangota kwance kan doguwar kujera ta yi kwalliya mai sauki a tamfarta *Delove* yelluwa, ta karbi jikinta da dan karamin dinkinta mai kyau. A fuskarta ba kwalliya sai farar *powder* da *wet lips* da ta sa a bakinta. Shi a fuskarsa ya ga ta yi mishi kyau sosai, don ya kwana biyu rabonshi da ganin ire-iren wannan kwalliyar tun, da ta shiga koma, sai kawai ta yi wanka da tsola doguwar riga wani jikon ba ko dan mai tana ta kanta. Ya kare mata kallo a zatonsa barcin nata take yi. Wani irin tausayin ta ya ratsa shi, shi da kansa ya san yanayin abubuwa da ba su dace ba, to amma ya rasa kansa, shi kansa yana zargin kan nasa uwa ya fiye son kai.

Idonta biyu, tun da yau tana jin kamar garau take shi din kawai ita ma take muradi tana bukatar soyayyarshi da kulawa, jan aji ne kawai take yi, shi ya sa ta share shi ta lumshe ido kamar mai barci. Ya aje kayan hannunsa kan dan teburin kujeru a hankai, ya cire rigarshi da jakarshi ya aje ya iso gabanta ya rankwafa mata ya fara ba ta soyayyarshi. Ta yi bakam kamar mai barci, zuciyarta ta yi yi, jikinta ya fara karbar marabarshi. Sai ta yi wal da ido ...nta cikin nasa, abin da ta gani ... kwayar idonshi dole ta ...she nata ta fara kokarin ture shi, ya dada manne mata, ...i yake cikin kunnenta.

*"Pls sorry I need your respond pls Excellency."*

Dama jan aji ne da ta ja iya iyawa, dole ta bada kai bori ya hau, don ya tafi a soyayyarta.

Ya samu yanda yake so, soyayyar da ya jima bai samu ba, komai ya lafa ya rungumeta yana shafata, ta ture shi ta fashe da kuka. Gaba ɗaya ya rikice ya kasa kataɓus, ya yi ta ƙoƙari yana lallaɓata da ƙyar ta yi shiru ya ce, 'Mene ne kuma *Excellency?"* Tana share ido ta kalle shi.

"Ni idan wani ya ce mini za ka ringa mini wulaƙanci irin haka zan tsine mishi albarka, tafi gaban dubu, don irin so da ƙaunar da ka nuna mini ina gaban iyayena da ƙaunar da ka nuna mini lokacin ina gidanka. Don me ne tashi ɗaya yau don ka ga na yi ciki, kuma shi kenan ina tare da larura sai ka tsane ni ka juya mini baya? Dama ba son nawa ne a ranka ba, buƙatarka kawai ka ringa kwantawa da ni, kana jin daɗinka tun da yanzun na zama ga yanda nake, shi kenan sai ka watsar da ni na zama ya kwai ya babu? Dama ku maza haka *true colour* ɗin ku ta ke, ko ko dai kai ne me irin wannan salon? Ni a labaran da nake ji da littattafan da nake karantawa na Hausa irin na manyan marubutan nan, irin Bilkisu, Zuwaira, Rahma, Sodangi, Kankia, Amma, B.H da sauransu, fadi mana suke yi yanda namiji ke macewa kan soyayyar matar shi, musamman idan an samu abin inganta soyayyar, amma [illegible] kuicin kawaida nan ke samu shariya ce kawai da [illegible] kance. Haba Ogana ni ɗin na cancanci abin da ka ke mini din ne?"

Ya runtse ido, ya dafe kai ya ce, "Oh! My God, Sakina irin sharrin da za ki ƙullan kuma kenan?"

Ta ce, 'Ba sharri Barista, kom i fa ina gani ina ta kauda ido ne ganin cewar ni ɗin ta k[illegible] na nake ko na mutu ko na rayuwa yaushe zan ringa nema rigima? Amma ina

sane da abun da ake yanzun da wanda ake yi da." Ya sauko daga kan kujerar ya zauna gabanta dabas, ya ɗora hannayensa kan ƙafafunta ya ce, "Wallahi Sakina ni duk abin da kika faɗa ba fa haka ba ne, ni har raina ba ni da wata manufa ta cutar da ke, wai ma to idan ban kula da ke da farin cikina, sanyin idona ba, da wa zan kula? Ki yi haƙuri ƙila kina ganin ban zaman gidan irin na da bare har na ringa kulawa da ke. Allah wasu sabgogi ne suka samu ana ƙoƙarin samun cigaba wanda na san ke ma za ki yi farin ciki da irin hakan, harkokin ne dole sai an yi zirga-zirga da aikace-aikace wanda su ke ɗan hana ni sukuni, ki yi haƙuri, *I don't mean that,* amma tun da kin mini wannan fassarar don Allah ki juya ni kaina abubuwan fin ƙarfina suke yi." Ta ƙanƙance ido.

"Kuma har da waya ma Ogana yanzun ban da matsayin da za a ringa mini, kana sane ba ni da lafiya kwarai ni kaɗai a gida komai fa na iya faruwa ba ni da wanda zan kama." Ya ce, "Ki yi haƙuri dai na amsa laifina duk insha Allahu za a gyara, wannan fassara da kika mini duk ba haka take ba."

Duk wani ilimbo da daɗin baki irin na maza sai da ya san yanda ya yi ya wanke kansa da su, har ta ke jin zuciyarta ta yi *cooling* kwarai. Tana nan zaune shi ya kawo mata gurasarta da namanta har gabanta ya kawo ruwan sanyi da *fresh milk* ya aje mata, ya kashe mata ido.

"To Edcellency sauko ga safon ki." Ta ringa yatsina tana shagwaɓa, kamar ba za ta sauko ba, ya ringa lallaɓata har ta samu ta ɗan tsakuri wani abun. Sannan ya samu nutsuwa. Shi da kansa ya ɗauko abincinsa yana ci, suna hirarsu kaɗan-kaɗan mai daɗi, abun da sun kwana biyu rabon da a samu wannan saken.

Ya kalleta, "Edcellency, gara dai a nemi 'yar yarinya ko wata mata ta ringa rage miki yawancin aiyuka. Tana kuma ɗebe miki kewa ta ringa duba min ke, nima na gane kina takura da yawa kaɗaici da ciwo ba su da daɗi, gara na yi wani abu." Ta ringa ilimbo na a tausaya mata, har sai da ya amince da buƙatunta tas. Sun aje maganar za a wa Yaya Zainab maganar ta samo mai aikin.

Sun cigaba da lallaɓawa yau a samu lafiya, gobe sai haƙuri. An samo mata yarinya ƙarama mai hankali, wai ita Rahane, tare suke zaune, idan tana da kuzari su yi aikin gidansu tare, idan kuma babu sai dai ita Rahanen ta yi. Yarinyar mai lura ce da kazar-kazar, sai zaman nasu ya yi daɗi.

Barista ya je Legos wata Semina da gwamnati ta shiryawa lauyoyinta, a lokacin cikin kamar ya fashe. Ai ko ilai a daren da ya tafi naƙuda mai zafi ta kama ta ga dare, ga ciwo, gida daga ita sai Rahane, wa ta kama? Ta lalubo wayarta wa za ta kira ya taimake ta. Ta tuna Hajiyarsa, to ita wa gare ta, gida daga ita sai Maryam, gidansu ko Alhajinsu gama yayyanta maza. Ta latsa wayar, Amma *is not recheacble*, ta wurgar da ita sai da ciwo ya lafa ta lalubi ta Baba, a kashe take, ta yi ta Umma, ta yi ta Muji duk ba labari. Ta fashe da ihu, ga takaici, ga ihu kai ɗan adam na cikin nadama dama haka hiahuwa take da azaba?

Dole ta nemo Barista duk da ba wani abu da zai iya shi da ke uwa duniya? Wayarshi buɗe take yana tsakar barci ya ji waya tsakar ka \ gigice ya farka ya kunna wuta idonshi kan agogo uku da kwata na dare. ranshi ya bashi ko matar ce. Ilai kuwa jikinsa na kyarma ya ɗaga wayar, faɗi yake,

"Excellency ya dai lafiya?" Ta zuba ihu.

'Zan mutu Oga na rasa mai taimakan."

Ya ce, "Oh! God kin......" Ai sai ta wurgar da waya da wani uban ciwo ya ratsa ta. Ya yi magana ya yi ihun shiru, sai ya juya ya latsa wannan wayar, ya buga waccan, ya samu layin yayansa mijin Hauwa yana barci ya ji, waya ya ce, 'Yaya ka taimaka Sakina za ta mutu ita kaɗai a gida ni kuma ina Legos, don Allah........" Ai bai gama jin sa ba ya latse wayar ya tashi Hauwa suka ficc. Bai haƙura ba ya yi waya gidansu a kai sa'a Mujin an samu tasa, ya tashi su Amma, da ita da Alhajinsu da Mujin suka fita misalin uku da rabi dabararsa a ga wanda zai riga zuwa.

Ko'ina ba laifi akwai 'yar tazara, amma dai su Muji sun ƙi kusa. Allah da iko kusan tare suka je aka ringa buga ƙofa da ƙyar da dabara ta buɗe ƙofa, Rahane ba ta iyawa ina amfanin wannan ta riga ta galabaita asibitin kawai suka wuce. Likita ya amsheta. Godiya ga Allah aka zo asibiti, don babyn zaran mahaifa ya shaƙe masa wuya, sannan hannunshi ya yi karan tsaye a bakin hanyar fitowa, dole da badan an zo asibiti ba, gaskiya dole a rasa ɗaya koma duka. Da taimakon Allah likitoci su rabata da shi lafiya, amma bayan ta gama sarewa, ko hannu ba ta iya ɗagawa saboda tsabar wahala.

Barka barka, shi ma Barista kamar da shi aka kwana jirgin bakwai ya hawo, takwas da 'yan motsi yana nan. Ya amshi baby cikin tsananin farin ciki, yana kallon 'yan uwa suna mishi barka da arziki, ya rungume baby ya kalli Hajiyarsa, don ita ma tun Asubahi tana nan, ga su Maryam ya ce, "Sakinan ƙa lafiya?"

Hajiya ta ce, "Likita ya ce ƙalau take, sai dai tana barci ne, saboda ta jigata da yawa, wannan mara kunyar ya wahalar mini da 'ya."

"Ai fa ma jin yanda ta kira ni na san tana tsaka-mai-wuya, na so a lokacin dama ina da fuffuke tashi kawai zan yi, saboda tsabar rudu, tun lokacin karatu nake taimaka da addu'o'i masu yawa, ku da kuke kusa kun fini kwanciyar hankali, seminar ta mu sai yau bayan biyu za mu gama, mu biyo jirgin yammma, abokaina sai dai su shafa su ji wayam, ni ko ta kan su ban tuna ba, tafiyar ma da ai kamar ba zan yi ba, rabon dai ai haka. Allah mun gode maka. Ungo nan Maryam ɗan nan naki, bari na je na ga matata."

Likita da kansa ya yi masa jagora. Barci take sosai, da ragowar ruwanta ana ƙara mata ya zauna gefen gadon, ya riƙe mata hannu ta bashi matuƙar tausayi darc ɗaya ta yi wata irin rama da hasken wahala. Kai mata suna aiki. Ya kai hannu ya share hawayen idonshi, kai ya ƙara sonta da tausaya mata, ga shi ta bashi farin ciki mai yawa. Ta buɗe ido har cikin barci ta ganshi har da hawayensa ta kai hannu ta shafi fuskarshi ta ce, "Oga." Sai kuma barcin ya kuma gaba da ita. Ya yi ta kallonta. likita ya ce, "Oga ba fa matsala barci ne kawai." Ya matsa jikin matar shi ya kwanta, ya zaro wayarshi aka fara bugawa abokai da 'yan'uwa waya an yi barka da arziki, baki har kunne.

Asibitin nan ya cika da 'yan'uwa da abokan arziki a kwanaki biyun nan da ta yi, ta kuma yi garau da ita. Sai abincinta take ci mai daɗi, ta sha kwalliyarta tana karɓar barka. A ranar da yammaci likita ya sallamota ta dawo gidanta cikin godiyar Allah da farin ciki mai yawa. Barista ya rasa inda zai tsoma ranshi, don daɗi, idan ya leƙa ya ga matarshi ta yi sarai ta ci ado mai yawa, ga kuma *a boy* a gefe sai ya rasa tantance lokacin da yafi farin ciki da lokacin amarci da lokacin nan na zaman jego. Matar fa ta gama tafiyar da shi cikin soyayyarta mai alfarma. Ta cigaba

da zaman barka, 'yan'uwa da abokan arziki na ta taya su farin ciki.

Ranar suna suka sawa yaran suna Muhammad Mufazzal. Yaro mai kyau da kwarjini. Ya zo da falala masu yawa. Bikin suna ya yi armashi sosai, don har ni kaina Maiturare na halarci bikin, na ci wara sosai da ƙyar na iya komawa su Abba da Yaya Abdul ina nishi faɗi suke. Umma ba ki kawo mana komai ba ne, gurin sunan? Da ƙyar na iya nuni aka miƙon jaka, na sam musu tsiren da *snacks* ɗin da na faki ido na wurga jaka ni fa ban sanya gurin ɗan abun kusa da baka (Dariya). Faɗi suke, kai Amma Umma an ci an more, har da extra? Masu da shi ne.

Na ce, Kai dai bari Yaya Amir, ai Barista ya nuna soyayyarshi kowa faɗi yake suna masha Allah, Allah dai ya raya Mufazzal Ida albarka, soyayyar kuma ta ɗore ta har abada. Amin.

Dare ko na yi ciki ya ce, Hauwa Salamu Alaiki. Haba in ba ki yi ba ni guri. Da taimakon nawa *man ɗin*, komai ya yi *stop*. Ya kama faɗa "Ke fa ba ki iya samun banza ba, daga gayyarki kin saki ciki, to *well done*, ga dai *playground nan*. Allah ya sauwaƙe." Na yi fakare, to ya zan yi? Kwaɗayina (Dariya).

An cigaba da rainon Mufazzal cikin so da kulawa. Suma sun cigaba da jin daɗin rayuwarsu 'yan ɓarakukin da da duk aka samu duk an ɗinke. sai kwanciyar hankali da soyewa. Har aka yi arba'in, ta zaga ɗangi sosai don a lokacin sun yi wata tafiya Duts kan wata shari'a suna sa ran za su kwana uku, ta kwan daya a gidansu ta zazzaga. Sannan ta tafi Kofar Nassarawa gidan Hajiya ta kwana biyu. Maryam nata rakata gidan 'yan'uwa. Bayan kwana uku Barista ya dawo, lokacin ta koma gidanta. Ya iso da

zumuɗi ita ma duk ta shiryawa zumuɗinsa, an ci an sha, aka kuma kwana ana buatar Ubangiji. Rayuwarsu mai daɗi da kowane zai fatan in ya same ta ya more.

Barista Alhamdulillah, yanzun ƙofofi na ta buɗewa, sunansa na daɗa shahara a tsakanin lauyoyi 'yan'uwansa. Allah ya bashi hikima kwarai da hangen nesa, ga jajurcewa a kan aikinsa. Nan da nan ya yi suna. Allah kuma ya sa albarka a cikin lamarin komai yana tafiya amintacce.

A cikin haka ne Allah ya fado da wata shari'a mai tsoka, to mai man don giwaye biyu ne suke tafka tsiya a kan wani fili da kowa yake iƙirarin mallakar shi, kuma kowa na da shaidu. Mutanen su ne; **Sanata David Modu**, da ***Director of Monitoring and Evaluation na Ministry of Education Abuja,*** Alhaji Ubale Yusuf.

Senetor Daɓid shi ne ya ɗauki Barista a matsayin lauyansa ya bashi ko wani irin shaidu da zai gabatar. To an dai fafata, fafatawa mai tsauri inda kowane ɓangare yake jin a shari'ar shi ke da nasara. To Allah baya barci, kuma baya zalunci fili ya tabbata na David ne, sakamakon ƙwararrun shaidu da shi da lauyansa suka gabatar, dole su Alh. Ubale s uka dangana duk da dama sunn sani ɗin ai ba kayansu ba ne, amma sun samu duk wasu kwararan ɓidance da za su rika sun kuma rika, don an fafata Allah ne ya yi, Allah nasa ya amso mishi kayansa.

To wannan shari'ar ma ta ƙara fito da sunansa. Sannan shi Senator David ya ji daɗi kwarai da gaske, sannan ya jawo Barista a jiki ya maida shi *personal assistance* ɗinsa, bayan kuma lauyansa da ya maida shi, ta ɓangaren duk wasu sabgoginsu, bai kuma bar shi bakan ba lokaci-lokaci idan wata kwangila ta fado ya kan danƙa mashi don shi ma ya samu ƙaruwa.

To yanzun ma wata kwangila ce ya samar masa mai tsokar gaske. wacce ake ɓuƙatar wasu miliyoyin kuɗi, don gudanar da ita, idan an kammala za a samu alhairi mai yawan gaske. Barista ba shi da wadannan maƙudan kudaɗan da zai gudanar da ita. sai ya sanyo abokanshi Ibrahim da Mukhtar suka haɗa ƙarfi da ƙarfe aka samar da guduma.

Masha Allah an samu abun da ake so, shi a cikin kasonsa ya sai wani ƙaramin gida a Gwammaja, ya canzawa kanshi mota CAMRY sabuwa dal, ɓaƙa. Sakina ma aka sai mata HONDA 86 *New Model* sabuwa, a kaima Hajiya gyara a gurinta, aka fito da 'yar tsohuwa mai ran ƙarfe, mai albarkar baya.

Ranar da ya zo da motar Sakina ta yi tsallen murna ta rungume shi tana mishi soyayyarta ta sake ta ce, "Barista ame zan ma ne kai ma ka ji daɗi, kamar yanda ka jiyar da ni daɗi yau?" Ya kishingiɗa a kan kujera yana mai dariya. Ta kalle shi.

"Um! Ina jinka." Ya ɗaga kafaɗa.

"*Well.* abun da nake so yau ki ta bani *kiss till day break*, ki fara daga yanzu." Ta riƙe haɓa.

*'Just like that'* Ka kwafsa ai ni na shirya haka, ka dai ɗan ban lokaci wannan jar danjar kawai ta ɗauke farar na kamawa za ka gane, eh yes an yi ma baiwa da matar kirki." Ya mata wani kallo ta hure mishi ido, ta faɗa jikin suna dariya.

A motar a kai ɗafiya zuwa gidansu da gidansu Hajiya nuna sabuwar ƙaruwar da ta samu. kuwa na ta mata barka yana mata fatan ciki da fatan Allah ya fissheta sharrin ƙarfe. Amin. Ranar ba zan ya kwatanta muku tsananin farin cikin ta ba.

Bayan nan ma a cikin gidan Barista ya yi musu 'yan gyare-gyare da sanya musu sababbin abubuwa, kai komai dai shar da su. Ya samu wasu 'yan caji ya je ya gaida Amma da Umma da Alhaji, yaran gidan ma duk sun shaida Barista ƙa dawa ta yi nama. Shi ma a na shi *side* ɗin an shashshaida don Anti Hauwa ma sabon *fridge* ya sai mata dal, da ya je gidan ya ji tana ƙorafin nata yana ba ta matsala bai gaya mata ba sai ji ta yi kawai ana kaya-kaya ga kaya, ta rasa wacce irin godiya za ta yi masa sai kawai ta tsaya tana kallonsa yaa sawa a janye tsohon daga gurin za a sa sabo.

Ya kalleta da harara. "Kin wani saki baki yau ba baka ne sai kunne? Ko dai na gama saye bakin duka, na huta da carinki." Ta yi murmushi ta ce, "To jeka an barma ni kuma ai yanzun na sallama. An gode Allah ya raya iyali, amin."

To rayuwar da aka tsinci kai kenan. Rayuwa mai daɗin gaske, mai tafiya da albarka da buɗi mai yawa. Suna jin daɗin juna, kowa na kula da ɗan'uwanshi da gasken-gaske.

Sakina macece 'yar soyayya, irin matannan da suka san maza, suka kuma ɗauke su da daraja mai yawa. Sakina macece da ke son mijinta ya so ta, ya nuna mata kulawa da soyayyarshi, ya ringa nuna yabawa a ciki duk abun da ta yi na yau da kullum. Sannan a ɓangaren rayuwar dare mai bukatar namiji ya nuna mata jarumtarshi. An yi sa'a kuma ta samu hakan Barista ya iya soyayya, ya iya tafiyar da ita har ya shagalar da ita ta kuma sakankancewa ba wani sai shi ɗin Wannan ya daɗa sa ta zage damtse don gamsar da shi, duk wasu bukatunshi, tun da tana samun yanda take so. Shi ma ɗin ya yi dai-dai da ita. Barista ko gayu a kai masa

sai ya yaba ya ringa kiraki, yana koɗata, ita kuma tana jin daɗi kanta na fashewa, idan ko abinci ne ya ringa cewa kai anya ko na taɓa cin abinci mai daɗi irin na yau." Ta ɗan harare shi ta ce, "Haba Malam santi dai, wanda ka ci a baya ya dai wuce ne kawai." Sai ya gyaɗa kai yana dariya. I ban garin ko in ya ringa sakin zance tana daɗa ziga shi, sai su ba ku matuƙar kunyar gaske.

Rayuwa na tafiya da sauyi mai yawa, wani daɗi, wani akasin hakan. Ana tsaka da wannan shagala, Sakina ta fara cin karo da duhu a cikin rayuwar zaman aurenta. Abubuwa da yawa na mata karan tsaye, tana samun matsala gun Oga, amma ko da yaushe tana haƙurƙurtar da ranta da yi wa Barista afuwa ƙila dai halin yau da gobe, da kuma faɗin manya na zaman gidan miji sai haƙuri. To tun tana ɗan kakkauccewa, har abun ya fara kai ta bango, ta fara maida addu'arta kacokan kan neman dai-daito, amma a banza wai an tsikari kakkausa. Duk wani abu da ta sani tana yi daa, kokari take yi tana ƙara azama a kan shi, amma ya kwai ya babu to sai ta fara rage walwala, kaɗan-kaɗan 'yar ƙibar da ta aje mai ban sha'awa ta fara raguwa don babu kwanciyar hankali. Sannu kan hannkali sai ga fuska ta kwama.

Wata rana ta je gidan Hajiya, ta shiga gidan Anti Hauwa suna hira ta kalle ta ta ce, "Sakina zabgewa fa naga kina yi, ko an samu ƙanin Mussadik ne?" Ta ce, "A'a wallahi ko ɗaya, ni a yanzun ma *red card* ne a hannuna, kawai dai yanayin yin ne." Ta yi ɗan sukui tana kallanta ta ce, "Ba dai ƙwaƙwaba, amma na ga kin rage walwala da rahar kin yi kama da mai damuwa duk mutumin da ya sanki zai iya fahimtar hakan in dai yana da tsinkaye." Ta yi shiru har kamar ba za ta tanka ba, sai Antie Hauwa ta sabu

da ita, tama shiga *kitchen* za ta fara hidimar girkin dare, don ba ta son yi mata ƙwaƙwa, amma ita a ganinta Sakinan ce tata ba ma Baristan ba, saboda yanda yarinyar ke mata abun gwanın sha'awa, ba irin akasarin abubuwan da suke faruwa ba wai kishi tsakanin facaloli, ya Allah, gidanku ɗaya ko kuma nesa da juna haka kawai sai ku ƙagawa kan ku bala'i ba gaira ba dalili, kishi ne ko ko baƙin ciki a dai nemo gaskiya ni ban wani yarda da kishi ba, to kishi ma na me? Mijinku ɗaya ko ƙaƙa? Allah ya kauta.

An daɗe ta biyo ta *kitchen* ɗin tana tayata tankaɗan garin fulawa za ta kwaɓa musu alkumbens (Alkubus). Ta ce, "Anti ina fama da matsala a gidana ne, matsalar da kullum nake ƙoƙarin ƙara ɓoye ta da ƙara haƙurƙurtar da raina, na amince zaman auren gaba ɗayan shi haƙuri ne. kullum idan na duba zuwa na ƙasa da ni sai na ƙara godewa Allah da ya yi mini ni'ima babba, domin ya yi mini suturar da dubun mata bai yi musu ba. Wannan sai ya ƙara shagaltar da ni, lallai na yi haƙuri na zauna gidan mijina. zama ma yanzun na fara; domin wata macen ta malam Bahaushe ta ci ɗan banzan duka, ba kuma ci, ba sha, dole ta nema da kanta ta yi kuma zaune take gidan aurenta. Don me ni zan ɗaga hankalina in ringa tunanin gudu? Antie ashe wauta nake yi jama'a har sun fara gane ni ɗin ina tare da damuwa da rashin jin daɗin aure. Gaskiya a yanzun kusan gab nake da fashewa ban taɓa tunkarar kowa da maganar nan ban ba sa ga Ubangijina da kullum nake kai kukana gare shi da ya yi mini rangwami. To ga shi ke ɗin kin gane akwai wata ƙasa. To Antie, Barista dai na ki ne, nima ɗin taki ce a cikin nagartarki na yi imanin za ki yi adalci a cikin lamarin ban ta ya canza mini gaba ɗaya.

Matakin farko yanzun kwata-kwata baya dawowa

gida da wuri. Sannan idan ya tashi da sauko yake fita, gashi yanzun abubuwa na dada samuwa bai fiye zaman garin ba, wannan ya sa ba shi da lokacina kwata-kwata, abincina idan na yi mutuka da shi 'yan lmomi sai ya ce ya koshi, ko baya jin dadin cikinsa dan ba ni dai ruwan shayi baki. Idan na yi kwalliya yaushe ya san ina yi, bai ma kalle ni ba barr ya san wata damuwata. Kin ga ko na tsiri lushi ma, kunnen uwar s go yake mini, ya nuna bai ma san Allah ya yi ni ba a gurin, barc bar ya gane ina fushi. In dare ya yi sai ya fara wasu sakin maganganu. Kai Sakina yau a gajiye nake, yau kaina ciwo yake mini, gobe ciwon kugu, gata ciwon jiki, dan debo mini *Panadol* na dan sha ko zan ji sa'ada. Ina mika mai ya kora, sai ya ja gefe kan ki ce komai sai ki ji shi yana sakin munshari uwa bajimin rago. Wannan matsalar na damuna, nayi-nayi ya tsaya mu fahimci juna ko da matsala sam ya kasa ba ni wannan damar. To wannan matsalar nake ciki sama da wata hudu, idan kin ga ya kulani sai radda ya yi ra'ayin kanshi, sai a shafe sama da sati uku, shi ma din irin yanda aka sabar mini da soyayyar shi sam ba ya yi. Caccakar kurciya kawai zai yi ya mike ni ko ko oho. Gaskiya Antie na gaji, ni din fa ba irin halittata kenan ba, ba kuma irin horan da aka mini kenan ba, don me za a ringa mini haka? Ko ko don takamar yanzun kudi sun zauna mai? Ba zan iya ba fa kin fara garin abubuwa na fashewa a jikina, ko ina tsoron nan gaba idan zan iya jurewa zan sanar da manya gara su shigo ciki duka auran shekara nawa ne? Amma har ana samun wannan, idan kawai ni din ya gaji da ni ba sai ya auro wata ba tun da giyar kudi na diban shi."

Anty Hauwa kanta ya yi girma da yawa, ba ta zaci matsalar za ta iya yin zurfi irin haka ba. Ta tausayawa

Sakina sosai, don ita ma macece, yaushe za ta juri yin hakan? Amma tun da yake ita babba ce, ba hakan za ta yi ba. Ta ɗauraye hannunta daga fulawar ta ce, "Anya Sakina ba ki fahimci mijinki hidindimu da sabgogi ne su kai masa yawa ba, suke sa shi irin hakan? Ki lura da da da yanzun fa duk ba ɗaya ba ne, a da harka ɗaya yake yi. da ya dawo daga *office* gidanshi kawai zai nufo, abubuwa ba su mashi yawa ba, ke ɗin ce kawai a gabanshi bayan aikinsa. Amma yanzun fa, ya sawa kan shi hidindimu da yawa. Ina ganin wannan ƙila shi ne jigon matsalar, kamata ya yi a dai samu zama a warware."

Ta taɓe baki, "Wacce irin matsala ce wannan da sabga? A kan shi aka fara neman kuɗi da aiki. har ya hana mutum kula da harkar iyalinshi? Na gaya miki yanzun ina jin yafi sama da kwanan wata 'yar cikin nashi kò ɗaukanta bai yi ba. To yaushe ya ganta? Idan ya dawo ta yi barci, in zai fita ba ta farka ba. Wannan wacce irin rayuwa ce? Ni kin ga kawai na gaji."

Ta daɗa kafaɗarta ta ce, "Kin ga Sakina ki yi shiru ɗin ki, rayuwar yau duk wacce kika ganta zaune a gidan mijinta fa kawai ƙyaleta dole ba za ta samu yanda take so ba ɗari-bisa-ɗari (100%). Sai dai kawai wata tafi wata matsala, wata tafi wata kwanciyar hankali, amma rokona gare ki don Allah haƙurin nan ki ƙara kar ki bari wani daga *side* ɗin ki ya ji wannan matsalar. Ki cigaba da addu'a nima zan taya ki, insha Allahu koma me ye za ki ga hasken abun albarkar Annabi (S.A.W.), kuma in za ki tafi zan haɗa miki wasu 'yan magunguna namu na mata ki gwada ki gani, insha Allah za mu fahimci inda ya dosa, ke kuma kar fushin ya rufe ki ki ƙi hilatarshi bare ki gane ko maganinki ya yi aiki, ko bai yi ba."

Wani irin kallo ta yi mata. A ranta tana kokonto anya ko wannan mata ta fahimci abubuwan da ta faɗa mata Barista na yi mata? Ita kanta ta fahimci abun da take nufi, ta bubbuga kafaɗa.

'Na ganc, haƙuri kawai za ki yi, ba ki ji an ce duk wanda aka bawa haƙuri an cuce shi ba ne?" Ita dai kallonta kawai take yi, ta ce, "Kin ga kin ringa ƙoƙarin sauraran rediyon Kano, akwai wani *programme* da Lami Sumaiya Murtala take gabatarwa akan ire-iren matsalolins da mata kan fuskanta a gidan aurensu. Sai kina jin *programme* ɗin za ki raina matsalarki, ko kuma ke ɗin ki ƙara godewa Allah da bai jarrabe ki da taikaicin rayuwa irin wannan ba."

Duk wani lallami da bam baki, Antie Hauwa ta yi mata, don haka *temper (fushi)* ɗin da take kai ta ragu sosai, sai tsananin tausayin kanta ta burin jan ɗamar wurin gyara rayuwar auranta. Don haka da sanyin zuciya kwarai ta koma gidanta, ta yi mai abinci mai daɗi, kus-kus, da miyar kayan lambu ta daɗa gyara gidanta don dama tsaf take, duk wata gaɓa, kusfa-kusfa an sa mata turare. Karƙashin hammata *rool on,* ƙasan mama, tsakiyar sa, cibiya, tsakiyar cinyoyi, gaɓoɓin hannu, bayan kunne duk ta sa Humra fara da baƙa gaba ɗaya ta feshe jikinta da *body spray,* sannan kayanta har Undis duk ta feshe su, ɗakinta da ko'ina na ƙamshin *room freshner* da turaren wuta. Komai acan-acan. Mijin kawai take jira, can gidan 'ya'yan ma an gyare shi tas.

A ranar ta sauke girman sai tai mishi *flashing.* Ya ga 3 *missed call,* sai ya biyo ya ce, "Ya ya ne?" Ta lallausar da murya ta ce, "Kana ina ne wai? Gani a kwance kai kawai nake jira." Tana jin dariyarshi.

"Ko? Me to za ki ba ni?"

"Komai ma in kana so."

"Shi kenan gani nan zuwa." Ta ajiye wayar cikin nishaɗi ta jawo carbinta tana jan Ya-ahadu, Ya Samadu, Ya wadudu.

An yi sa'a ya ko dawo ɗin nan, har ya yo mata tsarabar *fresh milk* da tsire mai daɗi. To shi mutum ne mai son tsire ya ci shi da tumatir da albasar, da su suke yankawa. To ita kuma ba ta son cin albasa musamman da dare. Don haka ta kawo mishi abinci ta shimfiɗa musu tabarma a tsakar capet ɗin. Suna hira kaɗan-kaɗan suna cin abincin suna kuma kallo, sai ta tsince gaba ɗayan albasar ta zuba a marufi, ta kalle shi tsakar ido ta ce, "Don Allah yau a hakura da cin albasar nan." Ya yi gajeran murmushi, ya kuma amince da abun da ta ce ɗin bai ci ba. Sakina ta samu kanta a wani yanayi mai daɗi cike da nishaɗi,, har zuwa lokacin kwanciyar barci ta yi wa ɗanta shimfiɗa ta shirya shi ya yi barci. Ta yo wata fitinanniyar shiga, rigar jikinta ya kwai ya babu, duk motsin da ta yi sai ƙamshi ne ke fita, ta yo *brush* ta fesa *mouth fresh* ta tafi ɗakin mijinta don neman yardarsa.

Ta tura ɗakin da sallama, ya amsa lokacin yana ƙoƙarin saita wani aggo da ke gefen gadonshi, ta tafi a hankali ta kwanta kan bayanshi, ƙamshin jikinta ya ratsa ƙofifin hancinsa, har ya gama saita agogon tana bayanshi kwance tana kallon mai yake yi, har ma ya gama sun ɗan yi jim, sai kuma ya ɗan zame ta ya ce, "Bari na shiga banɗaki." Ta matsa gefe, sai kuma ta kwanta a kan gadon. Ya ɗan jima,. sannan ya fito daga banɗaki. Ya haura gadon a hankali shi ma yana ƙamshin sabulun wanka, da *roll on*. ya kashe fitula ɗakin ya yi duhu. sai sanyin gari da ƙamshinsu yake ratsawa. Sakina kuma ta ɗan ja aji tun da ta nuna maitarta a fili yanzun kuma sauran aiki na Oga

Muttaƙa.

Sun ɓata shiru zuwa wani 'yan daƙcku cai sai ya miƙo hannu a hankali ya ratsata ya matso gun kunnuwanta cikin nutsuwa ya furta, "Na fahimci manufarki, amma don Allah ki yi haƙuri, ina jin jikina kamar mai zazzaɓi sanyi nake ji, kuma ba na son na rasa sallar Asubahi kin san wannan abun na hana mutum samun sallah a kan kari."
Wani irin rudani ya shigeta. Eyc Barista? Me yake nufi, ita zai rainawa wayo? Waniirin duhu ya ratsata mai tsanani. Ta ɓata minti wurin biyu tana shiru ba ta iya tanka komai ba, ya daɗa ƙoƙarin lallaɓata, ta make hannunshi ta miƙe da sauri, ta fita ta banko mishi ƙofarshi ta yi ɗakinta.

Ya Ilahi! Da gudu ta faɗa gadunta ta rusa wani irin kuka na sarewa da nadama, ta gama gano Barista akwai wata manufa gare shi a kanta. Ba ta iya haƙurin wannan cin kashin, gara kawai ta sama mishi lafiya ƙila dai ya gama nata yayin ne wata ce yake hangowa yake mata wannan cin kashin. Ranar ta yi kuka mai yawa iyaka dai ta kai, sai dosowar Asubahi ta samu barci, wanda har ta so ta ɗan makara, bugunshi ne ya farkar da ita, shida da kwata. Ta ja tsaki ta shige banɗaki tai yo alwala tana sallah tana jin nacin bugun shi, ba ta taɓa tsanar shi ba sai a wannan ranar burinta kawai a yau komai rintsi ta san inda dare ya yi mata. Ya gama nacin bugunshi ko alamar ta ma san da zamanshi ba ta yi ba, har Musaddic ya tashi, saboda buge-bugen'nashi, ta ɗauke shi ta yi masa wanka. Tana jin yaron na rigimar yunwa yake ji, ta yi burus ta ringa lallaɓa shi, ta ɗauko zani ta goya shi, wai don ya samu ya yi barci. Ai ko ya yi luf bai dai yi barcin ba. Da ya ga ta ƙi magana barc ta buɗe sai ya komawa waya ta yi *ringing* biyu da ta duba ta ga shi ne sai ta kashe wayar, gaba ɗaya tana jin shi ya gama

sukurniyarshi ya ficc daga gidan gaba ɗaya. Sannan ta samu ta fito ta dafawa Mussadiƙ indomic da ƙwai sai da ya ƙoshi, sannan ta yo wanka ko'ina ba ta tsaya wani gyarawa ba ta hadawa Mussadiƙ kaya kala hudu da 'yan abubuwan da zai bukata, ta ɗau nata kala ɗaya ta saka a jakar jcgonta. Ta kullc gida gaba ɗdaya ta ficc.

A hanya nc ta ringa tunanin inda za ta, gidansu ko gun Hajiyar Barista? Duk yanda ta kai da ɓacin rai, ƙokari take yi kada matsalar gidansu ta zaga gari kowa ya gane sirrinta, bayan jama'a 'yan'uwa da abokan arziki na sha'awar zamanta a rayuwarta ta aure, har jama'a na addu'ar Allah ya samu a danshin ki. Wane danshi? Jama'a na kuskure, idan sun ga mutum inuwa ta rufe kansa, ai ta fadi kai wanc ya dace, bayan ba su san tsananin matakan wahalar da ya ringa takawa kafin ya zo wannan mataki ba, kuma ƙila ƙaton kitse suke wa rogo, ba su san tsinin da mutum yake kai ba. Kila ma kai da kake shanawa kafi shi kwanciyar hankali.

Ranta ya gama amincewa ta je gidan Hajiya ko banza dai Hajiya uwarshi cc, kuma mutuniyar kirki ce, kuma tana da babbar rawar takawa wurin, wurin hana shi da sa shi, su ko iyayenta fa nasiha ce da ɗan lallami, amma in Hajiya ce alo tsiya, alo danja dole dai ya rusuna ya kuma bayyana abun da ya kawo gagarumin canji irin wannan.

Hajiya na alwalar sallar Walaha ta ji sallamarta, ta tsaya da alwalar tana kallonta da amsa sallamarta. Kallo ɗaya ta yi mata ta fahimci ran Sakina ba daɗi, dole ma ta yarda jiya-jiya ta bar gidan nan, sun rabu sai bayan kwana biyu. ga wannan sammakon. Ta wuce ta aje Musaddƙi da jakar kayanshi ta zauna zaman jiran Hajiya. Hajiya ta shigo kallo ɗaya ta yi mata ta ɗaukc kai ta koma *kitchen* ta kawo mata waina da miya da ta sawo a makota za ta ci idan ta

gama sallarta.

Ta ce, "Ci waina Sakina bari na yi sallah, sai mu gaisa sosai." Ba ta ƙi ba tun da ba 'yar haka tsakaninsu. Hajiya ta tada sallarta ita kuma ta sauka daga kujerar ta sahre duk wainar ta yi hamdala, Da ta shiga *kitchen* ta ga yawancin kwanukan Hajiya ba a wanke ba, ta haɗa su ta wanke tas. Ta share mata falo har ta ringa mamakin mai ya fitar da Maryam da safe irin hakan, bayan yanzun ba karatu suke ba. Tana wannan saƙe-saƙen Hajiya ta shafa ta ce, "Ina lafiya Sakina, ya kuka je gidan?"

"Lafiya lau, Hajiya ya Maryam fa lafiya?"

"Ta je asibiti, *Ulcer* ta ce ta tashi, tun jiya cikinta ke murɗa mata, shi ne ta yi sammako ta tafi Amini Kano."

Ta gyaɗa kai, sun ɗan yi shiru suna ta kallon Musaddiƙ yana shirmansa, ya ji ana kiɗa a rediyo yake taka rawa, suna mishi dariya. Can sun ɗan nutsu har shi ɗin ya koma barcinsa, tun da gwanin barci ne.

Hajiya ta rage rediyon ta kalli Sakina ita kuma sai ta sadda kai ta ce, 'Ina ga Sakina akwai abubuwan da suke faruwa, ƙila kin gaji da ɓoye su, ni ɗin ai kamar mahaifiyarki na ke tun da ni mahaifiyar mijinki ce, mun riga mun zama ɗaya da ke, ki saki jikinki ki gaya mini duk damuwarki insha Allahu zan yi iya iyawata na ga na kawo sauyi a kan matsalolin." Ta yi shiru sai sharɓe hawaye take takaici ya hana ta furta komai. Hajiya sai kallonta kawai take yi, tana nazarin abubuwa da dama tun kwanaki ta fuskanci kamar akwai abubuwan da ke damunta, to sai ta yi zaton ko ciki gareta. Suna a haka Antie Hauwa ta yi sallama ta shigo, Hajiyar ce kawai ta amsa, Sakina dai ta sahre hawayenta ta shiga nutsuwarta. Kallansu kawai ta yi ta gane lallai an ɓallo ruwa ajiya ba a kwashe da daɗi ba.

Ta zauna a sanyaye ta gaida Hajiya ta ce, "Ina za ku haka?"

"Dambatta za mu duk za mu je bikin sunan Wasila ta haihu."

'Ah! Allah ya raya mc aka [illegible], amma [illegible] kyauta ba baki ko gaya mini an haihun?"

"Ki yi hakuri Hajiya gani na yi hidimar da yawa ga shi nan da karshen watan nan za a shiga bikin Amina, zirga-zirgar sai ta yi yawa."

"To shi kenan Allah ya amfana bari na shiga na samo mata ko ɗan sabulu ne." Ta mike ta shige ciki. Ta kalli Sakina ta ce, "Wai ya ne Sakina, har yau dai matsalar ce, ina ce an samu daidaito jiya?" Ta ɗago ido da sauri takaici ya turnuketa ta kasa furta komai, sai hawaye. Ta tsaya galala tana kallonta a ranta da tunanin dole dai sai manya fa sun shiga cikin maganar. Har Hajiya ta fito ba su sani ba, ganin ta tu ta zo ɗaya daga mijin h ar matar da Antie Hauwa ta ce mata, "Yauwa Hauwa ga dai kanninki nan suna da matsala a gidansu, kila ke ta yi miki bayani, ni sai kuka take mini ina tambayarta." Ta kalli Hajiya.

'Eh na san da matsalolin jiya mun yi maganar, amma dai na ba ta hakuri gwargwadon hali, kuma a jiyan ta sauka kwarai ta amince da duk shawarwarin da na bata, ban kuma san me ya kuma faruwa ba a jiya. Hajiya matsalar babba ce dole sai ku ɗin kun yi zama da su gaba ɗaya a gano inda barakar take, tun da ta ce ita ya kasa ba ta damar da za su warware matsalar."

Hajiya ta gyaɗa kai na nuna gamsuwa ta ce, "Shi kenan ki yi wa mijinki waya ina nemanshi, ke kuma ki yi hakuri ki kwantar da hankalinki insha Allahu komai zai daidaita."

Ta mi*ƙ*a mata turmin atamfa *Heart target* ta ce, "Ki bawa maijego." Ta ri*ƙ*e ha*ɓ*a.

"Haba Hajiya ba ki fa san zancen ba?" Ta yi mata wani irin kallo, sai ta yi saurin mi*ƙ*a hannaye biyu ta ran*ƙ*wafa tana godiya. Ta yi sallama da Hajiya ta fito, sai Sakina ta yo mata rakiya su kai sallama a zauren *ƙ*arshe, ta ce, "Ki dafa ha*ƙ*uri Sakina, gara kawai manya su shiga ciki, ai maganin matsalar tun da kun kasa fahimtar juna, amma kuma kin burgeni da ba ki yi saurin kai maganar gidanku ba, bare har manya su sani irin wannan yana rage *ƙ*imar maigidan." Ta ja tsaki tana huci ta ce, "Jiya da kinga irin *ƙ*asar wula*ƙ*ancin da Muttaka ya bule ni da ita da kin tausaya mini, ashe haka namiji yake?" Ta gyaɗa.

"Kai lallai na yarda namiji dai ɗan kunama ne, *ƙ*udan zuma, tuwan *ƙ*aya, miyar allura, na ta*ɓ*a zaton Ogana zai mini cin kashin da yake? Kila wata can daban ya gano yake mini wannan kora da halin, to in ba kora da hali ba me ye ne wanna? Idonshi ya gano mishi wacce ta fini *ƙ*ima, kin sani ni ɗin bashi ni aka yi yanzun kuma ya ga wacce yake so dole na gane ni ɗin daban ce a gurinsa." Ta girgiza kai.

"Um-um Sakina kar ki yi saurin cewa haka, *ƙ*ila dai wata matsalarce daban, to inda wacce ya kamata ya baiwa fifikon *ƙ*ima ai sama da ke yake, don ya sani cewa an bashi ke ne ba wai don kin yi kwantai kin rasa wanda zai ɗauke ki ba, a'a ko *ƙ*ima wata na*ƙ*asa ce da ba a so a san kina da ita a ka li*ƙ*a mai, ko ɗaya, ko za*ɓ*o mata ya yi kina ganin zai kawo sama da ke ne? Gaki mai ilimi, kin yi *Graduating*, kin haddace Alkur'ani mai girma, gaki da kyan ki, to me kika rasa? Ta ɓangaren ɗabi'u da halaiya me aka fi ki? Ai wallahi a wannan zamani ba kowa ne yake da wannan

darajojin ba, gaki ɗaga gidan dattako, gidan da kowane siriki zai alfahari da surukutarshi, to da me aka fi mu?" Ta ja tsaki.

"Ki share kawai sharrin namiji ne idan ya motsa sai ya ɗana miki, ki yi haƙuri rayuwa mai wuce wace wata rana da kuɗi ba zai miki haka ba, kuma shi zai dawo a hannu yana binbini da ban baki, zuba ido ki sha kallo, haƙurin ne dai mai wahala, amma daɗi ai mai ɗorewa ne."

Ta yi ɗan *smilling*. "Na gode Antie Hauwa, ki je na tsayar da ke da magana yara na jiranki sai ƙin dawo." Su kai sallama ta tafi.

Ta shigo cikin gida Hajiya ta fara ƙoƙarin ɗora tukunya, ta tayata su kai girkinsu na rana. Har Maryam ta dawo ta same ta ta ce,, "Matar yayan kwana biyu kina ji da mu, sai ƙaunarmu kike." Murmushi kawai ta yi ba ta ce komai ba.

Hajiya ba ta kira Barista ba, haka shi ma bai nemi Sakina ba, bai kuma dawo da wuri ba sai misalin goma da kwata ana shirin Taskar Labarai. Ya yi matuƙar mamaki da ya ga ƙofar gidan a rufe. Abin da yake faruwa ya faɗo mishi a cikin rai tabbas dai Sakina ta yi fushin da ba ta taɓa irinsa ba. Jikinshi ya yi sanyi, haka dai ya buɗe gidan ya shiga.

Ƙomai na nan kamar jiya, kwanuka da duk abincin da ya rage sunan. ya yi wani irin *cooling* da shi, ya duba agogo sha ɗaya har ta kusa ina zai kuma dosa? Dare *already* ya riga ya yi, haka ya ringa komai ba da kuzari ba, har ya kwanta. Sannan ya lalubo wayarta a kashe take. Ya yi jim yana ta tunani, har barci ya kwashe shi. Kasancewar ranar *week-end* ne, bai tashi da wuri ba, sai goma. A gurguje ya yi wanka ya shirya, ko ɗan *tea* bai tsaya sha ba,

Bayan ya fito daga layin gidansu sai tunani ya kama shi, yanzun gidan na su Sakinan zai nufa Gwauran Dutse? Wata irin kunya ta ratsa shi, ya ringa jin abin da ya yin bai kyauta ba. To ita don mene ne daga ɗan abu za ta kwashi ƙafa ta yi gida, ita ba za ta iya haƙuri irin na sauran mata ba, sai ta yi wani yaji? Tsiyar matar malam Bahaushe kenan ba ta iya rayuwar zaman aure ba. (Kun ji ni da Barista ido ya rufe yana cin uban matan Hausawa, ko ko shi haka aka ce namijin Bahaushe ya ringa yi wa mace? Kamr ya san darajar 'ya mace, ce nake ita da hajja duk ɗaya ne? Makaranta na barku da ƙalubale).

Ya ringa tafiya a *slow* saboda duk gwiwarshi ta sare kunya ce duk ta dame shi, yana jin nauyin dattawan iyayenta, masu mutunci. Sai wata zuciyar ta ce, "Kila ma tana gun Hajiyarka, ka san Sakina da Hajiya fa sai Allah." Lamarinsu na burge shi. Wannan zuciyar tafi bashi kuzari da ɗan farin ciki, duk da ya san zai yabawa aya zaƙi, hajiya fa ba sauƙi ba ce, in ta kama faɗa ba ta jin Allah jisshe mu. Shi ya sama ƙila tafi zaɓar kai ƙarar shi can, don ta san can ne za a sulle shi tas. Duk da ya san hakan shi dai in can ta je zai fi mishi daɗi, kan gidansu yana jin nauyin iyayen nata kwarai, amma uwa ai uwa ce, koya ta kai da faɗa nata ne shi.

Yana wannan tunanin har ya isa ƙofar Nassarawa gidan Hajiya, ya ɗan daɗe ma a waje suna gaisawa da mutanen unguwarsu, tun da yanzun aure ya ɗauke shi ya maida shi Sharaɗa.

Sakina na tsakar gida tana ma Musaddik wanka, sai ta ji tafiyar takalmi kyam-kyam da nutsuwa zuciya ta ringa bugawa kaɗan-kaɗan ta rava a ranta ƙila mijinta ne tafiyar ta yi kama da takunsa. Ilai kuwa ya watso sallamar shi,

kallo ɗaya ta yi masa ta cigaba da abin da take yi ba tare da ta amsa mishi sallamar ba a fili, amma a zuciyarta ta amsa. Ya ɗan tsaya kaɗan a kanta ya ce, "Ku ba ku amsa sallama ne?" Ta yi masa banza ta ƙarasa watsawa Mussadiƙ ruwa ta wurga shi a baya ta ɗaure, ta ɗau tsintsiya ta fara sharce gurin. ya yi saurin matsawa, saboda kar ta fallatsa mai ya wuce ciki. Maryam ta fito daga *kitchen* a sanyaye ta gaishe shi. ta sa kai a rumfa ba ta zauna ba ma sai ta wuce can uwar ɗakin Hajiya.

Ya yi sallama Hajiya ta ɗaga kai ta kalle shi ta amsa mishi ba wata cikakkiyar fara'a. tun daga nan ya fara sarewa. Ya tuɓe takalmansa ya shige ciki ya zauna daf da ita ya ramƙwafa yana gaisheta tana amsawa kamar ba ta so. Sai kuma su kai shiru ita ba ta ce ba, shi kuma ya yi wuƙi-wuƙi. Sai ga Sakina ta shigo rumfar ta wuce su ta yi ɗakin Hajiya don ta shirya yaronta. ya bisu da kallo ganin wani mugun shariya da ta yi masa. Ashe Hajiya ita kuma shi take kallo, yana juyowa sai suka haɗa ido ya sauke idonshi a hankali ya yi ajiyar zuciya. sai ya ɗan muskuta ya ce, "Hajiya ashe su Sakina suna gurinku?" Ta haɗe rai.

"Eh, wani abu?" Sai kuma ya yi ɗan jim na rashin makama. Hajiya ta kwalawa Maryam kira ta ce ta kira mata Isma'il mijin Hauwa da Musa wansu a waya ta ce yanzun tana nemansu. Tun daga haka ba ta kuma tankawa ba. sai ma ta miƙe ta shiga banɗaki ta yo alwalarta ta sallar Walaha tai kamar Barista baya gurin. Duk sai ya yi ƙiri-ƙiri. Sai kuma ga Musaddiƙ nan ya fito yana takawarshi yana tasa gwaranci nsa, an shirya shi da kaya mai kyau, sai ƙamshin sabulun wanka da hoda yake yi. To shi ne ya ɗebe mishi kewar zugum ɗin shi.

Ba a ɗau wani lokaci ba, duk yayyan nasa suka zo,

kasancewar bantsı, gashi kuma *week end,* suka zauna aka gaida Hajiya. Sannan suka gaisa da Barista. Hajiya ta cire hijabinta na salla ta ce, "To Isma'ila da Musa na aika a kira ku ne, ku zama shaida a kuma yi komai a gaban idon ku, don ba na son a kuma maimaita kwatankwacin hakan, don duk ku ɗin nan ba irin horo da tarbiyar da muka ba ku ba ne, a'a kowannanku zaune yake lafiya shi da iyalansa da dadi, ba dadi ba a jin kan ku. To girma ya kama ni kwarai. Alhamdulllahi Allah ya azurta ni da rayuwa mai inganci da cikakken rufin asiri da kwanciyar hankali, to haka nan zikau ina cikin nutsuwata ba na maraba da tashin hankali, bare wani ya zo ya dame ni. Ga dai Muttaƙa nan so yake yi ya koyi halin tur, ya kasa zaunawa da matarshi kwaya ɗaya jalin-jal da ɗa ɗaya lafiya lau. Ban haifi wannan ɗan ba, don haka na kira ku, ku ku zama shaida, ya yi koƙari ya zauna da matarshi lafiya lau. Kowa da ya gani hakan nan yake zaune cikin alfarmar Allah, ko mu da kuke gani mun haife ku sai da muka ringa taka siraɗai kala-kala kafin mu cimma burinmu har mu ringa ganinku sanyin ido, don haka rayuwa gaba ɗayanta haƙuri, in mutum na so ya cimma rabo. Dare ga mai rabo sa'a ce. Matarshi ta zo min jiya wujiga-wujiga na yi tambayar duniya ba ta ce mini komai ba. Hauwa dai ta shaida mini ta san matsalar kuma a ganinta sai mu mun shiga ciki mun tsawatar, to ga mu a cikin dumu-dumu, ina so na san me ye yake haddasa saɓani a cikin auran na ku."

Barista ya yi wuƙi-wuƙi, sai wani muzurar yake yi, kamar ba zai magana ba. Alh. Musa ya ɗaga murya ya ce, "Magana ake maka sai wani kallon mu kake yi daɗdai" Hauwa ta sa baki ta kira Sakina wacce take rakuba a elen gacon Hajiyan tun da ko me ake faɗa suna ji. Ta fito a

hankali ta zaune nesa da su. Alh. Musa ya kalle ta ya ce, "Ke mene ne yake hada ki da mijinki kika kasa zama lafiya da shi?" Ta yi shiru ya maimaita tambayar har sau uku ba ta bashi amsa ba, sai ya juya ya kalli Barista yana mishi gargadi da ido saboda dai Alh. Musa mutum ne mai kwarjini kuma baya son wasa. Ya ce, "To ni dai Alhaji yarinyar nan dai ban san abin da na yi mata ba, kawai dai kullum sai ta ringa wani daddaurewa tana sha mini kunu, kuma ni a ɓangarena gaskiya ba abin da ta yi mini sai dai kawai na san na yi mata fada ta ringa yin *brush* idan za ta kwanta, kuma ta ringa gyara mini shimfidata, ina jin dai wannan maganar da na yi mata ne ta kama fushi, jiya bayan na fita aiki ta taho gidan Hajiya, kuma ni ban dawo gida da wuri ba jiyan, da na zo mun tafi tun jiyan ina ta kiran wayarta kuma a kashe ban san a wane yanayi take ba."

Sakina gaba daya ji ta yi kamar duniya ce ta rikito mata, jin irin wannan gundumemen sharrin wulƙanci da Barista ya yi mata a gaban mutanen da take tsananin jin kunya, yayyan miji ne fa da suruka ba su ne kunyar taka ba? Wai ba ta yin *brush* ba ta gyara shimfida, me ba ta gyara shimfida ke nufi hakan fa na da ma'anoni daban-daban.

Tun da ta doƙar da kanta, ai ko motsi ta kasa yi, saboda tsananin takaici da kunya, su kan su alƙalai dai dif su kai don zancen da ya fada wani ɓangare ne da kamar ya shafi ma'aurata, amma da yake hajiya ta dace, sai kawai ta ƙara hade rai ta ce, "Ka ga Muttaƙa ba wasa nan muka tara ku ba, ba na nufin jin wasan don haka wannan magana da ka fada ƙanzan korege ce, yaushe za a ce kamar Sakina har sai kai mata fada ta gyara wani abu da ya danganci tsafta? Mai son jiki ma ai daban yake, yarinyar nan ban taɓa ganin

wata illa ba dangane da ita. Koda yaushe tsafi ɗinta. kuma idan ta iso gidan nan gyara wannan, kauda wancan yau ɗin nan tun da ta tashi gyaran gidan nan take yi, dubi ɗanta tsaf da shi, sai ƙamshi yake yi shi ne za ka mata sharri? To wannan bai karɓu ba ka canza wani, wallahi tallahi na gama magana rana ta ƙarshe ko me ye ku kashe ku rufe, kar a kuma kawo mini matsalarka, ko ka kai wani guri kowa ka gani da iyalinsa da daɗi, babu haka yake zaune ka shiga taitayinka, idan ma 'yan kuɗin da ka ga ka fara kamawa ne za ka fara canza salo tun wuri ka canza, wallahi ban ma baki ba, babu wata mace da za ka samu a duniya sama da Sakina, ko 'yar wacece don haka ka shiga taitayinka. Na gama magana, ka kuma ji tsoron Allah wannan yarinyar amanarka ce, Allah ne ya baka ita ya kuma ɗanƙata gareka, don haka ka lura da kyau, ka riƙe amanarta, kar kai wa Allah butulci."

Tun daga nan ba ta kuma cewa komai ba, sai ta matsa ta jingina da kujera, tana kallonsu. Alh. Isma'il ya ce, "Ko ni ɗin nan na san haka ƙarya kawai yake yi, ya nemi kalmomi ne kawai na kare kai abun da ya faɗa ya nuna zahiri shi ne yake cusguna mata har haƙurinta ya ƙare. Sakina Alh. ya yi miki albarka mai yawa, ki yi haƙuri da mijinki insha Allahu komai ke da akwai zai daidaita tashi ki je, idan mijinki ya buƙaci ku tafi ki bishi ki manta da komai ki yi ta gayawa Allah kukanki ba wani taƙadari da ya gagari Allah. Ki je kin ji ki yi haƙuri." Cewar Alh. Musa. Ta miƙe cikin ruɗani jikinta sai wani karkarwa yake yi, ta faɗa ɗakin Hajiya. Su kuma suka bawa Ila ya haƙuri, suka ce za su shiga ɓangaren Alhajinsu za su tattauna wasu batutuwa. Suka miƙe suka kama tusa Barista gaba har gurin suka mashi tas, suka farke faya a kan abin da yake faruwa. Suka nuna mishi kuskurensa da fatan ya gyara

mutuƙar yana son inganin aurensa. Don mace fa zuma ce sai an cita da yaƙi, ko kuma mace kamar mota ce sai ka zuba mai, kai mata *service*, sannan za ka ji daɗin aiki da ita.

Ya yi alƙawarin in Allah ya yarda komai ya wuce, zai gyara dukkan wasu ɓarakoki. Sannan su kai sallama suka tafi.

Ita kuma Sakina tana shiga ɗakin Hajiya da gudu ta faɗa gado, kuka ta ringa yi ita tozarta tan da ya yi ya fi abun da yake mata ciwo. Maryam ta ce, "Haba Antie Sakina sai ka ce ƙarshen rayuwa? Ki yi haƙuri mana." Ta ɗaga jajayen idonta ta ce, "Meri kin ji irin ƙagen da Barista ya yi mini. wai daman a ajujuwan namiji ki ce har yanzun ban zo *primary* ba?"

"Kinga *relax your mind* Sakina, namiji ne fa sharrinsa yawa garai, su kansu sun sani, shi ai dama idan ya rasa abin cewa komai ya rarumo ƙiƙa ma zai yi, to me ye wane ne zai yarda wai ba ki yin *brush*, abun dariya Allah sharri ne *forget*." Sukai dariya. Hajiya da jinse, ta yi murmushi.

Barista Muttaƙa ya yi sallama ya shigo rumfar Hajiya ta ɗaga kai tana kallon shi a ranta yanda take mamakin budewar shi, sai wani ƙatoto yake zama, ya zama *big* Alh. lallai kuɗi na karfarsa sai dai ƙawai tsiyar da ya tsira kenan, matsalar malam Bahaushe kenan, da fa ya fara samun nutsuwa sai ya fara sakin iska, idan ke ɗin bai wulaƙanta ki ba, to *defenetely* zai ƙawo 'yar tayin ɗin naira, don a lokacin ya gane ke ɗin kin yi masa kaɗan baki gamssarshi sai ya nemi ƙari. In ba haka ba kuma ya shiga bin dare. Allah ya kyauta. Ta amsa sallamarshi bayan har ya zauna, a ranshi yana tunanin ko me take tunawa? Ya yi ɗan jugum ya ce, "Ko kun rage abin karyawa Hajiya ko kari ban ba."

"Babu." Ya miƙe. -

"Bari to na je na samu abun karyawa, ki ce n ata ta shirya kafin na dawo." Cikanka ba ta ce mishi ba, har ya yi

waje. Ya samu akalla awa biyu, sannan ya dawo. har lokacin Sakinan na ɗaki barci ne ma ya ɗauke su ita da Musaddik har Maryam ɗin.

Ya ce, "Hajiya ta shirya ɗin mu tafi?" Ta gi giza kai.

'A'a ba yau ba sai ta gama hucewa." Ya rike baki.

"Haba dai hajiya ai ta barin gidan haka ba kowa kenan, ai ba zai dadi ba."

"Idan ka gaji sai ka kawo wacce take yin *brush* sosai sai ku yi zamanku, ita kuma sai ta zauna a nan." Ya yi ɗan murmushi ya san tsakanin Hajiya da Sakina sai Allah, lamarinsu na bashi mamaki, kamar ba surukan juna ba, yanda yake ganin inda ake artabu tsakanin surukai (To dama yaushe za a zama ɗaya, akwai nagari cikin ɓatattu).

Ya ce. "Ki dai yi hakuri Hajiya, ai na zo biko ne."

"Na gama magana sai gobe da dai jiya ka biyo sawu ne dana baka ita, amma ka makara." Ya san ko ya yi magiya ɓata bakinsa zai yi tun da ta kafe, ya kuma san halin ta sarai. Ya mike a sanyaye ya yi mata sallama ya tafi. Koda ya tafi ragaita ya yi ta yi a gari da yamma daf da Magriba ya iko leda da kayan kwalam har biyu ɗaya ta Hajiya da ta su Sakinan. Ya kawo nan ne ya samu sun gama abincin dare waina da miyar gyada, ya samu ya ci. Ya bai wa kowa tashi ledar. Nan ya dada marairaicewa Hajiya ta ki ma kallonsai, bare ta saurare sa. Ya yi jugum, ya yi ɗan abin tausayi har ya ba ta tausayi, sai ta basar ta sani namiji ne fa? Da ya ga ba wani *hope* ɓangaren Hajiya, ba kunya ya sa baki ya kwalawa Sakina kira. Tana ji ta yi shiru. Hajiya kuma ba ta ce komai ba, ya yi kira har sau uku, sai da Maryam ta zunguretा ta ture Jannunta ta ce, "An gaya miki ni kurma ce ne Hajiya fa na ji." Ta yi ɗan murmushi jan ajin malam duniya. Su kai dariya, Hajiya ta ci gaba da jan carbinta, shi kuma ya yi kurus. Kawai ranshi sai ya ɓaci ya ga ta gidansu, ɗakinsa, matarshi,

Hajiyarshi waye bako Maryam ko Musaddik? Kawai sai ya murje ido ya yi dakin Hajiya. Maryam na ganin shi ta mike ta fito, ya yi tsaye kawai yana kallonta ya ce, "Ai da kina jina ki kai hanza da ni? Amma dai kin san ina da *right* din kiran ki ko yaushe ko?"

Hajiya ta sa baki, "Ya isa namiji me ya hana da kai wannan a gidanka fito ka ba mu wuri ka ji."

Ranshi ya yi ciwo haka nan ya fito ko sai da safe bai yi ba. Ashe da yana so? Da daddare za su kwanta ta y ta kara bawa Sakina baki ta ce, "Mazan yanzun n fa sai h kuri ba kamar irin namu mazajen ba, da akasarinsu suna daukar macece yarinya koda yaushe. Shi dama aure hakan yake kafin ku daidaice ku samu mukullin kulle barakoki, wani bin har sai yaranki sun taso sun girma, to tsinin idonsu ya sa a rinnga raga miki ko ke ki yi ta hakuri kina raga masa."

Ta amince da duk abin da Hajiya ta fada, ta yarda komai Hajiya ta sata za ta yi, don matar na sonta da gaskengasken abin da duk uwa tagari za ta yi wa 'yarta shi take mata, albarkacin Hajiya da Musaddik tana ta kara kaunar mijinta, zafin da ta yi sai ta sauko sosai. Don haka ranar ta yi barci mai dadi

Da safe misalin tara da rabi Barista ya shigo gidan ita ce da Maryam suna suyar kosai, shi su kai sha'awa da kunu. *Direct kitchen* din ya nufa, ya ce, *"Good morning Edcellency."* Har da rankwafawa yana jinjina hannu. Maryam ta yi dariya ta ce, "Yaya barka da kwana." Ya amsa da walwala, ita ko Sakina ko ta daga kai, sai saka kosanta take yi. Maryam ta aje matsamini tai yo waje, sai ya zauna kan kujerar da ta tashi ya matso da ita sosai suna gogar juna, ya dungure kanta.

"Nine kike sharewa haka ko Edcellency ce take duk laifin da na yi su yaya sun fanshe ni, albarkacinsu na ga

hasken ki, *pls* ki yi mini dariyarki man mai haske." Yana ƙoƙarin kallon idonta ta ɗauke kai, ya ringa zolayarta yana mata kalamai masu tsaurin gaske, har sai da ya sata dariya. To kan wani lokaci har sun daidaita mata da miji sai Allah. A nan *kitchen* ɗin ya ci ƙosansa mai zafi da kununshi. Suna 'yar hirarsu mai daɗi, Maryam ta ji shiru ta leƙo ta ce, "Iye Antie Sakina, muma taimaka ki ba mu mai ɗomin kada ya huce baki farga ba." Ta yi murmushi, shi kuma ya miƙe ya ce, 'Shigo daga cikin man Maryam zo zauna gurinki." A ranta ta ce, "Ka ce haka man tun da ka gama gyara cikin ka da zuciyar matarka." Ya yi rumfa gurin Hajiya. Suna gaisawa har su Maryam suka gama sabgarsu suka gyara gidan yana nan tun da Lahadi ce, da da ne har Lahadi yana *office* da gurin zuwa.

Sakina ta shige ɗaki, ya kalli Hajiya. "Muna iya tafiya yanzun?" Ta girgiza kai.

'A'a sai da dare." Ya yi murmushi.

"Na gode sai dare bari na wuce akwai gurin da za ni " Ya fita.

Komai ya yi daidai rayuwarsu ta dawo *normal,* kamar komai bai taɓa faruwa ba, har tana mamakin to wai ɗacin k[illegible]n na ma ye ne? Yanzun sai wani ƙara lallaɓata yake yi [illegible]a soyayyar shi mai daɗi. Da ta tuna mishi ƙagen da ya yi mata cewa ya yi, *"Forget,* neman kare kai ne, ba ki gani a gurin al[illegible]a ramfo ni, ni na isa na ce wannan *sweatable tongue* ɗin na wari?" Yana kallonta yana dariya.

To haka da[illegible] rayuwa mai daɗi, in ji 'yan magana [illegible]a cewa, "Zama lafiya yafi zama ɗan sarki. Zaman gidan aure [illegible] haƙuri.' Ba a dad[illegible] ba Allah ya hawa[illegible] Maryam mijin am[illegible] magidanci ne mai mata da yara [illegible]hida ɗan kasuwar Singa[illegible] aminee da shi ɗar[illegible] bisa-ɗari (10[illegible]%). Mai wayewa da ilin[illegible] suna son junansu don haka aka shi[illegible]a hidimar bikin ba da w[illegible]a ba. Daga dukkan [illegible]ayye[illegible]an bada [illegible]udummawa mai yawa, [illegible]

yarinya ta zama 'yar lele aka karɓo mata darajarta.

An yi shagali sosai ta tare a gidanta da ke unguwar Dorayi Babba *Oppiste* Rijiyar Zaki, gidansu sabo mai kyan gaske, kowa dai da *apartment* ɗinsa ta shige sukuf suna rayuwarsu mai daɗi da kishiyarta Hajara mutuniyar kirki.

A wannan ɗan tsakanin Allah ya kuma ba su rabo Sakina aka samu ciki, masha Allah kun santa da ɗan karen laulayi, ta shiga yi baji ba gani, har cikin ya kai wata huɗu, sai ta warke ta yi garau, komai ya yi *normal* sai wani shegen kyau da ta yi, jikinta ya ɗanyance ya yi luf-luf da shi. Shi kan shi Ogan kamar ya cinyeta.

Wata ranar Alhamis da hantsi bayan sun gama karya kumallo, yallaɓai na ƙoƙarin fita ta kalle shi ta ce, 'Oga zan je gida fa yau."

"Allah ya kiyaye a gaida su."

"Ogan ba mai fa a motata, kuma jakata *is zero.*" Ya harareta.

"Ke kin cika roke-roke." Ta yi ɗan sak, amma sai ta yi gajeran murmushi. Ta ce. "Kai ma dai ka faɗa, ai gara ka ringa mini gori ko na yi zuciya dai na karɓo *result* ɗina nima na nemi na kaina, maganin roƙo. Yauwa idan na fita zan wa Yaya Muji maganar." Ya sha kunu.

"Wai aiki a gidana da ke na rage ki?"

"Babu rashin ci da shi, sai dai babu kuɗin sabgar gaba, gara kawai mutum ya dogara da kan shi."

"Haka ne."

Har zai fita sai ta kuma cewa, "Yauwa Oga ina dada tunama kar ka manta yau dai ka shigo mana da kayan abinci, shinkafarmu da taliyarmu duk sun kare sai doya da kuskus kuwa ma ai sun kwana biyu. garin semo'fita ne kawai gare ni da ɗan dama." Ya ce, "Ke wai wace irin macece ne da baki so a zauna lafiya ne? Idan ba ki ce a kawo kaza-da-kaza ba ranki

ba zai miki dađi ba." Ta hađe rai, rainin hankalin kuma ya fara yawa. Ta ce, "Wani irin rashin son zaman lafiya? Daga na gaya maka abin da kai ne ka ke da hakkin siya tun da ba wani namijin gare ni ba bare idan kai ka ki na gaya mishi, sau nawa ina gaya ma kana sharewa, har yawancin abubuwa sun kare malcji kawai nake yi. 'yar shinkafar da ta rage mini cikin buhu ba na jin ta kai ko kwano đaya ta kai, jira kake sai na rasa wanda zan ci sai na gaya maka, bayan ka sani da đin ba haka kake yi ba, da kanka da kaga abu ya yi kasa za ka karo ba ka jiran wani ya kama hanyar karewa. Shinkafa buhu nawa kake ajewa, amma har ya kai jallin đayan ma nema yake ya gagaran."

Ya ce, 'Eh ai kin fađa da kan ki cewar da ba haka nake ba, kin kasa fahimta ne kila ko wata matsalar ce take hana ni hakan?" Ta ce, "Wacce matsala ce kuwa da za ta hana ka ba walinka abincin bayan ina zaune kake kirga dubban nairori, me kuma kake so na yi? Ni fa irin abubuwa da kake ta yi daga na toshe wannan ka 6ullo wancan na gaji, kamar ka har na kai matsayin cin lami to me ye amfanin samun ba za a wadata iyali ba?"

Ya yi wata dariya. "Ko kin shekara dubu kina fađin kina da yunwa a jiki ba mai yarda."

"Eh ni đin ma ba haka na ce ba, ina gaya ma ne, misali ya ci a ce kai đin kana gane akwai sauyin abubuwa da yawa a rayuwar aurenmu sai na kai ka gaba ka kaga mini sharri." Ya yi mata wani malalacin kallo ya ce, "Ko? To ki kai abun da ya fi gaba ma, ni baki gane ba kin fa zame mini kaya, daga bani sadaka sai kuma ki zo ki buwaye ni, ki je na sauwake miki igiya đaya, idan kin yi idda ki auri Đan Gote wanda zai kawo miki tirelar shinkafa acici."

Sakina ta hangame baki da wani irin tsananin mamaki da firgita mai yawa. An sake ta? Daga wannan 'yar maganar?

Maiturare, mata ƙalubalenmu mu sani duk daɗinki da namiji randa duk ya tashi kwance miki zani a kasuwa za ki sha mamaki, bai yiwuwa mu ɗauka a ranmu, mun yi aure ne na soyayya da ƙaunar juna, ita ce za mu cigaba da ci har ƙarshen rayuwa, tun da tun a soro, soyewa muke kamar mu hadiye junanmu. Ina ga an mallaka mana kan mu ai sai holewa. Aure ibaɗa ce, bauta ce, to duk ko mutumin da aka ce bawa ne shi, bauta kuma yake yi, to fa sai yanda Ubangijinsa ya yi da shi, don haka mu ɗauka a ranmu da mun shiga gidan aure ƙalubale ne za mu ringa fuskanta, wani bayan wani. Wannan shi zai hana mu shagala cikin tsanain so, yayin da matsala ta samu kuma mu gigice.

Sannan abu na biyu ga makaranta littattafanmu masu ɗaukar soyayyar littafi an so wancan, an ɗora ta a matsayi mai yawa, mijinta ya riritata, yana ta gaya mata kalmar soyayya da ta yi fushi zai ce wance *how far, am sorry,* ko kuwa ta littafi ta ci shinkafa wal kaza an ɗauketa daga maka zuwa Madina, London, Paris, India da sauransu. Ta hau *Humer Jeep,* ta hau Honda CRV, ko Brama, ko Hala, nima burina kenan, 'yar uwa farka, ban ce ba a samun irin haka ba, har ma fiye da haka, zaman aure fa ba haka yake ba, wahala ce da haƙuri a cikinsa don bauta muke yi. Ko matsalar ciki da goyo da raino ma kaɗai aka barka, babban ƙalubale ne, bare kuma wasu matsaloli na rayuwa ku dai Allah ya gyara mana. Nijeriya mai arzikin ƙasa, ƙasar da arziki da talauci suke gogayya kafaɗa da kafaɗa, kowa na ƙoƙarin ture kowa. To Ubangijinmu kai dubaiya ka gyara halinmu da halayyarmu ka arzurta mu da shugabanni masu kishin ƙasa ba masu kishin aljihunsu ba.

Talauci da ƙuncin da jama'a ake a ciki shi ne yake sanya ƙarancin samu da ƙarancin mallakar masarufin rayuwa, wanda ya sanyawa wasu mazan dole ba dan sun so ba abubuwan kan gaza musu, wanda ke hana su sauke nauyin

iyalinsu, inda za a samu nakasu, tare da bala'o'i da musibu. Macc da 'ya'ya kuma babu bata tsarinsu dole ka nema ka bawa macc, bayan ka zaga ka zago ba ka samu ba, ya za kai? To ɗan'uwa kar wannan ya kashe ma zuciya, kai ta fafutuka da mika al'amarin gurin Allah ko ba kai arzikin shahara ba, idan Allah ya yi maka arziki nema ka kawo a sakaya hanji ya yi maka babban arziki, don ka zama gwarzo jarumi wanda ka fita kunyar iyalinka. Allah kuma da manzonsa ke alfahari da kai. Don Manzo (S.A.W.) ya ce, "Mafi alhairinku shi ne wanda yake kyautatawa iyalansa, ni kuma na fiku alhairi don na fi ku kyautatawa nawa iyalin." Sadaka rasulil karim.

Jigonki afuwar matsalolinki, komawa ga Allah, tsarkake zuciya da cire mugun jafa'i da nifaka da kauracewa 'yan tsubbu, wallahi Allah ba zai tozarta ki ba, zai ta yi miki suttura ki sani hakuri shi ne jigon, don sai kin ɗana za ki ga samu, in kin gaza ki ci baya. Allah ka samu daga cikin masu godiya da hakuri, kai mana tsari da talauci da musibar rayuwa, ka shiryemu da mazajenmu, ka ba su ikon jan ragamarmu da ta 'ya'yanmu. Allah mun gode da tarin ni'i'mominka mayawaita. Amin.

Kun san guguwar da ta tumɓike auran Sakina da Muttaka? Shi kenan ko za su koma a gaba? Kila kuma ta yi karo da babban haske wanda zai wanke duhun zuciyarta. Mene ne ra'ayinku, Sakina Muttaka ko sabon kamu?

Afuwan ku dai taya ni da addu'a har kullum ku yi ta hakuri da ni, kullum *complain,* ajizancin kenan irin na ɗan adam na godewa Allah, na gode muku.

08024261568
08131508818
MAITURAREN KAMSHI
MRS YUSUF GARBA
UWAR SU

ABDUL-KADIR YUSUF
ABUBAKAR YUSUF
AUWAL YUSUF
AL-MUSTAPHA YUSUF

Allah ya rayanku da albarka, tare da 'ya'yan 'yan'uwa da jama'ar Musulmi. Amin.

KYAUTARWA

Ga Hajiya Lami Sumayya Murtala, Freedom Radio, da bazar tunaninki da kike ƙirƙiro *programs*, wanda ya shafi matsalar mata, na samu na rubuta haske magani duhu, Allah ya yi miki albarkar rayuwa. Amin.

JINJINA

Ga gwarzon mazaje, tsayuwarka kan iyalinka tana burgeni, wannan shi ya ɗaukaka uwata a gidanka malam Isa Kurna. Limamin Massalacin Kurna tare da Uwargidanka Faɗima (Ta manzo) tare da dukkan iyali, ina yabawa soyayyarku gare ni, duk domin Rahmatullah da Anti Murja (Mrs. Malam Ali) Allah ya barni da Zallah Naja'atu da Rumasa'u. Amin.

ALLAH YA YI MIKI RAHAMA BILKISU MUSTAPHA SA'AD

MRS. SALISU SHITU (MASHI) Duniyar makaranta ta yi rashinki, ta rasu a kan gwiwa bayan ta haife ɗanta lafiya lau. Allah ya jiƙanki, Amin Marubuciyar Sirrin Riƙe Miji, 'Yar Riƙo da Zikirin Safiya da Maraice.

UZURI

Don Allah za ku ga ba Kwai Tara ba ne, ina nan ina muku shiri ne, na saki na biyu da na uku a tare, abun zai fi bada sha'awa ko ya ya? Na san ƙila za ku ji ba daɗi afuwan 'yan'uwa, rayuwar ce sai da dabara.

Bissalam, sai mun haɗe a Kwai Taran ma fanshe.

JAKARA CITY
BOOKSHOP
07028826909

**Daga Marubuciyar:**

KHAIRIYYA 1-2
BIYAYYA 1-2
BABBAR MACE... 1-2-3
JARABIN RAYUWA 1-2
KWAI TARA...1

**Masu Fitowa:**

KWAI TARA...2

Tsarin Bango:
ANKA - GRAPHICS FAGGE
07030319787